Kasar Saudi Arebiya
Ma'aikatar Ilimi Mai Zurfi
Jami'ar Musulunci Ta Madina,
Sashen Bincikin Ilimi

Ɓangaren Fassara

www.iu.edu.sa

# RUKUNAN IMANI

Fassarar
**Muhammad Muslim Ibrahim**
**1424H**

أركان الإيمان بلغة الهوسا

المملكة العربية السعودية
وزارة التعليم العالي
الجامعة الإسلامية بالمدينة المنورة
عمادة البحث العلمي
قسم الترجمة

www.iu.edu.sa

# أركان الإسلام

## بلغة الهوسا

ترجمة/ محمد الحاج أبو بكر

بسم الله الرحمن الرحيم

# DA SUNAN ALLAH MAI YAWAN RAHAMA MAI MATUKAR JIN KAI

Yabo da godiya duka na Allah ne, salati da salami su tabbata ga Annabin da babu wani annabi bayansa, Annabinmu Muhammadu ɗan Abdullahi.

Bayan haka, haƙiƙa yaɗa ilimummukan addini yana da tasiri mai ƙarfin gaske cikin bayyana haƙiƙanin musulunci da tabbatar da ginshiƙansa da ma ciyar da al'umma gaba cikin rayuwarta. Wannan babbar manufa kuwa ita ce manufar da jami'ar Musulunci ta Madina take kai gwauro ta kai mari domin ganin an cin mata gwargwadon iko, ta hanyar da'awa da karantarwa.

A cikin nasa ƙoƙarin na ganin an cin ma wannan burin, sashin nazarin binciken ilimi na jami'ar ya ƙirƙiro aikace-aikace daban-daban masu manufa a fagen na ilimi, wanda daga cikinsu har da akwai wasu tsararrun rubuce-rubuce kan musulunci da kyawawan siffofinsa, da nufin yaɗa su domin kwaɗayinsa na yi wa 'ya'yan wannan al'umma ta musulunci guzuri mafi aminci kuma mafi inganci a ilimin musulunci; ta ɓangaren aƙida da ɓangaren shari'a.

To wannan rubutun ma da muke gabatarwa game da "Rukunan Imani" ɗaya ne daga cikin tsare-tsaren wannan sashi; domin shi ne ya gayyaci malaman da suka rubuta shi -daga cikin malaman wannan jami'a- sannan kuma ya ɗora wa 'yan kwamitin ilimi da ke ƙarƙashinsa da su yi bitar rubutun waɗancan malaman gami da gyara shi da kuma tsara shi har ya fito cikin surar da ta dace da manufofin wannan sashe, tare da mai da kai sosai wajen haɗa kowacce mas'ala da dalilanta. Manufar wannan rubutu dai a wajen sashen ilimi ba wata manufa ba ce illa sauƙaƙawa 'ya'yan musulmi hanyar samun ilimin addini mai amfani, wannan

shi ya sa ya nemi a fassara masa waɗannan littattafan zuwa harasa daban-daban na duniya; domin yaɗa su da kuma sa su cikin gizo-gizon sadarwa ta duniya (wato internet).

To muna dai roƙon Allah Mai girma da ɗaukaka Ya saka wa hukumar Masarautar larabawa ta Saudiya mafi alherin sakamako kuma mafi cikarsa saboda ƙoƙarin da take yi wajen yi wa musulunci hidima da yaɗa shi da kuma kare shi, da kuma irin abin da wannan jami'a take samu daga wajenta na kulawa da taimakawa.

Muna kuma roƙon Allah Mai yawan albarka da ɗaukaka da Ya amfanar da mutane da wannan littafi, Ya kuma datar da mu wajen buga sauran aikace-aikacen ilimi na wannan sashe don baiwarSa da karamcinSa Maɗaukaki, kuma muna roƙonSa da Ya datar da mu baki ɗaya zuwa ga aikata abubuwan da Yake so kuma Yake yarda da su, Ya kuma sa mu daga cikin masu kira zuwa ga shiriya tare da taimakawa gaskiya.

Allah Ya ƙara salati da salami da albarka ga BawanSa, AnnabinSa Muhammadu tare da 'yan gidansa da sahabbansa baki ɗaya.

SASHEN BINCIKEN ILIMI

Da sunan Allah Mai yawan rahama  Mai yawan jin ƙai

# RUKUNAN IMANI

Rukunan Imani su ne: Imani da Allah da Mala'ikunSa da LittafanSa da ManzanninSa da Ranar Lahira da Kaddara; alherinta da sharrinta.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ وَلَٰكِنَّ ٱلۡبِرَّ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلۡكِتَٰبِ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ ﴾ (البقرة ١٧٧)

Ma'ana: ((Sai dai (mai) biyayya (ga Allah shi ne) wanda ya yi imani da Allah da Ranar Lahira da Mala'iku da Littafai da Annabawa)). (Baƙara: 177)

Haka nan Allah Maɗaukaki ya ce:

﴿ ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مِن رَّبِّهِۦ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّن رُّسُلِهِۦۚ ﴾ (البقرة ٢٨٥)

Ma'ana: ((Manzo ya yi imani da abin da aka saukar masa daga Ubangijinsa haka nan Muminai; kowa –daga cikinsu- ya yi imani da Allah da Mala'ikunSa da LittattafanSa da ManzanninSa, (suna cewa) "Mu ba ma banbanta tsakanin manzannin naSa, kuma suka ce: "mun ji mun bi, ka gafarta mana ya Ubangijinmu, kuma gare ka ne makoma take"). (Baƙara: 285)

Allah Maɗaukaki ya ce:

﴿ إِنَّا كُلَّ شَيۡءٍ خَلَقۡنَٰهُ بِقَدَرٖ ٤٩ ﴾ (القمر ٤٩)

Ma'ana: ((Haƙiƙa Mu, kowanne abu mun halicce shi ne da wani tsari)). (Kamar: 49)

Annabi (s.a.w) ya ce:

"الإيمان أن تؤمن بالله، وملائكته، وكتبه، ورسله، واليوم الآخر، وتؤمن بالقدر خيره وشره". [ رواه مسلم ].

Ma'ana: "Imani shi ne ka yarda da Allah da Mala'ikunSa da LittattafanSa da ManzanninSa da Ranar Lahira, kuma ka yarda da Kaddara; alherinta da sharrinta".

IMANI: Furuci ne da harshe tare da ƙuduri a zuci haɗa da aiki da gaɓɓai, yana ƙaruwa, yana kuma raguwa.

Allah Maɗaukaki yana cewa:

﴿ إِنَّمَا ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَجِلَتْ قُلُوبُهُمْ وَإِذَا تُلِيَتْ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُهُۥ زَادَتْهُمْ إِيمَٰنًا وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ يَتَوَكَّلُونَ ﴿٢﴾ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ يُنفِقُونَ ﴿٣﴾ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُؤْمِنُونَ حَقًّا ۚ لَّهُمْ دَرَجَٰتٌ عِندَ رَبِّهِمْ وَمَغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ ﴿٤﴾ ﴾ (الأنفال ٠٠٢-٠٠٤)

Ma'ana: ((Ba wasu ba ne muminai face waɗanda da zarar an kira Allah sai zukatansu su razana, idan kuma aka karanta musu ayoyinSa sai su ƙara musu imani, kuma ga Allah kaɗai suke dogaro. Su ne waɗannan da suke tsaida sallah kuma suke ciyarwa daga abin da Muka azurta su da shi. Waɗannan su ne muminai na gaskiya, suna da darajoji a wajen Ubangijinsu tare da gafara da arziki mai yawa). (Anfal: 2-4).

Allah Maɗaukaki ya ce:

﴿ وَمَن يَكۡفُرۡ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا ١٣٦ ﴾ (النساء ١٣٦)

Ma'ana: ((Duk wanda ya kafirce wa Allah da Mala'ikunSa da LittattafanSa da Ranar Lahira, to haƙiƙa ya ɓata ɓata mai nisa)). (Nisa'i: 136)

Saboda haka akwai imani da harshe; kamar zikiri, addu'a, umarni da kyakkyawan aiki, hana mummunan aiki, karatun Alƙur'ani da makamantansu.

Akwai kuma imani da zuci; kamar ƙudurce kaɗaitakar Allah a cikin rububiyarSa (wato: mulki da halitta) da kaɗaitakarSa a cancantar bauta, da kaɗaitakarSa a sunayenSa da siffofinSa, da ƙudurce wajabcin bautar Allah shi kaɗai ba tare da an haɗa shi da wani abin bauta ba, da sauran abubuwan da suke da alaƙa da zuciya kamar niyyoyi da manufofin ayyukan bayi. Haka nan (ayyukan da malamai ke kiransu) "ayyukan zuci" suna shiga cikin imanin da a ke yi da zuciya; Misalinsu shi ne: son Allah, tsoronSa, komawar zuciya gare Shi da dogaro da Shi, da makamantansu.

Daga cikin abubuwan da sunan imani ya ƙunsa (bayan aikin harshe da na zuciya) akwai ayyukan gaɓɓai; irin su sallah, azumi, da dai sauran rukunan musulunci, da jihadi saboda ɗaukaka kalmar Allah, neman ilimi da makamantansu.

Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa:

﴿ وَإِذَا تُلِيَتۡ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُهُۥ زَادَتۡهُمۡ إِيمَٰنٗا ﴾ (الأنفال ٠٠٢)

Ma'ana: ((Idan aka karanta musu ayoyin (Allah) sai su ƙara musu imani ..)). (Anfal: 2)

A wani wajen kuma Allah cewa ya yi:

﴿ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ ٱلسَّكِينَةَ فِى قُلُوبِ ٱلْمُؤْمِنِينَ لِيَزْدَادُوٓاْ إِيمَـٰنًا مَّعَ إِيمَـٰنِهِمْ ۗ ﴾ (الفتح ٠٠٤)

Ma'ana: (( (Allah) Shi ne wanda ya saukar da nutsuwa a cikin zukatan Muminai domin su ƙara imani tare da imanin da suke da shi)). (Fathi: 4)

Imani yana daɗuwa a duk lokacin da bawa ya ƙara ayyukan ɗa'a ga Allah ya yawaita ibada, yana kuma raguwa a duk lokacin da ɗa'arsa da ibadarsa suka ragu, kamar yadda aikata saɓo ma yake tasiri a kan imani; har ma idan saɓon ya kai babbar shirka ko babban kafirci to sai ya warware asalin imani ya ɓata shi, idan kuma bai kai haka ba to sai ya hana imanin kai wa matakin da yake wajibi ne ya kai shi, ko kuma ya ɓata shi ya raunana shi.

Allah Maɗaukaki yana cewa:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغْفِرُ أَن يُشْرَكَ بِهِۦ وَيَغْفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُ ۚ ﴾ (النساء ٠٤٨)

Ma'ana: ((Haƙiƙa Allah baya yafe (laifin) shirka da shi, (amma) kuma yana yafe duk abin da bai kai haka ba ga wanda ya so yafewa)). (Nisa' 48).

Allah Ta'ala ya ƙara cewa:

﴿ يَحْلِفُونَ بِٱللَّهِ مَا قَالُواْ وَلَقَدْ قَالُواْ كَلِمَةَ ٱلْكُفْرِ وَكَفَرُواْ بَعْدَ إِسْلَـٰمِهِمْ ﴾ (التوبة ٠٧٤)

Ma'ana: ((Suna rantsewa da Allah cewa ba su faɗi komai ba, alhali sun faɗi kalmar kafirci, kuma (saboda haka) sun kafirce bayan da sun musulunta)) (Tauba: 74)

Annabi (s.a.w) kuma ya ce:

"لا يزني الزاني حين يزني وهو مؤمن، ولا يسرق السارق حين يسرق وهو مؤمن، ولا يشرب الخمر حين يشربها وهو مؤمن". [ متفق عليه ].

Ma'ana: ((Mazinaci baya yin zina -a lokacin da yake cikin yin zinar- alhali yana tare da imani, haka nan shi ma ɓarawo baya yin sata tare da imani -a daidai lokacin da yake yin satar, shi ma mai shan giya ba ya shanta a daidai lokacin da yake shanta alhali yana da imani)). Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

# RUKUNI NA ƊAYA: IMANI DA ALLAH MAƊAUKAKIN SARKI

(1) (GINSHIKAN) TABBATUWAR IMANI:

Imani da Allah Maɗaukakin Sarki yana tabbata ne da abubuwa masu zuwa:

**Na farko:** Kudurce cewa dukkanin waɗannan ababan halittu suna da ubangiji guda ɗaya, wanda shi shi kaɗai ya halicce su kuma shi ne mamallakinsu, shi ke da ikon sarrafa su da sarrafa dukkanin al'amuransu: arzikinsu, iko a kansu, aikace-aikacensu, raya su, kashe su, amfaninsu da cutarsu duka yana hannunSa, babu wani ubangiji in ba shi ba, shi kaɗai yake aikata duk abin da ya ga dama, kuma yake hukunta duk abin da ya so, yana ɗaukaka wanda ya so, ya kuma ƙasƙanta duk wanda ya so, mulkin sammai da ƙassai duka nasa ne, kuma shi ne Mai cikakken iko bisa ga komai, Mai cikakken ilimin komai da komai, Mawadaci ga barin waninSa, dukkanin al'amura naSa ne, kuma dukkanin alheri a hannunSa yake. Ba shi da abokin tarayya a cikin ayyukanSa, babu kuma wani mai rinjayarSa a kan wani lamari naSa, kai ba ma haka ba! dukkanin halittu –mala'iku da mutane da aljanu- bayi ne a gare Shi, ba su da ikon fita daga ƙarƙashin mulkinSa, da ikonSa da nufinSa, Tsarki ya tabbatar masa. AyyukanSa ba su ƙididdiguwa, babu kuma wani lissafi da zai iya iyakance su. Kuma dukkanin waɗannan siffofi haƙƙinSa ne shi shi kaɗai ba tare da wani ya yi tarayya da shi ba a cikinsu, babu kuma wanda ya cancanshe su in ba shi ba, bai halatta ba a jingina su ga wani ko a tabbatar da ko da wasu daga cikinsu ne ga wanin Allah Mabuwayin Sarki Maɗaukaki.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعۡبُدُواْ رَبَّكُمُ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ٢١ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ فِرَٰشٗا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءٗ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخۡرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزۡقٗا لَّكُمۡۖ ﴾ (البقرة ٠٢١-٠٢٢)

Ma'ana: ((Ya ku mutane ku bauta wa Ubangijinku wannan da shi ne ya halicce ku ku da waɗanda suka gabace ku, domin ku dace da taƙawa (wato Allah ya azurta ku da tsoronSa da bin dokokinSa). Shi ne wanda ya sanya ƙasa shimfiɗa a gareku, ya kuma sanya sama ta zama rufi, ya kuma saukar da ruwa daga sama, sai ya fitar muku da wasu daga cikin 'ya'yan itatuwa domin amfaninku .. )). (Baƙara: 21-22)

Allah ya ƙara cewa:

قُلِ ٱللَّهُمَّ مَٰلِكَ ٱلۡمُلۡكِ تُؤۡتِي ٱلۡمُلۡكَ مَن تَشَآءُ وَتَنزِعُ ٱلۡمُلۡكَ مِمَّن تَشَآءُ وَتُعِزُّ مَن تَشَآءُ وَتُذِلُّ مَن تَشَآءُۖ بِيَدِكَ ٱلۡخَيۡرُۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٦ ﴾ (آل عمران ٠٢٦)

Ma'ana: ((Ka ce: Ya Allah ya Sarkin Sarauta, Kai ne Kake ba da mulki ga wanda ka ga damar ba wa, kuma Kai Kake ƙwace shi daga wajen wanda ka ga dama, Kai ka ke ɗaukaka duk wanda ka ga damar ɗaukakawa, kuma Ka ƙasƙanta wanda ka ga damar ƙasƙantarwa, dukkanin alheri a hannunKa yake, haƙiƙa Kai ne mai cikakken iko a kan komai da komai)).

﴿ ۞ وَمَا مِن دَآبَّةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزۡقُهَا وَيَعۡلَمُ مُسۡتَقَرَّهَا

وَمُسۡتَوۡدَعَهَاۚ كُلّٞ فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ٦ ﴾ (هود ٠٠٦)

Ma'ana: ((Babu wata halitta mai tafiya a bayan ƙasa face arzikinta (ci da sha da buƙatunta) yana hannun Allah, kuma yana sane da mazauninta da ma'ajiyarta (wato bayan mutuwa), dukkanin wannan yana rubuce a cikin littafi bayyananne (wato Lauhul Mahfuz) )). (Hud:6)

Allah ya ce:

﴿ أَلَا لَهُ ٱلۡخَلۡقُ وَٱلۡأَمۡرُۗ تَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ﴾ (الأعراف ٠٥٤)

Ma'ana: ((Ku saurara ku ji! Yin halitta da ba da umarni duka naSa ne, alheran Allah Ubangijin talikai sun yawaita)) (A'raf: 54)

**Abu na biyu** da imani yake tabbata da su, shi ne: Kudurce kaɗaituwar Allah da mafi kyawun sunaye da kuma mafi kammalar siffofi, waɗanda ta hanyar wasu daga cikinsu ne ya shiryar da bayinSa zuwa ga ZatinSa, a cikin littafinSa ko kuma a sunnar Cikamakin annabawanSa da manzanninSa Muhammadu (s.a.w).

Allah Matsarkakin Sarki Maɗaukaki ya ce:

﴿ وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ فَٱدۡعُوهُ بِهَاۖ وَذَرُواْ ٱلَّذِينَ يُلۡحِدُونَ فِيٓ أَسۡمَٰٓئِهِۦۚ سَيُجۡزَوۡنَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٨٠ ﴾ (الأعراف ١٨٠)

Ma'ana: ((Kuma Allah yana da mafiya kyawun sunaye, saboda haka ku kiraye Shi da su, ku rabu da waɗanda suke fanɗarewa game da sunayen nasa, da sannu za mu saka musu da abin da suka kasance suna aikatawa)). (A'raf: 180)

Annabin Rahama (s.a.w) kuma ya ce:

"إن لله تسعة وتسعين اسماً، من أحصاها دخل الجنة، وهو وتر يحب الوتر". [متفق عليه].

Ma'ana: "Haƙiƙa Allah yana da wasu sunaye guda casa'in

da tara, duk wanda ya kiyaye su zai shiga aljanna, kuma shi Allah mara ne, yana son mara". Bukhari da Muslim suka ruwaito shi.

Wannan aƙida (ta sunaye da siffofin Allah) tana tsayuwa ne bisa wasu manya-manyan ginshiƙai guda biyu:

**Ginshiƙi na farko:** Cewa Allah yana da mafiya kyawun sunaye da kuma mafiya ɗaukakar siffofi waɗanda suke ɗauke da ma'anoni na kamala, ba su kuma da wata alaƙa da tawaya ta kowace fuska, (waɗannan abubuwa duka shi shi kaɗai ya cancance su); saboda haka ba shi da wani wanda yake daidai da shi a cikinsu, kamar yadda babu wani mahaluki da yake tarayya da shi cikin wani abu daga cikinsu.

Daga cikin sunayen nasa Matsarkaki kuma Maɗaukakin Sarki akwai: "Al-Hayyu" wato: "Rayayye", kuma yana da siffar: "Al-Hayatu", wato "Rayuwa", wacce ya wajaba a tabbatar masa da ita Mabuwayi Maɗaukaki ta fuskar kamalar da ta dace da shi, wannan rayuwa ta Allah rayuwa ce cikakkiya kuma dawwamammiya, dukkanin dangogin kamala sun haɗu a cikinta; irin su ilimi, iko, da sauransu, kuma rayuwar Allah rashi bai gabace ta ba, kamar yadda ƙarewa ba za ta cin mata ba. Allah Maɗauki ya ce:

قال تعالى: ﴿ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡحَيُّ ٱلۡقَيُّومُۚ لَا تَأۡخُذُهُۥ سِنَةٞ وَلَا نَوۡمٞۚ ﴾ [سورة البقرة:الآية ٢٥٥].

Ma'ana: ((Allah, babu wani abin bauta na gaskiya face shi, Rayayye (cikakkiyar rayuwar da ba ta da farko ba ta da ƙarshe), Tsayayye Mai tsaida waninSa, gyangyaɗi ba ya ɗaukansa wala bacci ..)) (Baƙara: 255)

**Ginshiƙi na biyu** (a aƙidar sunaye da siffofin Allah): Cewa Allah ta'ala tsarkakakke ne daga dukkanin wata siffa ta tawaya da dukkan wani aibi gaba ɗaya, kamar bacci, gajiya, jahilci, zalunci da makamantansu, kamar yadda yake

tsarkakakke ne daga kamanceceniya da duk wani abin halitta. Saboda haka ya wajaba a kore wa Allah duk abin da ya kore wa kanSa, ko AnnabinSa ya kore maSa, tare da ƙudurce cewa Allah ya siffantu da cikakkiyar siffar da take kishiya ce ga siffar da aka kore masa ɗin; alal misali, a lokacin da muka ce: Allah ba ya gyangyaɗi ko bacci, to kore gyangyaɗi yana tabbatar masa da cika da kamalar siffarSa ta: "Kayyumiyya" (tsayuwa da kanSa da tsayar da waninSa), kore bacci kuma yana tabbatar masa da kamalar siffarSa ta "Al-Hayatu" wato rayuwa –kamar yadda ya gabata-. To haka nan duk wata siffa da ake kore wa Allah wannan korewar tana ƙunshe da tabbatar da cika tare da kamalar kishiyarta. Allah shi kaɗai yake cikakke, duk abin da ba shi ba kuwa tauyayye ne. Allah Ta'ala ya ce:

قال تعالى: ﴿ لَيْسَ كَمِثْلِهِۦ شَىْءٌ ۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْبَصِيرُ ﴾ [سورة الشورى:الآية ١١]

Ma'ana: (( (Allah) Babu wani abu kwatankwacinSa, kuma shi ne Jiyau Ganau)). (Shura: 11)

Ya kuma ce:

وقال تعالى: ﴿ وَمَا رَبُّكَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ﴾ [سورة فصلت:الآية ٤٦].

Ma'ana: ((Ubangijinka ba azzalumi ba ne ga bayinSa)). (Fussilat: 46)

Allah Ta'ala ya ce:

وقال تعالى: ﴿ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُعْجِزَهُۥ مِن شَىْءٍ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِى ٱلْأَرْضِ ۚ﴾ [سورة فاطر:الآية ٤٤].

Ma'ana: ((Babu wani abu da zai gagari Allah a sammai wala a ƙassai)). (Faɗir: 44)

Allah Ta'ala ya ce:

وقال تعالى : ﴿ وَمَا كَانَ رَبُّكَ نَسِيًّا ﴾ [سورة مريم:الآية ٦٤].

Ma'ana: ((Ubangijinka bai zamanto mai mantuwa ba)). (Maryam: 64)

Imani da sunayen Allah da siffofinSa da ayyukanSa shi ne kaɗai tafarkin da zai kai mutum ga sanin Allah da kuma yin bauta gare shi; domin kuwa Allah ya ɓuya daga mahangar dukkanin halittu, ya hana su gan shi a nan duniya da idanunsu, sai kuma ya buɗe musu wannan ƙofa ta ilimi, wacce daga ita ne za su iya shiga zuwa sanin ubangijinsu kuma abin bautarsu, sai su bauta masa gwargwadon wannan ingantacce, kuma amintaccen ilimin da suka samu game da shi; domin dama duk mai bauta ba ya bauta wa komai sai abin da yake da masaniyar siffar sa, saboda haka wanda duk yake wofintar da Allah daga siffofinSa to babu yake bautawa, wanda kuma yake kamanta Allah da wasu halittu shi kuma gunki yake bautawa, shi kuwa musulmi yana bauta wa Allah ne Makaɗaici, Abin nufi da buƙata, Wanda bai haifa ba kuma ba a haife Shi ba, kuma babu wani kini a gare Shi.

Ya kamata a kula da waɗannan al'amura yayin tabbatar wa da Allah kyawawan sunayenSa:

1- A yi imani da tabbatuwar dukkanin kyawawan sunayen da suka zo cikin Alƙur'ani da Sunna, ba tare da an ƙara ko an rage su ba.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ هُوَ ٱللَّهُ ٱلَّذِى لَآ إِلَـٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْمَلِكُ ٱلْقُدُّوسُ ٱلسَّلَـٰمُ ٱلْمُؤْمِنُ ٱلْمُهَيْمِنُ ٱلْعَزِيزُ ٱلْجَبَّارُ ٱلْمُتَكَبِّرُ ۚ سُبْحَـٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٢٣﴾ ﴾ [سورة الحشر:الآية ٢٣].

((Shi ne Allah wanda babu wani abin bautawa na gaskiya

sai shi, Cikakken Sarki, Tsarkakau, Kuɓutacce daga duk wani aibi, Mai gaskatawa (ga ManzanninSa da ba su hujjoji), Mai kula da komai, Mabuwayi, Mai dole (kuma Mai ɗora karayar bayinSa), Mai ji da girma, tsarki ya tabbata ga Allah daga dukkanin ababan da suke yi masa tarayya da su)). (Hashr: 23)

Ya tabbata cikin sunnar Manzon Allah (s.a.w) cewa ya ji wani mutum yana cewa:

"اللهم إني أسألك بأن لك الحمد، لا إله إلا أنت، المنان، بديع السموات والأرض، يا ذا الجلال والإكرام، يا الحي يا القيوم".

Ma'ana: "Ya Allah Ina roƙonka da cewa dukkanin yabo da godiya naka ne, babu abin bautawa na gaske sai kai, Mai yawan baiwa, Mahaliccin sammai da ƙassai, ya Ma'abocin girma da ɗaukaka, ya Rayayye da cikakkiyar rayuwa, ya Tsayayye Mai tsaida waninSa"

Sai Annabi (s.a.w) ya ce: "Kun san da abin da ya kirayi Allah? Sai suka ce: Allah da ManzonSa ne suka sani. Sai ya ce: Na rantse da wanda raina yake hannunSa, haƙiƙa ya kira Allah da sunanSa mafi ɗaukaka, wanda idan aka kira shi da shi sai ya amsa, idan kuma aka roƙe shi da shi sai ya bayar (da abin buƙatar)". Abu Dawuda da Ahmadu ne suka ruwaito shi.

2- Imani da cewa Allah shi ne wanda ya raɗawa kanSa waɗannan sunayen, babu wani cikin bayinSa da ya raɗa masa su, kuma Allah ya yabi kanSa da waɗannan sunayen tun tuni, ba wai fararru ba ne ko ababan halitta.

3- Imani da cewa kyawawan sunayen Allah suna nuna ma'anoni masu matuƙar kamalar da babu wata tawaya a cikinsu ta kowace fuska; saboda haka imani da waɗannan ma'anoni wajibi ne kamar yadda imani da su kansu sunayen yake wajibi.

4- Wajabcin girmama waɗannan ma'anoni na sunayen

Allah da gudun yi musu karan tsaye ta fuskar kautar da su daga ma'anoninsu ko kore musu ma'anonin nasu ɗungurungun.

5- Imani da abin da kowanne suna yake nunawa na hukunci, da abin da ke ɗoruwa a kan wannan imani na daga ayyuka da siffofi.

Domin fito da waɗannan al'amura guda biyar fili, bari mu buga misalinsu da Sunan Allah: "Assami' " wato "Jiyau". Yana wajaba a kula da abubuwa masu zuwa:

a- Imani da tabbatuwar sunan "Assami" ga Allah domin ya zo a cikin Al-Kur'ani da Sunna.

b- Imani da cewa Allah shi ne ya raɗa wa kanSa wannan suna, kuma ya faɗe shi ya kuma saukar da shi a cikin littafinSa mai girma.

c- Imani da cewa sunan Allah "As-Sami' " ya ƙunshi siffar "ji", wacce ɗaya ce daga cikin siffofinSa.

d- Wajabcin girmama siffar Allah ta "ji", wacce sunanSa "As-Sami' " ya ƙunsa, kuma a guji canza shi ko ma kore shi baki ɗaya.

e- Imani da cewa Allah yana jin komai, kuma jinSa ya ishi duk wani sauti, haka nan imani da abubuwan da suke ginuwa a kan wannan imani, kamar wajabtuwar muraƙabar Allah (wato jin cewa Allah yana kallonka yana kula da kai) da tsoronSa da cikakken yaƙini da cewa Allah Mabuwayi Maɗaukaki babu wani ɓoyayyen abu da zai iya ɓoye masa.

Abin da ya shafi tabbatarwa da Allah siffofinSa kuma ya kamata a kula da abubuwa masu zuwa:

1- Tabbatar masa dukkanin siffofin da suka zo a cikin Alƙur'ani da Sunna tabbatarwa ta haƙiƙa ba tare da an canza su ko an kore su ba.

2- Tabbataccen ƙudurin cewa Allah Ta'ala ya siffantu da siffofin kamala, kuma tsarkakakke ne daga duk wasu siffofin tawaya da duk wani aibi.

3- Barin haɗa kama tsakanin siffofin Allah da na halittunSa; domin Allah Matsarkaki ba shi da wanda ya yi kama da shi, a siffofinSa ko a ayyukanSa, Allah Ta'ala ya ce:

ﭐ لَيۡسَ كَمِثۡلِهِۦ شَيۡءٞۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ﴾[سورة الشورى:الآية ١١].

Ma'ana: (( (Allah) Babu wani abu kwatankwacinSa, kuma shi ne Jiyau Ganau)). (Shura: 11)

4- Ɗebe haso gaba ɗaya daga sanin yanayin siffofin Allah; domin babu wanda ya san yadda siffofin Allah suke sai Shi; domin babu wani mahaluki da yake da wata hanya ta sanin hakan.

5- Imani da abin da ke ginuwa bisa kan waɗannan siffofi na daga hukunce-hukunce, da kuma abubuwan da suke haifarwa ga wanda ya yi imani da su; domin kuwa kowace siffa tana da ibadarta ta musamman.

Domin fito da waɗannan al'amura guda biyar fili, bari mu buga misalinsu da siffar "Istiwa'i" wato daidaiton Allah bisa al'arshi, inda za mu ga cewa ya wajaba a kula da abubuwa masu zuwa a wajen tabbatar da ita:

a- Tabbatar da siffar "istiwa'i" da kuma imani da ita saboda ta zo a cikin nassoshi shari'a; Allah Ta'ala ya ce:

: ﭐ ٱلرَّحۡمَٰنُ عَلَى ٱلۡعَرۡشِ ٱسۡتَوَىٰ ﴿٥﴾ [سورة طه:الآية ٥]

Ma'ana: (( (Allah) Mai yawan rahama Ya daidaita bisa al'arshi)). (Ɗaha: 5)

b- Tabbatar da siffar ta istiwa'i ga Allah Mabuwayi Maɗaukaki a bisa fuskar kamalar da ta dace da shi Maɗaukaki, da kasancewar ma'anarta shi ne birbisantar Allah da ɗaukakarSa a kan al'arshinSa ɗaukaka da birbishi na haƙiƙa, irin yadda ya dace da girman Allah da wadatarSa.

c- Barin kamanta istiwa'inSa (daidaitonSa) bisa al'arshi da daidaiton halittunSa; domin kuwa shi Allah Mawadaci ne ga barin al'arshi, ba ya buƙatarSa, amma daidaiton abin halitta yana tare da buƙatuwarSa ga abin da ya daidaita a kansa, saboda faɗin Allah Ta'ala:

ا لَيۡسَ كَمِثۡلِهِۦ شَيۡءٞۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ﴾ [سورة الشورى:الآية ١١].

Ma'ana: ((Babu wani abu da ya yi kama da shi, kuma shi ne Jiyau, Ganau)). (Shura: 11)

d- Barin kutsawa cikin yanayin yadda istiwa'in Mahalicci a bisa al'arshi yake; domin lamari ne na gaibu babu wanda ya san shi sai Allah Mabuwayi Maɗaukaki.

e- Imani da hukunci da kuma sakamakon da ke ginuwa kan wannan siffa ta istiwa'i; kamar tabbatar wa Allah girma, ɗaukaka da isa waɗanda suka dace da Shi, daga cikin hanyoyin gano wannan, akwai duba zuwa ga cikakkiyar ɗaukakar Allah bisa halittu baki ɗaya (istiwa'i da uluwwi), da kuma fuskantuwar zukata zuwa gare shi a can sama, kamar yadda mai sajada yake cewa: "Tsarki ya tabbata ga Ubangijina Mafi ɗaukaka".

**Abu na uku da Imani yake tabbatuwa da shi:** Bawa ya ƙudurce cewa Allah shi ne Ubangijin gaskiya, kuma shi kaɗai ne ya cancanci a yi dukkanin ibadoji na zahiri da na baɗini dominSa, ba shi da abokin tarayya.

Allah Ta'ala ya ce:

ا وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَۖ﴾ [سورة النحل:الآية ٣٦].

Ma'ana: ((Haƙiƙa mun aiko wa kowacce al'umma manzo (da cewa) ku bauta wa Allah ku kuma nisanci Ɗagutu)) (Nahl: 36)

Kuma babu wani manzo face ya ce wa mutanensa:

﴿ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥٓ ﴾ [سورة الأعراف:الآية ٥٩].

Ma'ana: ((Ku bauta wa Allah ba ku da wani abin bautawa da gaskiya face shi)). (A'raf: 59)

Har ila yau ya ce:

﴿ وَمَآ أُمِرُوٓا۟ إِلَّا لِيَعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ ﴾ [سورة البينة:الآية ٥].

Ma'ana: ((Ba a umarce su da komai ba sai dai su bauta wa Allah suna masu tsarkake ibada a gare shi tare da nisantar shirka)). (Bayyina: 5)

Ya zo a cikin ingantattun littattafai biyu: cewa Annabi (s.a.w) ya ce wa Mu'az:

أتدري ما حق الله على العباد، وما حق العباد على الله؟". قلت: الله ورسوله أعلم. قال: "حق الله على العباد أن يعبدوه ولا يشركوا به شيئاً، وحق العباد على الله ألا يعذب من لا يشرك به شيئاً".

Ma'ana: "Ko ka san menene haƙƙin Allah a kan bayi, kuma menene haƙƙinsu a wajen Allah? Sai ya ce: Allah da ManzonSa ne suka fi sani. Sai ya ce: Haƙƙin Allah a kan bayinSa shi ne su bauta maSa kuma kada su haɗa shi da kowa a bautar. Haƙƙinsu kuma a wajenSa shi ne kada ya azabtar da duk wanda bai haɗa shi da kowa ba)).

Ubangijin gaskiya shi ne wanda zukata suke begenSa sai su cika da sanSa su bar san waninSa, kuma su wadatu da tsammanin alherinSa su bar tsammanin alherin waninSa, ta kuma wadatu da roƙonSa, neman taimakonSa da tsoronSa ga barin waninSa.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ هُوَ

ٱلۡبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡكَبِيرُ ﴿٦٢﴾ ﴾ [سورة الحج:الآية ٦٢].

((Wannan (bayani da ya gabata) kuwa saboda haƙiƙa Allah shi ne abin bauta tabbatacce na gaske, amma abin da suke kira –kiran bauta- wanda ba shi ba shi ne ubangijin ƙarya maras tabbas, kuma haƙiƙa shi Allah shi ne Maɗaukaki matuƙar ɗaukaka Mai girma)). (Haj: 62)

Wannan shi ne kaɗaita Allah da ayyukan bayi.

**Muhimmancin Tauhidi:**

Muhimmancin Tauhidi yana fitowa fili cikin abubuwa masu zuwa:

1- Cewa shi ne farkon wannan addini, kuma shi ne tuƙewarsa da ƙarshensa, shi ne kuma zahirinsa da baɗininsa, kuma shi ne da'awar manzanni alaihimus salam.

2- Saboda tauhidi ne Allah ya halicci dukkanin halittu, ya turo manzanni kuma ya saukar da littattafai, kuma saboda shi ne halittu baki ɗaya suka saɓa har suka zama gida biyu; muminai da kafirai, 'yan aljanna da 'yan wuta.

3- Shi ne farkon abin da yake wajabtuwa bisa ga "mukallafi" (wanda shari'a ta hau kansa), kuma shi ne farkon abin da bawa zai shiga musulunci da shi, kuma shi ne abu na ƙarshe da zai fita duniya da shi.

**Kammaluwar Tauhidi**

Ana nufin tsarkake shi da tace shi daga duk wani birbiɗin shirka, bidi'a da kuma saɓo. Kammala tauhidi ya kasu gida biyu: wajabtacciyar kammalawa da kuma mustahabbiyar kammalawa.

Wajabtacciyar kammalawa tana kasancewa ne da abubuwa guda uku:

1- Tsarkake tauhidi daga shirka; abin da ke cin karo da asalin tauhidi.

2- Tsarkake shi daga bidi'o'i; waɗanda imma dai su

zamanto masu cin karo ne da wajabtacciyar kamalarsa, ko ma su zamanto masu fito-na-fito ne da asalinsa da tushensa, idan bidi'ar ta zamanto mai fitar wa ce daga musulunci ɗungurungun.

3- Tsarkake shi daga ayyukan saɓo waɗanda suke tauye shi kuma suke yi masa tasiri.

Ita kuwa Mustahabbiyar kammalar tauhidi tana nufin kammala abubuwan da ake neman mutum ya aikata su, amma ba su kai matsayin dole ba. Daga cikin misalansu:

a- Isa martaba "ihsani" (bauta wa Allah kamar ana ganinSa).

b- Isa martabar "yaƙini" (yarda da sakankancewa).

c- Isa martabar haƙuri mai kyau, wato ta hanyar barin kai ƙara ga wanin Allah ta'ala.

d- Isa matsayin wadatuwa da roƙon Allah ga barin bayin Allah.

e- Isa matsayin tawakkali ta yadda mutum zai bar wasu hanyoyin biyan buƙatarsa na halal; kamar mutum ya ƙi neman a yi masa tofi ko lalas; saboda tsabar dogaro da Allah.

f- Isa matsayin soyayya irin ta bauta, ta hanyar neman kusancin Allah da ayyukan nafilfili.

Duk wanda ya cika tauhidi kamar yadda aka yi bayaninsa, ya kuma tsira daga babbar shirka, to haƙiƙa wannan ya samu aminci ga barin dawwama a cikin wuta, wanda kuma duk ya kuɓuta daga babar shirka da ƙarama ya kuma nisanci manya-manyan kaba'ira da sauran manyan zunubai to wannan shi ne mai cikakken aminci a duniya da lahira.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ ﴾

[سورة النساء:الآية ٤٨].

Ma'ana: ((Haƙiƙa Allah ba ya yafewa a yi shirka da shi, (sai dai) yana yafe abin da bai kai haka ba ga wanda ya so)) (Nisa': 48)

Allah ya ƙara cewa:

﴿ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمْ يَلْبِسُوٓاْ إِيمَٰنَهُم بِظُلْمٍ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلْأَمْنُ وَهُم مُّهْتَدُونَ ﴿٨٢﴾ ﴾ [سورة الأنعام:الآية ٨٢]

Ma'ana: ((Waɗanda suka yi imani ba su kuma cakuɗa imanin nasu da wani zalunci ba (wato shirka), to waɗannan su ne suke cikin aminci, kuma su ne shiryayyu)). (An'am: 82)

Kishiyar Tauhidi shi ne "Shirka". Shirka kashi uku ce:

1- Babbar Shirka mai warware asalin tauhidi, Allah ba ya yafe ta sai ga wanda ya tuba kurum, saboda haka duk wanda ya mutu a cikinta za a dawwamar da shi a cikin wuta. Babbar shirka ita ce mutum ya yi wa Allah kishiya a cikin bautarsa, ya zamo yana kiransa kamar yadda yake kiran Allah, yana nufinsa, dogaro da shi, tsammanin amfaninsa, sonsa da tsoronsa duka kamar yadda yake yi wa Allah.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّهُۥ مَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَقَدْ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِ ٱلْجَنَّةَ وَمَأْوَىٰهُ ٱلنَّارُ ۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ ﴾ [سورة المائدة:الآية ٧٢]

Ma'ana: ((Haƙiƙa duk wanda ya yi shirka da Allah to haƙiƙa Allah ya haramta masa aljanna, kuma wuta ce makomarsa, azzalumai kuma ba su da mataimaka)). (Ma'ida: 72)

2- Karamar Shirka, wacce ita kuma tana warware kamalar tauhidi ne. Wannan shirka itace duk wata hanya ko wata kafa da take kai wa zuwa ga babbar shirka, kamar

rantsuwa da wanin Allah da kuma ƙaramar riya.

3- Ɓoyayyar Shirka; ita ce shirkar da ta shafi niyyoyi da manufofi, tana iya zama babba ko ƙarama, kamar yadda dai aka yi bayani a kashi biyun farko da suka gabata.

An karɓo daga Mahmud ɗan Labid, Allah ya ƙara yarda da shi, cewa Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"إن أخوف ما أخاف عليكم الشرك الأصغر، قالوا وما الشرك الأصغر يا رسول الله ؟ قال: الرياء". [ رواه الإمام أحمد ]

Ma'ana: "Haƙiƙa abin da na fi ji muku tsoronsa shi ne ƙaramar shirka! Sai suka ce ya Rasulal Lah mecece ƙaramar shirka? Sai ya ce: "Riya". Ahmad ne ya ruwaito shi.

## (2) Ma'anar Ibada:

"Ibada" suna ne da ya haɗe duk wani abin da Allah yake so kuma ya yarda da shi, daga ƙudurce-ƙudurce da sauran ayyukan zukata da na gaɓɓai, da duk wani abin da yake kusantarwa zuwa ga Allah, sawa'un aiki ne ko bari.

Daga abubuwan da ke shiga ƙarƙashin sunan Ibada: duk wani abin da Allah ne ya shar'anta shi a littafinSa ko a sunnar ManzonSa, Waɗanda ibadoji ne daban-daban; akwai ibadojin zuciya, kamar rukunan imanin nan guda shida, tsoron Allah, tsammanin amfaninSa, dogaro da shi, kwaɗayin rahamarSa, tsoron narkonSa da dai sauran ibadojin. Akwai kuma ibadoji na zahiri kamar sallah, zakka , azumi da hajji.

Dukkanin wata ibada ba ta inganta sai ta ginu bisa wasu turaku guda biyu:

1- Tsarkake ibada ga Allah da rashin yin shirka a cikinta, wannan shi ne ma'anar shedawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah.

Allah Ta'ala yana cewa:

﴿ أَلَا لِلَّهِ ٱلدِّينُ ٱلۡخَالِصُۚ وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَ مَا نَعۡبُدُهُمۡ إِلَّا لِيُقَرِّبُونَآ إِلَى ٱللَّهِ زُلۡفَىٰٓ إِنَّ ٱللَّهَ يَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡ فِي مَا هُمۡ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَنۡ هُوَ كَٰذِبٞ كَفَّارٞ ٣ ﴾ [سورة الزمر:الآية ٣].

Ma'ana: ((Ku saurara ku ji! cewa tataccen addini na Allah ne, waɗanda kuwa suka riƙi wasu iyayen giji ba Shi ba (suna cewa: "Ba ma bauta musu sai kawai don su kusanta mu da Allah". Ba shakka Allah zai yi hukunci a tsakaninsu game da abin da suke sassaɓawa a cikinsa. Haƙiƙa Allah ba ya shiriyar wanda yake maƙaryaci kafiri)) (Zumar: 3)

Allah Ta'ala ya ƙara cewa:

﴿ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ ﴾ [سورة البينة:الآية ٥]

Ma'ana: ((Ba a umarce su da komai ba, sai dai su bauta wa Allah suna masu tsarkake ibada a gare shi, kuma suna masu karkacewa ɓata zuwa shiriya ..)). (Bayyina: 5)

Turke na biyu: Biyayya ga abin da Manzon Allah (s.a.w) ya zo da shi; wato mutum ya aikata irin abin da Annabi (s.a.w) ya aikata, kuma a bisa sifar da ya aikata, babu ƙari babu ragi. Wannan shi ne ma'anar shedawa cewa Ananabi Muhammadu (s.a.w) manzo ne.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ

﴿لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۚ﴾ [سورة آل عمران:الآية ٣١].

Ma'ana: ((Ka ce (da su ya Rasulal Lah): in dai kuna son Allah to ku bi ni sai Allah ya so ku, ya kuma gafarta muku zunubanku)). (Ali-Imran: 31)

Allah Ta'ala ya ce:

﴿وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ وَمَا نَهَىٰكُمۡ عَنۡهُ فَٱنتَهُواْۚ﴾

[سورة الحشر:الآية ٧].

Ma'ana: ((Kuma abin da Manzon Allah ya zo muku da shi sai ku yi riƙo da shi, abin da kuma ya hana ku sai ku hanu)). (Hashr: 7)

Kuma Allah Ta'ala ya ce:

﴿فَلَا وَرَبِّكَ لَا يُؤۡمِنُونَ حَتَّىٰ يُحَكِّمُوكَ فِيمَا شَجَرَ بَيۡنَهُمۡ ثُمَّ لَا يَجِدُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ حَرَجٗا مِّمَّا قَضَيۡتَ وَيُسَلِّمُواْ تَسۡلِيمٗا ٦٥﴾ [سورة النساء:الآية ٦٥].

Ma'ana: ((Na rantse da Ubangijinka ba za su zama muminai na gaskiya ba har sai sun sanya ka mai hukunci a kan abin da ya faru a tsakaninsu, sannan kuma ba za su sami wata tababa ba a zukatansu game da abin da ka hukunta, su kuma miƙa wuya gaba ɗaya)). (Nisa'i 65)

Cikakkiyar Bauta ba ta kammaluwa sai da samuwar abubuwa guda biyu:

1- Cikakkiyar soyayya ga Allah, ta yadda bawa zai gabatar da soyayyar Allah da son abin da Allah yake so akan son duk wani abin da ba su ba.

2- Cikakkiyar risinawa da ƙasƙantar da kai ga Allah, yadda bawa zai risina wa Allah ya bi umarninSa ya kuma nisanci haninSa.

Saboda haka kalmar "Ibada" tana nuna abin da ya haɗa cikakkiyar soyayya tare da cikakken ƙasƙantar da kai, risinawa, ƙaunar amfani da kuma tsoro; da samuwar waɗannan abubuwan ne bautar bawa ga mamallakinsa mahaliccinsa take kammaluwa, kular bawa da ibada kuwa ita ce za ta sa Allah ya so shi kuma ya yarda da shi; domin Allah yana so bawanSa ya kusance shi da aikata abubuwan da ya wajabta masa, kuma duk lokacin da bawa ya ƙara nafilfilin ibadu sai kusancinsa da Allah ya ƙaru, darajarsa ta ɗaukaku a wajen Allah, wannan kuma sai ya zamanto masa hanya ce ta shiga aljanna da falalar Allah da rahamarSa. Allah Ta'ala ya ce:

﴿ ٱدۡعُواْ رَبَّكُمۡ تَضَرُّعٗا وَخُفۡيَةًۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُعۡتَدِينَ ﴾

[سورة الأعراف:الآية ٥٥].

Ma'ana: ((Ku kirayi Ubangijinku kuna masu ƙasƙantar da kai tare da ɓoye wa, haƙiƙa shi ba ya son masu shige gona da iri)). (A'raf: 55)

**Dalilai da Hujjojin Kaɗaita Allah:**

Haƙiƙa shedu da dalilan kaɗaitakar Allah suna da ɗimbin yawa, wanda ya yi la'akari da su, ya aiwatar da tunaninsa wajen nazari a kansu, iliminsa zai kafu, yaƙininsa ya ƙaru a kan kaɗaituwar Allah Tsarkakakken Sarki Maɗaukaki, a cikin ayyukanSa, sunayenSa da siffofinSa da cancantarSa ga ibada.

Bari mu kawo wasu daga cikin waɗannan shedu, dalilai da hujjoji a matsayin misali ba ƙididdigewa ba:

a- Girman halittar wannan duniya, da shiryuwar zubin halittarta, da yawan nau'o'in halittun cikinta, da kuma matuƙar tsaruwar tsarin da take tafiya a kansa. Duk wanda ya kula da waɗannan abubuwa ya yi tunani a kansu zai tabbatar da kaɗaitakar Allah. Wanda ya ya nazari a cikin

halittar sammai da ƙassai, da yadda aka halicci rana da wata, da zubin ɗan Adam da dabbobi, da halittar tsirrai da sandararru zai samu cikakken ilimi da sakankancewa da cewa lallai suna da wani mahalicci mai cikakkiyar kamala a sunayenSa da siffofinSa da ubangijintakarSa; abin da ke nuna cewa shi kaɗai ne yake cancantar bauta.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَجَعَلْنَا فِي ٱلْأَرْضِ رَوَٰسِيَ أَن تَمِيدَ بِهِمْ وَجَعَلْنَا فِيهَا فِجَاجًا سُبُلًا لَّعَلَّهُمْ يَهْتَدُونَ ۝٣١ وَجَعَلْنَا ٱلسَّمَآءَ سَقْفًا مَّحْفُوظًا ۖ وَهُمْ عَنْ ءَايَٰتِهَا مُعْرِضُونَ ۝٣٢ وَهُوَ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ ۖ كُلٌّ فِى فَلَكٍ يَسْبَحُونَ ۝٣٣ ﴾ [سورة الأنبياء:الآيات ٣١-٣٣].

Ma'ana: ((Mun sanya turaku (na duwatsu) a ƙasa don kar ta rifta da su, Muka kuma sanya wurin tafiya (ya zama) hanyoyi don su gane (inda za su). Muka kuma sanya sama (ta zama) rufi amintacce, su kuwa (duk da haka) masu bijire wa ayoyinmu ne. (Allah) shi ne kuma Wanda Ya halicci dare da rana, da kuma rana da wata; kowannensu yana ninƙaya ciki falakinsa)). (Anbiya: 31-33)

Har ila yau Allah yana cewa:

﴿ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦ خَلْقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَٱخْتِلَٰفُ أَلْسِنَتِكُمْ وَأَلْوَٰنِكُمْ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَأَيَٰتٍ لِّلْعَٰلِمِينَ ۝٢٢ ﴾ [سورة الروم:الآية ٢٢].

Ma'ana: ((Daga cikin ayoyinSa (abubuwan da suke nuna sarautarSa) halittar sammai da ƙassai da kuma sassaɓawar harsunanku da launukanku, haƙiƙa a cikin waɗannan abubuwa da akwai ayoyi ga ma'abota ilimi)). (Rum: 22)

b- Abubuwan da Allah ya aiko manzanninSa da su na daga shari'o'i, da kuma abin da ya ƙarfefe su da shi na daga ayoyi da hujjoji waɗanda suke nuna wahadaniyyarSa da kaɗaitakarSa Maɗaukakin Sarki da ibada, saboda hukunce-hukuncen da Allah ya shar'anta wa halittunSa suna nuna wa a fili cewa babu mai iya irin wannan tsarin sai Ubangiji Mai hikima, Mai cikakken sani game da halittunSa da kuma abin da zai gyara su. Allah Ta'ala ya ce:

﴿ لَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلَنَا بِٱلْبَيِّنَٰتِ وَأَنزَلْنَا مَعَهُمُ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْمِيزَانَ لِيَقُومَ ٱلنَّاسُ بِٱلْقِسْطِ ﴾[سورة الحديد:الآية ٢٥]

Ma'ana: ((HaKiƙa mun aiko manzanninmu da hujjoji, mun saukar da littafi da ma'auni tare da su domin mutane su yi adalci}}

Allah ta'ala ya ce:

﴿ قُل لَّئِنِ ٱجْتَمَعَتِ ٱلْإِنسُ وَٱلْجِنُّ عَلَىٰٓ أَن يَأْتُوا۟ بِمِثْلِ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ لَا يَأْتُونَ بِمِثْلِهِۦ وَلَوْ كَانَ بَعْضُهُمْ لِبَعْضٍ ظَهِيرًا ﴿٨٨﴾ ﴾ [سورة الإسراء:الآية ٨٨].

Ma'ana: ((Ka ce da su (ya kai wannan Manzo) Wallahi idan da mutane da aljanu sun haɗu a kan su kawo kwatankwacin wannan Al-ƙur'ani, da ba su iya kawo kwatankwacin nasa ba, ko da sashinsu yana taimakon sashi)). (Isra'i: 88)

c- Fiɗira (wato ɗabi'ar) da Allah ya halicci zukatan mutane a kanta; inda take tabbatar da kaɗaitakar Allah, wannan kuwa abu ne tabbatacce a cikin rayukan mutane, idan wata masifa ta faɗo kan mutum sai ya samu wannan haƙiƙar a cikin zuciyarsa, sai ya koma wa Allah Ta'ala. Kuma da a ce mutum zai kuɓuta daga shubuhohi (raunanan

hujjoji masu ɓatarwa) da kuma sha'awowin da suke canza masa fiɗira da ba abin da zai samu a cikin ƙoƙon zuciyarsa sai yarda da miƙa wuya ga kaɗaitakar Allah a cikin sarautarSa, sunayenSa, siffofinSa da ayyukanSa, da kuma miƙa wuya ga shari'arSa da ya aiko manzanninSa da ita, Allah ya ƙara musu salati da salami.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ فَأَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفًا ۚ فِطْرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِى فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَا ۚ لَا تَبْدِيلَ لِخَلْقِ ٱللَّهِ ۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلْقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٠﴾ ۞ مُنِيبِينَ إِلَيْهِ وَٱتَّقُوهُ وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَلَا تَكُونُوا۟ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٣١﴾ ﴾ [سورة الروم:الآيتان ٣٠-٣١].

Ma'ana: ((Ka tsayar da fuskarka ga addinin da ya saɓa wa addinan ɓata, (wannan shi ne) halittar Allah da ya halicci mutane a kanta, babu wani canji ga addinin Allah, wannan shi ne addini miƙaƙƙe, sai dai kuma yawaicin mutane ba su san (haka) ba. Ku zama masu komawa zuwa gare Shi (wato Allah) kuma ku ji tsoronSa ku kuma tsai da salla kuma kada ku zamanto cikin mushirikai)). (Rum: 30-31)

Annabi (s.a.w) kuma ya ce:

"كل مولد يولد على الفطرة، فأبواه يهودانه أو ينصرانه أو يمجسانه، كما تنتج البهيمة بهيمة جمعاء، هل تحسون فيها من جدعاء. ثم قرأ ﴿ فِطْرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِى فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَا ۚ ﴾"[ رواه البخاري].

Ma'ana: "Ko wanne ɗa ana haifarsa ne a bisa fiɗira (wato a kan tauhidin da Allah yake halittar zukata da shi) sai dai iyaye su juyar da shi bayahude ko banasare ko bamajushe,

kamar dai yadda tunkiya take haihuwar ɗanta sumul, ko kuna ganin ana haihuwarsu da gutsurarren kunne? Sannan sai ya karanta faɗin Allah ta'ala:

﴿ فِطْرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِى فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَا ۚ ﴾

" Bukhari ne ya ruwaito shi.

# RUKUNI NA BIYU: IMANI DA MALA'IKU

(1) Ma'anar Imani da Mala'iku: Ana nufin tabbataccen ƙuduri kan cewa Allah yana da mala'iku da ya halicce su daga haske, ya kuma ɗabi'antar da su a bisa yi masa ɗa'a; ba sa saɓawa umarninSa kuma suna aikata abin da aka umarce su da shi, suna tsarkake shi (da tasbihi) dare da rana ba sa gajiyawa, babu wanda ya san adadinsu sai Allah, ya kuma ɗora musu aikace-aikace daban-daban.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ وَلَٰكِنَّ ٱلۡبِرَّ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ ﴾ [سورة البقرة: الآية ١٧٧].

Ma'ana: ((Shi bin Allah (yana ga) wanda ya ba da gaskiya da Allah da ranar lahira da mala'iku)). (Baƙara: 177)

Ya kuma cewa:

﴿ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّن رُّسُلِهِۦۚ ﴾ [سورة البقرة: الآية ٢٨٥].

((Kowanne daga cikinsu ya yi imani da Allah da mala'ikunSa da littattafanSa da manzanninSa: ba ma banbance tsakanin ɗaya daga manzanninSa)). (Baƙara: 285)

A shahararren hadisin nan na Jibrilu kuma, yayin da ya tambayi Manzon Allah (s.a.w) game da imani, musulunci da kuma ihsani, sai ya ce:

" الإيمان أن تؤمن بالله، وملائكته، وكتبه، ورسله، واليوم الآخر، وأن تؤمن بالقدر خيره وشره."

"Ba ni labarin menene Imani? Sai ya ce: shi ne ka yi imani da Allah da mala'ikunSa da littattafanSa da manzanninSa da ranar lahira, ka kuma yi imani da ƙaddara; alherinta da kishiyarsa".

**Matsayin Imani da Mala'iku a cikin addini da kuma hukuncinsa:**

Imani da Mala,iku shi ne rukuni na biyu daga cikin rukunan imani guda shida, waɗanda imanin mutum ba ya ingantuwa ba kuma ya karɓuwa sai da su.

Musulmi dukkaninsu sun yi ijma'I a kan wajabcin imani da mala'iku; saboda haka duk wanda ya musunta samuwarsu ko wasu daga cikinsu daga waɗanda Allah Mabuwayi Maɗaukaki ya ambace su, to ya zama kafiri, ya kuma saɓa wa al'ƙur'ani da sunnah da kuma ijma'i.

Allah ta,ala ya ce:

ا وَمَن يَكْفُرْ بِٱللَّهِ وَمَلَـٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَٱلْيَوْمِ ٱلْـَٔاخِرِ فَقَدْ ضَلَّ ضَلَـٰلًۢا بَعِيدًا ﴾ [سورة النساء:الآية ١٣٦]

Ma'ana: ((Wanda ya kafirce wa Allah da mala'ikunSa da littafanSa da manzanninSa da ranar lahira, to ya ɓata ɓacewa mai nisa)). (Nisa': 136)

**Yadda ake imani da Mala'iku:**

Imani da Mala'iku akwai na dunƙule da kuma na dalla-dalla.

a- **Dunƙulallen** ya ƙunshi abubuwa da dama ga wasu daga cikinsu:

1- Na farko: Yarda da samuwarsu, da kuma cewa su wani nau'i ne daga cikin nau'o'in halittun Allah, ya halicce su ne domin su bauta maSa, kuma samuwarsu samuwa ce ta haƙiƙa, rashin ganin mu gare su kuma ba ya nuna rashin

samuwar su; domin da ma ai da akwai abubuwa da dama da ba a ganinsu tare da cewa samammu ne.

Kuma ma ai Annabi (s.a.w) ya ga Jibrilu a surarsa ta haƙiƙa har sau biyu, wasu sahabbai kuma sun ga wasu daga cikin mala'iku a lokacin da suka rikiɗe zuwa siffar 'yan Adam. Kamar yadda Imam Ahmad ya ruwaito a cikin littafinsa "Al-Musnad" daga Abdul Lahi ɗan Mas'ud Allah ya yarda da shi ya ce:

"رأى رسول الله ﷺ جبريل في صورته وله ستمائة جناح، وكل جناح منها قد سدّ الأفق".

"Manzon Allah (s.a.w) ya ga Jibril a surarsa (ta haƙiƙa) yana da fukafukai ɗari shida (600), kowanne ɗaya daga cikinsu ya doɗe sasanni. Ya kuma tabbata a shahararren hadisin Jibrilu wanda Muslim ya ruwaito shi: cewa Jibril ya zo da surar wani mutum mai tsananin farin tufafi mai tsananin baƙin gashi, ba a ganin wata alamar tafiya a tare da shi, kuma babu wanda ya san shi a cikin sahabban da suke wajen.

2- Abu na biyu: Ba su gwargwadon matsayin da Allah ya ba su; domin su bayi ne masu karɓar umarni daga Allah, Allah ya girmama su ya kuma ɗaukaka matsayinsu ya kusantar da su zuwa gare shi, kuma daga cikinsu akwai waɗanda ake aikensu da wahayi ko waninsa, ba su kuma da iko sai abin da Allah ya ba su iko a kansa, amma tare da haka ba sa mallakar wa kansu ko waninsu wani amfani ko cuta koma bayan Allah; saboda haka ba ya halatta a miƙa musu wani nau,i na ibada, balle ma a siffanta su da siffofi irin na Ubangiji, kamar yadda kiristoci suke riyawa game da "Ruhul ƙudsi" wato Jibrila alaihis salam.

Allah ta'ala ya ce:

ا وَقَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱلرَّحۡمَٰنُ وَلَدٗاۗ سُبۡحَٰنَهُۥۚ بَلۡ عِبَادٞ مُّكۡرَمُونَ

(٢٦) لَا يَسۡبِقُونَهُۥ بِٱلۡقَوۡلِ وَهُم بِأَمۡرِهِۦ يَعۡمَلُونَ (٢٧) ﴾ [سورة الأنبياء:الآيتان ٢٦-٢٧].

Ma'ana: ((Suka kuma ce wai Allah ya riƙi ɗa (daga mala'iku), tsarki ya tabbata a gare Shi, a'a bayi ne dai da aka girmama su. Ba sa gabatar Allah a magana, kuma da umarninSa ne ma suke aiki)). (Anbiya': 26-27)

Har ila yau Allah ya ce:

﴿ لَّا يَعۡصُونَ ٱللَّهَ مَآ أَمَرَهُمۡ وَيَفۡعَلُونَ مَا يُؤۡمَرُونَ ﴾

[سورة التحريم:الآية ٦]

Ma'ana: ((Ba sa saɓa wa Allah a umarninSa, suna kuma aikata abin da aka umarce su)). (Tahrim: 6)

Iyaka wannan bayani game da mala'iku wajibi ne kan kowanne musulmi da musulma, su nemi iliminsa su kuma ƙudurce shi, ba su kuma da uzuri idan suka jahilce shi.

**b- Amma imani da mala'iku na dalla-dalla,** to shi ma ya ƙunshi abubuwa daban-daban ga wasu daga cikinsu:

**1- Na farko: Sinadarin halittarsu:**

Allah ta'ala ya halicci mala'iku daga haske, kamar yadda su kuma aljanu an halicce su ne daga wuta, 'yan Adam kuma daga taɓo. Su kuma an halicce su ne kafin a halicci Annabi Adamu alaihis salam.

Ya zo a cikin hadisi:

«خلقت الملائكة من نور، وخلق الجان من مارج من نار، وخلق آدم مما وصف لكم»

رواه مسلم .

"An halicci mala'iku daga haske, aljanu kuma daga tataccen harshen wuta, Adamu kuma daga abin da aka wasafta muku (a ƙur'ani)". Muslim ne ya ruwaito shi.

**2- Na biyu: Adadin Mala'iku:**

Mala'iku babu wanda ya ƙididdige yawansu sai Allah Mabuwayi Maɗaukaki saboda tsabar yawansu; domin kuwa

a sammai babu wurin da za a sanya 'yan yatsu guda huɗu sai ka samu da akwai mala'ika a kan wurin yana sajada ko yana tsaye (cikin aikin Allah), haka nan "Al-Baitul Ma'mur" wato rayayyen ɗaki wanda yake a sama ta bakwai a kullum ta Allah mala'iku dubu saba'in ne suke shiga cikinsa, sannan ba za su ƙara komawa cikinsa ba saboda tsananin yawansu, ranar alƙiyama kuma za a zo da wuta tana da linzami dubu saba'in, kowanne linzami kuma mala'iku dubu saba'in ne suke riƙe da shi suna jan ta. Allah ta'ala ya ce:

ا وَمَا يَعْلَمُ جُنُودَ رَبِّكَ إِلَّا هُوَۚ﴾ [سورة المدثر:الآية ٣١] .

Ma'ana: ((Babu wanda ya san rundunar Ubangijinka sai Shi)). (Muddassir: 31)

Ya zo kuma a cikin hadisi cewa Annabi (s.a.w) ya ce:

"أطَّت السماء وحق أن تَئِطَّ، ما فيها موضع قدم إلا وفيه ملك ساجد وراكع".

"Sama ta nisa, kuma ta cancanci ta nisa; domin babu inda za a iya sa ƙafa a cikinta face da akwai mala'ika a wajen yana mai sajada ko ruku'i". Kuma Annabi (s.a.w) ya ce game da "Baitul Ma'mur":

"يدخله في كل يوم سبعون ألف ملك لا يعودون إليه". [رواه البخاري ومسلم].

"Kullum mala'iku dubu saba'in ne ke shiga cikinsa ba sa taɓa komawa cikinsa". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi. Haka nan Annabi (s.a.w) ya ce:

"يؤتي بجهنم يومئذٍ لها سبعون ألف زمام، مع كل زمام سبعون ألف ملك" [ رواه مسلم ].

"Za a zo da Jahannama a wannan rana tana da linzami

dubu saba'in, kowanne linzami yana da mala'iku dubu saba'in" Muslim ne ya ruwaito shi.

Daga nan ne za mu iya gane girman adadin mala'iku, domin waɗannan kawai alal misali sun kai miliyan dubu huɗu da ɗari tara (4900000000), to ina kuma da sauran mala'ikun! Tsarki ya tabbata ga wanda ya halicce su ya kuma sarrafa su ya kuma ƙididdige adadinsu.

**3- Na uku: Sunayen Mala'iku:**

Ya wajaba a yi imani da mala'ikun da Allah ya ambaci sunayensu gare mu a cikin alƙur'ani, ko kuma manzonSa ya ambata a cikin sunna, mafi girmansu dai guda uku ne:

1- Jibrilu, kuma a kan kira shi: Jibra'il, shi ne kuma "Ruhul ƙudsi" (wato tsarkakken rai) mai sauka da wahayi – abin tsarkake zuciya- bisa manzanni, Allah ya ƙara musu salami.

2- Mika'ilu, a kan kira shi kuma da: Mikal, shi kuma shi ne mai kula da ruwan sama –abin da ke raya ƙasa- sai ya kora shi zuwa ga inda Allah ya umarce shi.

3- Israfilu: Shi kuma an dogara shi ga aikin busa ƙaho ne mai nuna ƙarewar rayuwar duniya da fara rayuwar lahira, shi kuma busa ƙaho da shi ne jikkuna suke rayuwa (bayan mutuwa).

**4- Na huɗu: Siffofin Mala'iku:** Mala'iku ababan halitta ne na haƙiƙa, suna da jukkuna na haƙiƙa masu siffantuwa da kamanni da halaye na musamman, ga wasu daga cikin siffofin nasu:

a- **Girman halitta da manya-manyan jukkuna**: Allah tsarki ya tabbatar masa ya ɗaukaka ya halicci mala'iku da manya-manyan kamanni kuma masu ƙarfi, yadda za ta dace da manya-manyan ayyukan da Allah ya ɗora musu a sammai da ƙassai.

b- **Suna da fuka-fukai**: Allah Subuhanahu ya halitta wa mala'iku fuka-fukai wasu bibiyu, wasu uku-uku, wasu hurhuɗu, wasu ma a kan ƙara musu ya fi haka, kamar yadda

Annabi (s.a.w) ya ga Jibrila alaihis salam a kamarsa ta haƙiƙa sai ya ga yana da fuffuke ɗari shida (600) duk ya rufe masa sararin samaniya. Allah ta'ala ya ce:

﴿ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ جَاعِلِ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا أُو۟لِىٓ أَجْنِحَةٍ مَّثْنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَ ۚ يَزِيدُ فِى ٱلْخَلْقِ مَا يَشَآءُ ۚ ﴾ [سورة فاطر:الآية ١] .

Ma'ana: ((Yabo ya tabbata ga Allah Mahaliccin sammai da ƙassai, Mai sanya mala'iku manzanni masu fuka-fukai bibiyu da masu uku-uku da masu hurhuɗu, ya ƙara abin da yake so a cikin halittar)). (Faɗir: 1)

c- **Rashin buƙatar ci da sha**: Allah -tsarki ya tabbatar masa ya ɗaukaka- ya halicci mala'iku ta yadda ba sa buƙatar abinci ko abin sha, haka nan ba sa aure ba kuma sa haihuwa.

d- **Mala'iku suna da hankali da zukata**: domin mun ga cewa suna yi wa Allah magana, shi ma yana yi musu, kuma sun yi wa Annabi Adamu da ma sauran annabawa magana.

e- **Ikon rikiɗa zuwa kamannin da ba nasu ba**: Allah ya ba wa mala'iku damar kamantuwa da kamannin mazan bil adama, wanda hakan ya ƙunshi raddi ga masu bautar gumaka da suke riya cewa mala'iku 'ya'ya mata ne da Allah ya haifa. Ba mu san yadda suke rikiɗar ba, sai dai mun san cewa suna juye wa ne ta yadda ba a iya gane wani banbanci tsakaninsu da mutanen da suka canzu zuwa kamanninsu.

f- **Mutuwar Mala'iku**: Mala'iku suna mutuwa dukkaninsu ranar alƙiyama, har shi ma kansa mala'ikan mutuwa, sannan kuma sai a tashe su domin su ci gaba da ayyukan da aka dora musu.

g- **Ibadar Mala'iku**: Mala'iku suna bauta wa Allah da ibadoji daban-daban, irin su sallah, addu'a, tasbihi, ruku'u, sajada, da son Allah da tsoronSa da makamantansu.

Daga cikin siffofin ibadojinsu:

1- Dawwama da ci gaba tare da rashin gajiyawa.

2- Ikhlasi ga Allah Subhanahu wa ta'ala.

3- Lazimtar ɗa'a da barin saɓa wa Allah domin su ma'asumai ne wato an katange su ga barin ayyukan zunubai da saɓo.

4- Tawalu'u da ƙanƙan da kai ga Allah tare da yawan bautata masa.

Allah Ta'ala ya ce:

ا يُسَبِّحُونَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ لَا يَفۡتُرُونَ ﴿٢٠﴾ [سورة الأنبياء:الآية ٢٠]

Ma'ana: ((Suna tsarkake Allah dare da rana ba sa gajiyawa)). (Anbiya: 20)

**Na biyar: Ayyukan Mala'iku:**

Mala'iku suna yin wasu manya-manyan ayyuka da Allah ya ɗora musu su, shi ya sa daga cikinsu akwai:

1- Masu ɗaukan al'arshi.

2- Wanda aka wakilta ga saukar da wahayi zuwa ga manzanni.

3- Masu gadin aljanna da wuta.

4- Masu kula da giza-gizai da ruwa da tsiro.

5- Masu kula da duwatsu.

6- Mai aikin busa ƙaho.

7- Masu rubuta ayyukan 'yan Adam.

8- Masu aikin kare 'yan Adam (daga abin da zai cuce shi), sai dai idan abun ƙaddararre ba makawa sai su rabu da shi domin tabbatuwar ƙaddarar a kansa.

9- Masu aikin zama tare da ɗan Adam da kiransa zuwa ga alheri.

10- Masu aikin kula da ruwan asalin halittar bil Adama tun yana mahaifa, haka kuma busa masa rai da rubuta

arzikinsa da aikinsa da kasancewarsa ɗan wuta ne shi ko ɗan aljanna.

11- Masu aikin karɓar ran 'yan Adam lokacin mutuwarsu.

12- Masu tambayar mutane a kabari da abin da ke biyo bayansa na ni'ima ko azaba.

13- Masu kai wa Annabi (s.a.w) saƙon gaisuwar al'ummarsa gare shi. Wannan ya sa musulmi ba ya buƙatar ya shirya tafiya takanas-ta-kano domin zuwa kabarin Annabi, a'a, ya ishe shi ya yi masa salati da sallama daga ko'ina yake; domin waɗannan mala'ikun suna ɗauka da isar da wannan sallamar gare shi, ana takanas-ta-kano ne kurum domin yin salla a masallacin Annabi (s.a.w).

Hakanan mala'iku suna da wasu ayyukan masu yawan gaske, waɗannan dai su ne mafiya shahara daga cikinsu. Daga dalilan da suke bayyana waɗannan ayyuka na su:

Faɗin Allah ta'ala:

﴿ ٱلَّذِينَ يَحۡمِلُونَ ٱلۡعَرۡشَ وَمَنۡ حَوۡلَهُۥ يُسَبِّحُونَ بِحَمۡدِ رَبِّهِمۡ وَيُؤۡمِنُونَ بِهِۦ وَيَسۡتَغۡفِرُونَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ ﴾ [سورة غافر:الآية ٧].

Ma'ana: ((Waɗanda suke ɗauke da al'arshi da waɗanda suke daura da shi suna yin tasbihi da yabon Ubangijinsu suna kuma yin imani da Shi, kuma suna nema wa waɗanda suka yi imani gafara)). (Gafir: 7)

Haka nan Allah ta'ala ya ce:

﴿ قُلۡ مَن كَانَ عَدُوًّا لِّجِبۡرِيلَ فَإِنَّهُۥ نَزَّلَهُۥ عَلَىٰ قَلۡبِكَ بِإِذۡنِ ٱللَّهِ ﴾ [سورة البقرة:الآية ٩٧].

Ma'ana: ((Ka ce (da su) wanda ya kasance maƙiyi ne ga (mala'ika) Jibrila, haƙiƙa shi ne ya saukar da shi (wato Alƙur'ani) a zuciyarka da izinin Allah)). (Baƙara: 97)

A wani gurin kuma Allah cewa ya yi:

﴿ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِى غَمَرَٰتِ ٱلْمَوْتِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ بَاسِطُوٓا۟ أَيْدِيهِمْ أَخْرِجُوٓا۟ أَنفُسَكُمُ ۖ ﴾ [سورة الأنعام:الآية ٩٣].

Ma'ana: ((Da za ka ga lokacin da kafirai suke cikin magagin mutuwa, mala'iku kuma suna miƙa hannayensu (suna cewa da su): "Ku fito da rayukanku .."')). (An'am: 93)

**Na shida: Haƙƙoƙin Mala'iku a kan 'yan Adam:**

a- Imani da su.

b- Sonsu da girmama su da ambaton falalarsu.

c- Haramta zaginsu ko tawayarsu ko yin izgili da su.

d- Nisantar abin da suke ƙi; domin su ma suna cutuwa da abin da 'yan Adam suke cutuwa da shi.

**Fa'idojin imani da Mala'iku:**

a- Samuwar imani; domin imani ba ya ingantuwa sai tare da imani da su.

b- Sanin girman Mahaliccinsu tabaraka wa ta'ala da sanin ƙarfinSa da isarSa; domin girman abin halitta yana nuna girman mahaliccinsa.

c- Karuwar imani a cikin zuciyar musulmi ta hanyar sanin siffofinsu da halayensu da ayyukansu.

d- Amintuwa da nutsuwar zuciyar muminai yayin da Allah ya ƙarfafi gwiwarsu da mala'ikunSa.

e- Son mala'iku saboda bauta wa Allah da suke yi sosai da gaske, da kuma nema wa muminai gafara da suke yi.

f- Kin munanan ayyuka da saɓo.

g- Gode wa Allah Subhanahu a kan kula wa da bayinSa da yake yi; domin yadda yake wakilta musu mala'ikun da suke kula da su da rubuta ayyukansu da dai sauran kula da masalahohinsu.

# RUKUNI NA UKU: IMANI DA LITTATTAFAI

Imani da littattafan da Allah ya saukar wa annabawanSa, salati da salaminSa su ƙara tabbata a gare su, shi ne rukuni na uku daga rukunan imani. Allah ta'ala ya aiko manzanninSa da hujjoji, ya kuma saukar musu da littattafai domin rahama da jin ƙai ga halittu, kuma domin shiryar da su zuwa ga samun jin daɗin duniya da na lahira, haka nan domin waɗannan littattafan su zamanto musu tafarki da za su tafiyar da rayuwarsu a kansa, kuma su zamanto alƙalai tsakaninsu a cikin abubuwan da sukan iya saɓawa a kansu. Allah Ta'ala ya ce:

﴿لَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلَنَا بِٱلْبَيِّنَٰتِ وَأَنزَلْنَا مَعَهُمُ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْمِيزَانَ لِيَقُومَ ٱلنَّاسُ بِٱلْقِسْطِ﴾ [سورة الحديد:الآية ٢٥].

Ma'ana: ((Haƙiƙa mun aiko manzanninmu da hujjoji mabayyana, Muka kuma saukar da littattafai da ma'auni a tare da su don mutane su tsayar da adalci)). (Hadid: 25).

Kuma Allah Ta'ala yana cewa:

﴿كَانَ ٱلنَّاسُ أُمَّةً وَٰحِدَةً فَبَعَثَ ٱللَّهُ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ وَأَنزَلَ مَعَهُمُ ٱلْكِتَٰبَ بِٱلْحَقِّ لِيَحْكُمَ بَيْنَ ٱلنَّاسِ فِيمَا ٱخْتَلَفُوا۟ فِيهِ﴾ [سورة البقرة:الآية ٢١]

Ma'ana ((Da can mutane sun kasance al'umma ɗaya (a kan addini ɗaya) sai Allah ya aiko annabawa masu albishir (da Aljanna) kuma masu gargaɗi (da wuta) ya kuma saukar da littattafai tare da su (suna ɗauke) da gaskiya don su yi hukunci a tsakanin mutane game da abin da suka yi saɓani

a cikinsa)). (Bakara:213)

**(1) Haƙiƙanin imani da littattafan Allah:**

Imani da littafi shi ne: cikakkiyar gaskatawa da cewa Allah yana da littattafai waɗanda ya saukar da su ga manzanninSa (s.a.w), kuma su waɗannan littattafan zancen Allah ne na haƙiƙa, kuma su haske ne da shiriya, kuma abin da suka ƙunsa gaskiya ne da kuma adalci, ya kuma wajaba a bi su a kuma yi aiki da abin da yake cikinsu, kamar yadda babu wanda ya san adadin su sai Allah.

Allah ta'ala ya ce:

ا وَكَلَّمَ ٱللَّهُ مُوسَىٰ تَكۡلِيمٗا ﴾ [سورة النساء:الآية ١٦٤].

Ma'ana: ((Allah ya yi wa Annabi Musa magana kai tsaye)). (Nisa'i: 164)

Ya kuma cewa:

ا وَإِنۡ أَحَدٞ مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ٱسۡتَجَارَكَ فَأَجِرۡهُ حَتَّىٰ يَسۡمَعَ كَلَٰمَ ٱللَّهِ ﴾ [سورة التوبة:الآية ٦]

Ma'ana: ((Idan wani mushiriki ya nemi mafaka a wajenka to sai ka ba shi har ya samu damar jin zancen Allah)). (Tauba: 6)

**(2) Hukuncin imani da littattafan Allah:**

Ya wajaba a yi imani da dukkanin littattafan da Allah ya saukar wa manzanninSa, Allah ya ƙara musu salati da salami, da kuma cewa Shi ne ya yi furuci da su furuci na gaske kuma ya saukar da su, ba wai ababan halitta ba ne. Duk wanda ya musunta littattafan Allah ko ya musunta wasu daga cikinsu to ya zama kafiri.

Allah ta'ala ya ce:

ا يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِي

نَزَّلَ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَٱلْكِتَـٰبِ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ مِن قَبْلُ ۚ وَمَن يَكْفُرْ بِٱللَّهِ وَمَلَـٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَٱلْيَوْمِ ٱلْـَٔاخِرِ فَقَدْ ضَلَّ ضَلَـٰلًۢا بَعِيدًا ﴿١٣٦﴾ [سورة النساء:الآية ١٣٦].

Ma'ana: ((Ya ku muminai , ku yi imani da Allah da ManzonSa da littafin da ya saukar wa ManzonSa, da littattafan da ya saukar tun da can. Wanda kuwa ya kafirce wa Allah da mala'ikunSa da littattafansa da manzanninSa da ranar lahira to haƙiƙa ya ɓace manisanciyar ɓacewa)). (Nisa'i: 136)

Haka nan Allah ya ƙara cewa:

﴿ وَهَـٰذَا كِتَـٰبٌ أَنزَلْنَـٰهُ مُبَارَكٌ فَٱتَّبِعُوهُ وَٱتَّقُوا۟ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ﴿١٥٥﴾ [سورة الأنعام:الآية ١٥٥]

Ma'ana: ((Wannan kuwa (wato alƙur'ani) littafi ne da Muka saukar da shi , mai albarka, sai ku bi shi, kuma ku ji tsoron (Allah) domin ko a ji ƙanku). (An'am: 155)

**(3) Buƙatuwar mutane ga saukar da littattafai da bayanin hikimar saukar da su:**

- Na farko dai: Domin littafin da aka saukar wa kowanne annabi ya zamanto shi ne madogarar al'ummarsa (wajen gane addini); sai su koma masa domin fahimtar addininsu.
- Na biyu: Domin littafin kowanne annabi ya zamanto shi ne alƙalin gaskiya mai raba duk wani saɓani da ke iya faruwa a cikin al'ummarsa.
- Na uku: Domin littafin ya zamanto mai kiyaye addini bayan mutuwar annabin da ya zo da shi, komin nisan guri da kuma zamani, kamar dai abin da ke faruwa a da'awar Annabinmu Muhammadu (s.a.w).

- Na huɗu: Domin waɗannan littattafai su zamanto yanke hanzari ne ga dukkanin halittun Allah, ba su da damar saɓa musu ko tsallake su. Allah ta'ala ya ce:

ا كَانَ ٱلنَّاسُ أُمَّةً وَٰحِدَةً فَبَعَثَ ٱللَّهُ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ

وَأَنزَلَ مَعَهُمُ ٱلْكِتَـٰبَ بِٱلْحَقِّ لِيَحْكُمَ بَيْنَ ٱلنَّاسِ فِيمَا ٱخْتَلَفُوا۟ فِيهِ ۚ

﴾ [سورة البقرة:الآية ٢١]

Ma'ana ((Da can mutane sun kasance al'umma ɗaya (a kan addini ɗaya) sai Allah ya aiko annabawa masu albishir (da Aljanna) kuma masu gargaɗi (da wuta) ya kuma saukar da littattafai tare da su (suna ɗauke) da gaskiya don su yi hukunci a tsakanin mutane game da abin da suka yi saɓani a cikinsa)). (Bakara:213)

**(4) Yadda imani da Littattafan Allah ya ke:**

Imani da littattafan Allah akwai na dunƙule akwai kuma na dalla-dalla.

Dunƙulallen imani da littattafan Allah shi ne ka yi imani da cewa Allah ya saukar wa da manzanninSa (s.a.w) littattafai.

Shi kuwa dalla-dallan; shi ne ka yi imani da littattafan da Allah ya ambata cikin Alƙur'ani mai girma, wanda daga cikinsu mun san Alƙur'ani, Attaura, Zabura, Injila da kuma Takardun Ibrahim da Musa, sai kuma ka yi imani da cewa Allah yana da wasu littafan daban da ya saukar wa annabawanSa, babu wanda ya san sunayensu da adadinsu sai Allan da ya saukar da su tsarki ya tabbatar masa ya ɗaukaka.

Waɗannan littattafai kuwa dukkaninsu sun zo ne domin tabbatar da tauhidin Allah; a kaɗaita shi da bauta, da kuma umarni da ayyuka na gari da hana yin shirka da ɓarna a

bayan ƙasa, saboda haka za mu gane cewa asalin da'awar annabawa iri ɗaya ce, ko da dai sun saɓa a shari'o'i da hukunce-hukunce.

Imani da littattafan da suka gabata shi ne ka yi yarda da cewa an saukar wa manzannin nan magabata su. Shi kuwa Alƙur'ani imani da shi yana nufin yarda da shi da kuma biyayya ga abin da ya zo a cikinsa.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مِن رَّبِّهِۦ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ ﴾ [سورة البقرة:الآية ٢٨٥].

Ma'ana: ((Manzo ya yi imani da abin da aka saukar masa da shi daga Ubangijinsa, haka ma muminai; kowanne ya yi imani da da Allah da mala'ikunSa da littattafanSa da manzanninSa)). (Baƙara: 285)

Har ila yau Allah ta'ala ya ce:

﴿ ٱتَّبِعُواْ مَآ أُنزِلَ إِلَيۡكُم مِّن رَّبِّكُمۡ وَلَا تَتَّبِعُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَۗ ﴾ [سورة الأعراف:الآية ٣].

Ma'ana: ((Ku bi abin da aka saukar muku daga Ubangijiku, kada kuma ku riƙi wasu iyayen giji ba Shi ba)). (A'raf: 3)

Alƙur'ani yana da fifiko a kan sauran littattafan da suka gabace shi ta fuskoki daban-daban, mafi muhimmanci daga cikinsu:

1- Cewa shi mu'jiza ne; ta fuskar lafazinsa da ma'anoninsa da kuma abin da ke cikinsa na daga tabbatattun ilimummukan kimiyya da nazarin halittu.

2- Cewa shi ne littafi na ƙarshe da aka saukar daga sama; saboda haka an rufe littattafai da shi, kamar yadda

aka rufe manzanci da Annabinmu Muhammad (s.a.w).

3- Allah ya yi alƙawarin kare shi daga duk wata karkatarwa ko canzawa, saɓanin sauran littafan da suka gabace shi, su kam amma rigaya an karkatar da su an caccanza su.

4- Alƙur'ani yana gaskata dukkanin littattafan da suka gabace shi kuma yana shaida a gare su.

5- Yana shafe (hukunce-hukuncen) dukkanin littafan da suka wuce.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

ا مَا كَانَ حَدِيثًا يُفْتَرَىٰ وَلَٰكِن تَصْدِيقَ ٱلَّذِى بَيْنَ يَدَيْهِ وَتَفْصِيلَ كُلِّ شَىْءٍ وَهُدًى وَرَحْمَةً لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴾ [سورة يوسف:الآية ١١١]

Ma'ana: (( (Alƙur'ani) bai zamanto zance ne da ake ƙirƙirarsa ba, sai dai zance ne da yake gaskata abin da ya rigaye shi (na littattafai), da kuma bayanin komai; shiriya ne kuma da rahama ga mutanen da suke yin imani)). (Yusuf: 111)

**(5) Karɓar labaran tsofaffin littattafan Allah:**

Mun sani tabbas cewa abin da ya zo cikin waɗancan littattafai na daga labaran da Allah ya aiko wa manzanninSa gaskiya ne babu kokwanto a cikinsu.

Amma wannan ba ya nufin cewa mu karɓi duk abin da yake cikin waɗannan littattafan da ke hannun su ma'abota littattafan na yanzu; domin kuwa an caccanza su an baddala su, a yanzu ba sa kan zubin da Allah ya saukar da su ga manzanninSa, salati da salamin Allah su ƙara tabbata a gare su.

Daga cikin abubuwan da muka sansu na cikin waɗancan littattafai tabbataccen sani; abin da Allah ya ba mu

labarinsu a cikin Alƙur'ani cewa wata rai ba ta ɗaukan nauyin wata, kuma mutum ba shi da wani rabo sai abin da ya aikata, kuma da sannu za a duba aikinsa, sannan a yi masa cikakken sakamako kan abin da ya aikata.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ أَمۡ لَمۡ يُنَبَّأۡ بِمَا فِي صُحُفِ مُوسَىٰ ٣٦ وَإِبۡرَٰهِيمَ ٱلَّذِي وَفَّىٰٓ ٣٧ أَلَّا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰ ٣٨ وَأَن لَّيۡسَ لِلۡإِنسَٰنِ إِلَّا مَا سَعَىٰ ٣٩ وَأَنَّ سَعۡيَهُۥ سَوۡفَ يُرَىٰ ٤٠ ثُمَّ يُجۡزَىٰهُ ٱلۡجَزَآءَ ٱلۡأَوۡفَىٰ ٤١ ﴾ [سورة النجم:الآيات ٣٦-٤١].

Ma'ana: ((Ko ba a ba shi labarin abin da yake takardun (Annabi) Musa ba ne? Da (Annabi) Ibrahimu wannan da ya cika (umarce-umarcen Allah); cewa wani ba ya ɗaukar laifin wani. Kuma mutum ba shi da wani abu sai abin da ya aikata. Kuma haƙiƙa da sannu za a duba aikin nasa, sannan a yi masa cikakken sakamako)). (Najm: 36-41)

A wani wajen kuma Allah cewa ya yi:

﴿ بَلۡ تُؤۡثِرُونَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا ١٦ وَٱلۡأٓخِرَةُ خَيۡرٞ وَأَبۡقَىٰٓ ١٧ إِنَّ هَٰذَا لَفِي ٱلصُّحُفِ ٱلۡأُولَىٰ ١٨ صُحُفِ إِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ ١٩ ﴾

[سورة الأعلى، الآيات:١٦-١٩].

Ma'ana: ((Kai! Ku dai kuna fifita rayuwar duniya, lahira kuwa ita ta fi alheri da wanzuwa. Haƙiƙa wannan (batu) lallai yana cikin takardun farko. Takardun Ibarhimu da Musa)). (A'la: 16-19)

Game da hukunce-hukuncensu kuwa; to abin da Al-ƙur'ani ya zo mana da shi ya wajaba mu bauta wa Allah da aikata shi, saɓanin abin da ya ke cikin waɗancan tsofaffin

littattafan, shi kam sai an duba an yi nazari, in ya saɓa da abin da yake cikin Alƙur'ani to ba za mu yi aiki da shi ba; ba wai don ƙarya ba ne, a'a shi ma a zamaninsa gaskiya ne kuma daidai ne, amma duk da haka ba ya lazimtar mu mu yi aiki da shi, saboda shari'ar mu ta shafe shi, wanda kuma ya dace da shari'armu to wannan daidai yake da mu yi aiki da shi saboda shari'armu ta yi nuni ga hakan.

**(6) Littattafan da aka ambata cikin Al-ƙur'ani da Sunnah:**

1- ALKUR'ANI MAI GIRMA:

Shi ne maganar Allah da ya saukar wa Muhammadu (s.a.w) cikamakin manzanni da annabawa, sai ya zamanto shi ne littafi na ƙarshe da aka saukar, kuma Allah ya yi alƙawarin kare shi daga canzawa da gurɓatawa, ya kuma sanya shi mai shafewa ga sauran littattafan da suka riga shi. Allah ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا ٱلذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ۝٩ ﴾ [سورة الحجر:الآية ٩].

Ma'ana: ((Haƙiƙa Mu Mu ne Muka saukar da Alƙur'ani kuma a haƙiƙa Mu Mu ne masu kiyaye shi)). (Hijir: 9)

Allah ya ƙara cewa:

﴿ وَأَنزَلْنَآ إِلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ بِٱلْحَقِّ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلْكِتَٰبِ وَمُهَيْمِنًا عَلَيْهِ ۖ فَٱحْكُم بَيْنَهُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ ۖ ﴾ [سورة المائدة: الآية ٤٨].

Ma'ana: ((Mun saukar maka da littafi (ya Muhammadu) da gaskiya, mai gaskata abin da yake gabaninsa na littattafai, mai kuma yin shaida a gare su; saboda haka ka yi hukunci a tsakaninsu da abin da Allah ya saukar)). (Ma'ida: 48)

2- ATTAURA:

Shi ne littafin da Allah ya saukar wa Annabi Musa, salamin Allah ta ƙara tabbata a gare shi, ya kuma sanya shi shiriya da haske, (domin) annabawa da malaman banu isra'ila su yi musu hukunci da shi.

Attaurar da ya wajaba a yi imani da ita ita ce wacce Allah ya saukar wa Annabi Musa (s.a.w), ba wacce aka gurɓata aka caccanza ba, wacce yanzu ita ce a hannun mazowa littafi. Allah ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّآ أَنزَلۡنَا ٱلتَّوۡرَىٰةَ فِيهَا هُدٗى وَنُورٞۚ يَحۡكُمُ بِهَا ٱلنَّبِيُّونَ ٱلَّذِينَ أَسۡلَمُواْ لِلَّذِينَ هَادُواْ وَٱلرَّبَّٰنِيُّونَ وَٱلۡأَحۡبَارُ بِمَا ٱسۡتُحۡفِظُواْ مِن كِتَٰبِ ٱللَّهِ ...﴾ [سورة المائدة، الآية: ٤٤].

Ma'ana: ((Haƙiƙa mun saukar da Attaura, a cikinta da akwai shiriya da haske, annabawa da suka miƙa wuya (ga Allah) suna hukuncin da ita ga yahudawa, haka ma malamai masu tarbiyyar (mutane) da manya-manyan malamai, (suna yin hakan) saboda abin da aka ba su amanarsa na daga littafin Allah ..)). (Ma'ida: 44)

3- INJILA:

Shi ne littafin da Allah ya saukar wa Isa (s.a.w) da gaskiya, mai gaskatawa ga saukakkun littafan da suka gabace shi.

Injilar da ya wajaba a yi imani da shi shi ne littafin da Allah ya saukar wa Isa (s.a.w) na asali, ba injilolin da aka caccanza ba, waɗanda yanzu su ne suke a hannun mazowa littafi. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَقَفَّيۡنَا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم بِعِيسَى ٱبۡنِ مَرۡيَمَ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ

يَدَيۡهِ مِنَ ٱلتَّوۡرَىٰةِۖ وَءَاتَيۡنَٰهُ ٱلۡإِنجِيلَ فِيهِ هُدٗى وَنُورٞ وَمُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِ مِنَ ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَهُدٗى وَمَوۡعِظَةٗ لِّلۡمُتَّقِينَ ﴿٤٦﴾ ﴾ [سورة المائدة، الآية:٤٦].

Ma'ana: ((Muka kuma biyo da Isa ɗan Maryamu a bayansu (wato annabawa) yana mai gaskata abin da ya gabace shi na Attaura, muka kuma ba shi Injila, a cikinta akwai shiriya da haske, kuma tana mai gaskata abin da yake gabaninta na Attaura, kuma shiriya ce da wa'azi ga masu tsoron (Allah) )). (Ma'ida: 46)

Daga cikin abin da Attaura da Injila suka ƙunsa yin albishir da manzancin Annabinmu Muhammadu (s.a.w). Allah ya ce:

﴿ ٱلَّذِينَ يَتَّبِعُونَ ٱلرَّسُولَ ٱلنَّبِيَّ ٱلۡأُمِّيَّ ٱلَّذِي يَجِدُونَهُۥ مَكۡتُوبًا عِندَهُمۡ فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَٱلۡإِنجِيلِ يَأۡمُرُهُم بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَىٰهُمۡ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَيُحِلُّ لَهُمُ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَيُحَرِّمُ عَلَيۡهِمُ ٱلۡخَبَٰٓئِثَ وَيَضَعُ عَنۡهُمۡ إِصۡرَهُمۡ وَٱلۡأَغۡلَٰلَ ٱلَّتِي كَانَتۡ عَلَيۡهِمۡۚ ... ﴾ [سورة الأعراف، الآية:١٥٧].

Ma'ana: (( (Su ne) waɗanda suke bin Manzo Annabi Ummiyi (wanda ba ya karatu ko rubutu) wanda kuma suke da shi a rubuce a gurinsu cikin Attaura da Injila, yana umartarsu da alheri yana kuma hana su ga yin mummunan aiki, yana kuma halatta musu tsarkakan abubuwa yana haramta musu najasu, yana kuma sauke musu nauyaye-nauyayen da ke kansu da huƙumce-huƙumcen da aka ɗora su a kansu..)). (A'raf:157)

4- ZABURA:

Shi ne littafin da Allah ya saukar wa Annabi Dawuda (s.a.w). Zaburar da ya wajaba a yi imani da ita ita ce wacce Allah ya saukar wa Annabi Dawuda (s.a.w) ba wacce Yahudawa suka gurɓata kuma suka caccanza ba. Allah ta'ala ya ce:

﴿ ... وَءَاتَيْنَا دَاوُۥدَ زَبُورًا ﴿١٦٣﴾ ﴾ [سورة النساء، الآية:١٦٣].

Ma'ana: ((.. Mun kuma ba wa Dawuda Zabura)). (Nisa'i: 163)

5- TAKADDUN IBRAHIMU DA MUSA

Su ne takardun da Allah ya ba wa Ibrahim da Musa su, amma yanzu waɗannan takardu babu su, ba a san komai ba game da su, sai abin da Alƙur'ani da Sunna suka faɗi a kan su. Allah ta'ala ya ce:

﴿ أَمْ لَمْ يُنَبَّأْ بِمَا فِى صُحُفِ مُوسَىٰ ﴿٣٦﴾ وَإِبْرَٰهِيمَ ٱلَّذِى وَفَّىٰٓ ﴿٣٧﴾ أَلَّا تَزِرُ وَازِرَةٌ وِزْرَ أُخْرَىٰ ﴿٣٨﴾ وَأَن لَّيْسَ لِلْإِنسَٰنِ إِلَّا مَا سَعَىٰ ﴿٣٩﴾ وَأَنَّ سَعْيَهُۥ سَوْفَ يُرَىٰ ﴿٤٠﴾ ثُمَّ يُجْزَىٰهُ ٱلْجَزَآءَ ٱلْأَوْفَىٰ ﴿٤١﴾ ﴾

[سورة النجم، الآيات:٣٦-٤١].

Ma'ana: ((((Ko ba a ba shi labarin abin da yake littattafan Musa ba ne da Ibrahimu wannan da ya cika (umarce-umarcen Allah); cewa wani ba ya ɗaukar laifin wani. Kuma mutum ba shi da wani abu sai abin da ya aikata. Kuma haƙiƙa da sannu za a duba aikin nasa, sannan a yi masa cikakken sakamako)). (Najm: 36-41)

Haka nan Allah ta'ala ya ce:

﴿ بَلْ تُؤْثِرُونَ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا ﴿١٦﴾ وَٱلْءَاخِرَةُ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰٓ ﴿١٧﴾ إِنَّ

﴿ هَٰذَا لَفِي ٱلصُّحُفِ ٱلۡأُولَىٰ ١٨ صُحُفِ إِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ ١٩ ﴾

[سورة الأعلى، الآيات:١٦-١٩].

Ma'ana: ((Kai! Ku dai kuna fifita rayuwar duniya, lahira kuwa ita ta fi alheri da wanzuwa. Haƙiƙa wannan (batu) lallai yana cikin littattafan farko. Takardun Ibarhimu da Musa)). (A'la: 16-19)

# RUKUNI NA HUƊU: IMANI DA MANZANNI

(1) **Imani da Manzanni** tsira da amincin Allah su tabbata a gare su shi ne ɗaya daga cikin rukunan imani wanda imanin mutum ba ya inganta sai ya yi imani da shi.

Abin da ake nufi da imani da Manzanni kuwa shi ne tabbataccen ƙudurin cewa Allah yana da wasu manzanni ('yan aike) da ya zaɓe su domin su isar da saƙonninSa, saboda haka wanda ya bi su ya shiriya, wanda kuma ya saɓa musu to haƙiƙa ya taɓe, a kuma ƙudurce cewa sun isar da abin da Allah ya saukar musu cikakkiyar isarwa, sun ba da amana, haka nan sun yi nasiha ga al'umma, kuma sun yi jihadi a tafarkin Allah haƙiƙanin jihadi, sun tsayar da hujja, ba su canza ko su baddala ko su ɓoye wani abu daga abubuwan da aka aiko su da shi ba. Mun yi imani da waɗanda Allah ya ambaci sunayensu da ma waɗanda bai ambaci sunayen nasu ba, kuma kowanne manzo yana albishir da wanda zai biyo bayansa, na baya kuma daga cikinsu duka suna gaskata na gaba da su.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ قُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَمَآ أُنزِلَ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَمَآ أُوتِيَ ٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمۡ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّنۡهُمۡ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ١٣٦ ﴾ [سورة البقرة، الآية:١٣٦].

Ma'ana: (( (Ku muminai) ku ce (da su): "Mun yi imani da Allah da kuma abin da aka saukar mana da kuma abin da aka saukar wa Ibrahimu da Isma'ila da Ishaƙa da Yakubu da

jikokinsa, da abin da aka bai wa Musa da Isa, da abin da aka kawo wa annabawa daga Ubangijinsu. Ba ma bambanta wa tsakanin ɗaya daga cikinsu, mu kuma masu miƙa wuya ne gare shi" )). (Baƙara: 136)

Saboda haka wanda duk ya ƙaryata wani manzo to ya ƙaryata wanda ya gaskata shi, wanda kuma ya saɓa wa wani daga cikinsu to ya saɓa wa wanda ya yi umarni da biyayya gare shi. Allah ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكۡفُرُونَ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَيُرِيدُونَ أَن يُفَرِّقُواْ بَيۡنَ ٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَيَقُولُونَ نُؤۡمِنُ بِبَعۡضٖ وَنَكۡفُرُ بِبَعۡضٖ وَيُرِيدُونَ أَن يَتَّخِذُواْ بَيۡنَ ذَٰلِكَ سَبِيلًا ۝١٥٠ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡكَٰفِرُونَ حَقّٗاۚ وَأَعۡتَدۡنَا لِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابٗا مُّهِينٗا ۝١٥١ ﴾ [سورة النساء، الآيتان: ١٥٠ ، ١٥١].

Ma'ana: ((Haƙiƙa waɗanda suke kafirce wa Allah da kuma manzanninSa, suke kuma son su bambanta tsakanin Allah da manzanninsa suke kuma cewa: "Mun yi imani da wasu mun kuma kafirce wa wasu" suna kuma son su sami wata hanya a tsakanin waɗanan (watau imani da kafirci). Waɗancan su ne kafirai tsantsa. Mun kuma tanadi azaba ta wulaƙanci don kafirai)). (Nisa'I 150-151)

**(2) Haƙiƙanin Ma'anar Annabta:**

Annabta: tsani ne tsakanin mahalicci da halittunSa domin isar da shari'arSa, yana yin baiwar wannan matsayi (na tsanantaka) ne ga wanda ya so daga cikin bayinSa, kuma zaɓa yake yi daga cikin halittunSa, zaɓe ne nasa -Sarkin tsarki da ɗaukaka- ba na wani ba. Allah ta'ala ya ce:

﴿ ٱللَّهُ يَصۡطَفِي مِنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلٗا وَمِنَ ٱلنَّاسِۚ إِنَّ ٱللَّهَ

سَمِيعُۢ بَصِيرٌ ﴿٧٥﴾ [سورة الحج، الآية:٧٥].

Ma'ana: ((Allah yana zaɓar manzanni daga mala'iku haka kuma daga mutane, haƙiƙa Allah Jiyau ne kuma Ganau)). (Hajj: 75)

Kuma annabta baiwa ce ba nemanta ake ba, ba a samunta don yawan ibada ko ɗa'a ga Allah, ba kuma zaɓin shi wanda aka ba wa annabtar ba ne ko nemansa, sai dai kurum zaɓe ne da darjewa daga Allah Mabuwayi Maɗaukaki. Allah ta'ala ya ce:

﴿... ٱللَّهُ يَجْتَبِىٓ إِلَيْهِ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِىٓ إِلَيْهِ مَن يُنِيبُ ﴿١٣﴾﴾

[سورة الشورى، الآية:١٣].

Ma'ana: ((Allah yana zaɓar wa kanSa wanda ya so, yana kuma shiryar da wanda yake komawa gare shi)). (Shura: 13)

### (3) Hikimar aiko manzanni:

Hikimar Allah wajen aiko manzanni tana bayyanuwa a cikin abubuwa masu zuwa:

- Na ɗaya: Tsamo mutane daga bautar 'yan uwansu mutane zuwa bautar Ubagijin mutane, haka kuma tsamo su daga ƙangin bautar ababan halitta zuwa 'yancin da ke cikin bautar Ubangijin halittu. Allah ta'ala ya ce:

﴿وَمَآ أَرْسَلْنَـٰكَ إِلَّا رَحْمَةً لِّلْعَـٰلَمِينَ ﴿١٠٧﴾﴾ [سورة الأنبياء، الآية:١٠٧].

Ma'ana: ((Ba mu kuwa aiko ka ba sai don rahama ga talikai)). (Anbiya: 107)

- Na biyu: Sanar da mutane manufa da hikimar da ta sa aka halicce su, wacce ita ce bautar Allah Subhanahu da kaɗaita shi, kuma wannan abu ne da ba za a iya saninsa ba

sai ta hanyar manzannin da Allah ya zaɓe su daga cikin halittunSa ya kuma fifita su a kan sauran halittu. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَلَقَدْ بَعَثْنَا فِي كُلِّ أُمَّةٍ رَّسُولًا أَنِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ وَٱجْتَنِبُوا۟ ٱلطَّٰغُوتَ... ﴾ [سورة النحل، الآية:٣٦].

Ma'ana: ((Haƙiƙa mun aiko manzo a cikin kowacce al'umma (da) cewa "Ku bauta wa Allah, kuma ku nisanci Ɗagutu (wato shaiɗan, gumaka, shuwagabanni masu ƙirƙiro dokoki)…)). (Nahli: 36)

Na uku: Tsayar da hujja kan mutane (yanke hanzari) da aiko musu manzanni:

Allah ta'ala ya ce:

﴿ رُّسُلًا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةٌۢ بَعْدَ ٱلرُّسُلِ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿١٦٥﴾ ﴾ [سورة النساء، الآية:١٦٥].

Ma'ana: ((Manzanni ne masu albishir (ga muminai masu kuma) gargaɗi ga kafirai don kada mutane su sami wata hujja a gun Allah bayan (aiko) manzanni. Allah kuwa ya kasance Mabuwayi ne Gwani)). (Nisa'i: 165)

- Na huɗu: Bayanin wasu ɓoyayyun abubuwa da mutane ba za su gano su da zurfin hankulansu ba, misalin sunayen Allah da siffofinSa, sanin mala'iku da ranar lahira da makamantansu.

- Na biyar: Domin su manzannin su zama ababan koyi na gari, Allah ya kammala su da kyawawan ɗabi'u ya kuma kiyaye su daga shubuhohi (dalilan ƙarya masu ɓatarwa) da sha'awowi. Allah ta'ala ya ce:

﴿ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ هَدَى ٱللَّهُ ۖ فَبِهُدَىٰهُمُ ٱقْتَدِهْ ۗ ... ﴾ [سورة الأنعام،

الآية: ٩٠].

Ma'ana: ((Waɗannan su ne waɗanda Muka bai wa littattafai da hukunci da kuma Annabta. Sai ku yi koyi da irin shiriyarsu)). (An'am: 90)

Allah ya ƙara cewa:

﴿ لَقَدْ كَانَ لَكُمْ فِيهِمْ أُسْوَةٌ حَسَنَةٌ...﴾ [سورة الممتحنة، الآية:٦].

Ma'ana: ((Haƙiƙa kyakkyawan abin koyi a gareku ya tabbata a cikin (lamarinsu) )). (Mumtahana: 6)

- Na shida: Gyara zukata da tsaftace su da tsarkake su da tsoratar da ma'abotansu daga faɗawa cikin duk wani abu da zai halakar da su. Allah ta'ala cewa ya yi:

﴿ هُوَ ٱلَّذِى بَعَثَ فِى ٱلْأُمِّيِّـۧنَ رَسُولًا مِّنْهُمْ يَتْلُواْ عَلَيْهِمْ ءَايَـٰتِهِۦ وَيُزَكِّيهِمْ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلْكِتَـٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ...﴾ [سورة الجمعة، الآية:٢].

Ma'ana: ((Shi ne wanda ya aiko Manzo cikin mutanen da ba sa karatu ko rubutu, (ya aiko shi) daga cikinsu, yana karanta musu ayoyinSa yana kuma tsarkake su, kuma yana sanar da su littafi da hikima…)) (Jumu'a: 2).

Annabi (s.a.w) kuma cewa ya yi:

"إنما بعثت لأتمم مكارم الأخلاق." [ رواه أحمد والحاكم ].

Ma'ana: ((An aiko ni ne domin in cika ɗabi'un girma da mutunci)). Ahmad da Hakim suka ruwaito shi.

**(4) Ayyukan Manzannin Allah ya ƙara yi musu salami:**

Manzanni (a.s) suna da ayyuka masu daraja da ƙima:

a- Isar da shari'a da kiran mutane zuwa ga bautar Allah shi shi kaɗai, da rabuwa da bautar komai da ba shi ba. Allah ta'ala ya ce:

﴿ ٱلَّذِينَ يُبَلِّغُونَ رِسَـٰلَـٰتِ ٱللَّهِ وَيَخْشَوْنَهُۥ وَلَا يَخْشَوْنَ أَحَدًا إِلَّا

ٱللَّهَۗ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ حَسِيبٗا ﴿٣٩﴾ [سورة الأحزاب، الآية:٣٩].

Ma'ana: ((Waɗanda suke isar da saƙon Allah suke kuma tsoronSa, basa kuma tsoron kowa sai Allah. Allah kuma ya isa mai yin hisabi)). (Ahzab: 39).

b- Bayyana abin da aka saukar na addini da shari'a. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلذِّكۡرَ لِتُبَيِّنَ لِلنَّاسِ مَا نُزِّلَ إِلَيۡهِمۡ وَلَعَلَّهُمۡ يَتَفَكَّرُونَ ﴿٤٤﴾ ﴾ [سورة النحل، الآية:٤٤].

Ma'ana: ((Mun kuma saukar maka da Alƙur'ani don ka bayyana wa mutane abin da aka saukar musu kuma domin ko sa yi tunani)). (Nahl: 44)

c- Shiryar da al'umma zuwa ga alheri da tsoratar da su daga sharri, da yi musu albishir da kyakkyawan sakamako da kuma gargaɗarsu daga mummunan sakamako. Allah ta'ala ya ce:

﴿ رُّسُلٗا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ...﴾ [سورة النساء، الآية:١٦٥].

Ma'ana: ((Manzanni ne masu albishir (ga muminai) masu kuma gargaɗi (ga kafirai) )). (Nisa'i: 165)

d- Gyara mutane ta hanyar nuna musu kyakkyawan abin koyi a cikin maganganu da ayyuka.

e- Tsayar da shari'ar Allah tsakanin bayinSa da kuma ɗabbaƙa ta.

f- Shedar Manzanni a kan al'ummunsu ranar alƙiyama da cewa sun isar musu da saƙon Allah isarwa bayyananniya. Allah ta'ala ya ce:

﴿ فَكَيۡفَ إِذَا جِئۡنَا مِن كُلِّ أُمَّةِۭ بِشَهِيدٖ وَجِئۡنَا بِكَ عَلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِ شَهِيدٗا ﴿٤١﴾ ﴾ [سورة النساء، الآية:٤١].

Ma'ana: ((Sannan ƙaƙa (halin kafirai zai kasance) idan Muka zo da mai ba da shaida daga kowacce al'umma, kuma Muka zo da kai ka zama mai shaida a kan waɗannan)). (Nisa'i: 41)

**(5) Musulunci shi ne addinin dukkanin annabawa:**

Musulunci shi ne addinin dukkanin annabawa da manzanni. Allah ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلْإِسْلَٰمُ ﴾ [سورة آل عمران، الآية:١٩].

Ma'ana: ((Haƙiƙanin adidini a wajan Allah (shi ne) Musulunci)). (Ali-Imran: 19)

Saboda haka dukkaninsu suna kira ne zuwa bautar Allah shi shi kaɗai da watsar da bautar waninSa, duk da yake shari'o'insu da hukunce-hukuncensu sun sha banban, sai dai sun haɗu a kan asali kuma tushen lamarin wanda shi ne Tauhidi. Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"الأنبياء إخوة لعلات." [ رواه البخاري ].

Ma'ana: "Annabawa 'ya'yan kishiyoyi ne (tushensu ɗaya, uwa ce kowa da tasa)". Bukhari ne ya ruwaito shi.

**(6) Manzanni Mutane ne ba su san gaibu ba:**

Sanin gaibu yana daga keɓantattun ilimummukan Allah, ba ya daga cikin siffofin annabawa; domin mutane ne kamar sauran mutane, suna ci suna sha, kuma suna aure, suna bacci, kuma suna cuta, suna wahala. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَمَآ أَرْسَلْنَا قَبْلَكَ مِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ إِلَّآ إِنَّهُمْ لَيَأْكُلُونَ ٱلطَّعَامَ وَيَمْشُونَ فِى ٱلْأَسْوَاقِ... ﴾ [سورة الفرقان، الآية:٢٠].

Ma'ana: ((Ba mu aiko manzanni ba gabaninka face lallai suna cin abinci kuma suna tafiya cikin kasuwanni…)). (Furƙan: 20)

Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلًا مِّن قَبْلِكَ وَجَعَلْنَا لَهُمْ أَزْوَاجًا وَذُرِّيَّةً ﴾

[سورة الرعد، الآية:٣٨].

Ma'ana: ((Haƙiƙa kuma Mun aiko manzanni a gabaninka, Muka kuma ba su mata da zurriya)). (Ra'ad: 38)

Kuma abin da yake samun mutane yana samunsu, na daga baƙin ciki, farin ciki, gajiya da nashaɗi, illa dai su Allah ya zaɓe su ne domin su isar da addinin Allah, ba kuma sa sanin gaibu sai ɗan abin da Allah ya buɗa musu. Allah ta'ala ya ce:

﴿ عَالِمُ الْغَيْبِ فَلَا يُظْهِرُ عَلَىٰ غَيْبِهِ أَحَدًا ﴿٢٦﴾ إِلَّا مَنِ ارْتَضَىٰ مِن رَّسُولٍ فَإِنَّهُ يَسْلُكُ مِنْ بَيْنِ يَدَيْهِ وَمِنْ خَلْفِهِ رَصَدًا ﴿٢٧﴾ ﴾

[سورة الجن، الآيتان ٢٦ ، ٢٧].

Ma'ana: (( (Shi ne) Masanin asirin fake, babu wanda zai buɗa wa gaibunSa, sai wanda ya yarda da shi daga cikin manzanni, to haƙiƙa Shi zai (buɗa masa wani abu daga ciki daidai hikimarSa tare da) saka masa tsaro daga gabanSa da kuma bayansa)) (Jin: 26-27)

(7) Kare Manzanni (daga zunubai) (Isma)

Allah tsarki ya tabbatar masa ya ɗaukaka ya zaɓi mafifitan halittunSa ne domin aikinSa na manzancin da isar da saƙonSa, tare da haka zaɓaɓɓun naSa su ne mafi kamalar mutanensu a halittun jikkunansu da kuma halayensu, ya kuma kare su daga afkawa manyan zunubai (kaba'ira), ya kuɓutar da su daga dukkanin wani aibi domin su iya isar da saƙon Allah izuwa al'ummunsu, saboda haka su kiyayyu ne cikin duk wani labari da suke bayarwa daga Allah Subhanahu wa ta'ala domin isar da saƙonSa, wannan

kuma dukkanin malaman al'umma sun yi ijma'i a kan haka. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ بَلِّغۡ مَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَۖ وَإِن لَّمۡ تَفۡعَلۡ فَمَا بَلَّغۡتَ رِسَالَتَهُۥۚ وَٱللَّهُ يَعۡصِمُكَ مِنَ ٱلنَّاسِۗ ﴾ [سورة المائدة، الآية:٦٧].

Ma'ana: ((Ya kai wannan Manzo, ka isar da abin da aka saukar gare ka daga Ubangijinka; idan kuma ba ka aikata (haka) ba, to ba ka isar da saƙonSa ba, Allah kuma zai kiyaye ka daga (sharrin) mutane)). (Ma'ida: 67)

Allah ta'ala ya faɗa (cikin siffofin annabawa):

﴿ ٱلَّذِينَ يُبَلِّغُونَ رِسَٰلَٰتِ ٱللَّهِ وَيَخۡشَوۡنَهُۥ وَلَا يَخۡشَوۡنَ أَحَدًا إِلَّا ٱللَّهَۗ...﴾ [سورة الأحزاب، الآية:٣٩].

Ma'ana: (( (Su ne) Waɗanda suke isar da saƙon Allah suke kuma tsoronSa, basa kuma tsoron kowa sai Allah)). (Ahzab: 39)

Haka nan Allah ta'ala ya ce:

﴿ لِّيَعۡلَمَ أَن قَدۡ أَبۡلَغُواْ رِسَٰلَٰتِ رَبِّهِمۡ وَأَحَاطَ بِمَا لَدَيۡهِمۡ وَأَحۡصَىٰ كُلَّ شَيۡءٍ عَدَدَۢا ٢٨ ﴾ [سورة الجن، الآية:٢٨].

Ma'ana: ((Don (shi Allah) ya san cewa haƙiƙa sun isar da saƙonnin Ubangijinsu, ya kuma kiyaye abin da yake tare da su, ya kuma ƙididdige komai da saninsa)). (Jinni: 28)

Idan kuma ƙananan zunubai suka afku daga gare su waɗanda ba su da alaƙa da isar da saƙon Allah, to sai Allah ya bayyana musu, nan da nan su kuma sai su tuba zuwa ga Allah, su koma zuwa gare shi, sai su zamanto kamar basu yi ba, sai ma su samu ƙarin daraja a kan wacce suke da ita;

domin Allah ya keɓanci annabawanSa (s.a.w) da kyawawan halaye da kuma siffofin alheri, ya kuma tsarkake su daga duk wani abin da zai zubar da mutuncinsu da matsayinsu.

**(8) Adadin annabawa da manzanni da kuma ambaton mafificin daraja daga cikinsu:**

Ya tabbata cewa adadin manzanni (s.a.w) ɗari uku ne da goma sha wani abu; saboda faɗin Manzon Allah (s.a.w) da aka tambaye shi gameda yawan manzanni, sai ya ce:

"ثلاثمائة وخمس عشرة جماً غفيراً." [ رواه الحاكم ].

Ma'ana: "Ɗari uku ne da goma sha biyar ….." Hakim ne ya ruwaito shi.

Su kuwa annabawa sun fi haka yawa, daga cikinsu akwai waɗanda Allah ya ambata mana ƙissoshinsu a cikin alƙur'ani, wasu kuma bai faɗe su ba. Ya faɗa mana annabi da manzo ashirin da biyar a cikin littafinSa.

Allah ta'ala ya ce:

﴿وَرُسُلًا قَدْ قَصَصْنَاهُمْ عَلَيْكَ مِن قَبْلُ وَرُسُلًا لَّمْ نَقْصُصْهُمْ
عَلَيْكَ ۚ...﴾ [سورة النساء، الآية:١٦٤].

Ma'ana: (( (Muka) kuma (aiko) manzanni waɗanda Muka ba ka labarinsu tun tuni, da kuma wasu manzannin da ba Mu ba ka labarinsu ba)). (Nisa'i: 164)

Haka nan Allah ta'ala ya ce:

﴿وَتِلْكَ حُجَّتُنَا آتَيْنَاهَا إِبْرَاهِيمَ عَلَىٰ قَوْمِهِ ۚ نَرْفَعُ دَرَجَاتٍ
مَّن نَّشَاءُ ۗ إِنَّ رَبَّكَ حَكِيمٌ عَلِيمٌ ﴿٨٣﴾ وَوَهَبْنَا لَهُ إِسْحَاقَ وَيَعْقُوبَ ۚ
كُلًّا هَدَيْنَا ۚ وَنُوحًا هَدَيْنَا مِن قَبْلُ ۖ وَمِن ذُرِّيَّتِهِ دَاوُودَ

وَسُلَيْمَٰنَ وَأَيُّوبَ وَيُوسُفَ وَمُوسَىٰ وَهَٰرُونَۚ وَكَذَٰلِكَ نَجْزِى ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٨٤﴾ وَزَكَرِيَّا وَيَحْيَىٰ وَعِيسَىٰ وَإِلْيَاسَۖ كُلٌّ مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٨٥﴾ وَإِسْمَٰعِيلَ وَٱلْيَسَعَ وَيُونُسَ وَلُوطًاۚ وَكُلًّا فَضَّلْنَا عَلَى ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٨٦﴾ وَمِنْ ءَابَآئِهِمْ وَذُرِّيَّٰتِهِمْ وَإِخْوَٰنِهِمْۖ وَٱجْتَبَيْنَٰهُمْ وَهَدَيْنَٰهُمْ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٨٧﴾ ﴾ [سورة الأنعام، الآيات:٨٣-٨٧].

Ma'ana: ((Wađancan kuma hujjojinmu ne da Muka bai wa Ibrahimu game da mutanensa; Muna đaukaka darajar wanda muka so, haƙiƙa Ubangijinka Gwanin hikima ne da hukunci, Sanau. Kuma muka ba shi ('ya'ya) Ishaƙa da Yakubu, dukkaninsu mun shirye su, Mun kuma shiryi Nuhu tun gabaninsu, kuma daga zuriyyarsa Mun shiryi Dauda da Sulaimanu da Ayyuba da Yusufa da Musa da kuma Haruna. Kamar haka kuwa muke saka wa masu kyautata (ayyukansu). Kuma Zakariya'u da Yahaya da Isa da kuma Iliyasu, kowannensu yana daga cikin salihai. Da kuma Isma'ila da Al-yasa'u da Yunusa da kuma Luđu; kowannensu kuwa Mun fifita shi a kan (sauran) talikai. (Haka) kuma (Mun fifita wasu) daga iyayensu da zuri'arsu da kuma 'yan uwansu, Muka zaɓe su kuma muka shiryar da su tafarki madaidaici)). (An'am: 83-87)

Haƙiƙa Allah ya fifita wasu annabawa sama da wasu, kamar yadda ya ce:

﴿ ...وَلَقَدْ فَضَّلْنَا بَعْضَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ عَلَىٰ بَعْضٍۖ...﴾ [سورة الإسراء، الآية:٥٥].

Ma'ana: ((.. Haƙiƙa mun fifita wasu annabawa sama da

wasunsu ..)) (Isra'i: 55)

Kamar yadda ya fifita wasu manzanni a kan wasu, kamar yadda ya ce:

﴿ تِلْكَ ٱلرُّسُلُ فَضَّلْنَا بَعْضَهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ ...﴾ [سورة البقرة، الآية:٢٥٣].

Ma'ana: ((Waɗancan manzannin Mun fifita shashinsu a bisa shashi)). (Baƙara: 253)

Mafifitan manzanni su ne waɗanda ake kira "ulul azmi" wato zaratan annabawa, su ne: Nuhu, Ibrahim, Musa, Isa da kuma Annabinmu Muhammadu Allah ya ƙara musu salati da salami. Allah ta'ala ya ce:

﴿ فَٱصْبِرْ كَمَا صَبَرَ أُوْلُواْ ٱلْعَزْمِ مِنَ ٱلرُّسُلِ ...﴾ [سورة الأحقاف، الآية:٣٥].

Ma'ana: ((Ka yi haƙuri kamar yadda manyan manzanni (zarata) suka yi)). (Ahƙaf: 35)

A wani gurin Allah ya ce:

﴿ وَإِذْ أَخَذْنَا مِنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مِيثَٰقَهُمْ وَمِنكَ وَمِن نُّوحٍ وَإِبْرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ ۖ وَأَخَذْنَا مِنْهُم مِّيثَٰقًا غَلِيظًا ۝٧ ﴾ [سورة الأحزاب، الآية:٧].

Ma'ana: ((Kuma ka tuna lokacin da Muka ɗauki alƙawari daga annabawa (na isar da aike), kamar yadda muka ɗauka daga wajenka, haka nan daga Nuhu da Ibrahimu da Musa da Isa ɗan Maryamu; Muka kuma riƙi alƙawari mai kauri (abin ƙarfafawa) daga gare su)). (Ahzab: 7)

Annabi Muhammadu (s.a.w) shi ne mafificin manzanni, kuma cikamakin annabawa, shumagaban masu taƙawa, shugaban 'yan Adam, kuma shi ne limamin annabawa idan suka haɗu, kuma shi ne kakakinsu idan suka kai ziyara, shi

ne mai matsayin yabo wanda halittun farko da na ƙarshe suke fatansa, kuma shi ne mai tutar yabo da tafkin da za a sha ruwansa (ranar ƙiyama), haka nan shi ne mai ceton dukkanin halittu a wannan rana, shi ne mai matsayin "wasila" (kusanci na musamman) da "fadhila" (falala ta musamman), Allah ya aiko shi da mafificin shari'o'in addininSa, ya kuma sa al'ummarsa su ne mafifita sama da dukkanin al'ummun da suka bayyana cikin mutane, haka dai Allah ya tattara wa wannan Annabi da shi da al'ummarsa darajoji da kyawawan abubuwan da ya rarraba su tsakankanin annabawa da al'ummun da suka gabace su, haka nan su ne al'umma ta ƙarshe da aka halitta, amma kuma su ne al'umma ta farko da za ta tashi ranar alƙiyama.

Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"فضلت على الأنبياء بست...". [ رواه مسلم].

Ma'ana: "An fifita ni bisa annabawa da abubuwa guda shida". Muslim ne ya ruwaito shi.

Annabi (s.a.w) ya ce:

"أنا سيد ولد آدم يوم القيامة، وبيدي لواء الحمد ولا فخر. وما من نبي يومئذ آدم فمن سواه إلا تحت لوائي يوم القيامة." [ رواه أحمد والترمذي].

Ma'ana: "Ni ne shugaban 'yan Adam ranar alƙiyama, kuma a hannu na tutar yabo take, ba alfahari ba, kuma babu wani annabi a wannan rana; Adamu ko waninsa face yana ƙarƙarshin tutata ranar alƙiyama". Ahmad da Tirmizi ne suka ruwaito shi.

Mai bin Annabi (s.a.w) a falala daga cikin sauran annabawa shi ne Annabi Ibrahim (a.s) badaɗin Allah, saboda haka badaɗai guda biyu su ne mafifitan manyan annabawa, sannan kuma sai sauran manyan guda uku.

**(9) Alamomin annabawa (a.s) (Mu'ujizoji):**

Allah ya ƙarfafi manzanninSa (a.s) da wasu alamomi masu girma, da mu'ujizojin da suka fi ƙarfin hankula, domin su kasance hujja a gare su, wani zubin kuma biyan buƙatu a gare su, kamar Alƙur'ani mai girma, tsagewar wata, rikiɗewar sanda zuwa micijiya, ƙera tsuntsu mai rai daga taɓo, da makamantansu.

Ita mu'ujiza wacce take keta al'ada dalili ce bisa annabci na gaske, ita kuma karama dalili ce a bisa gaskiyar mai ita kan cewa shi mai gaskata wa ne ga annabcin nan na gaske.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ لَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلَنَا بِٱلْبَيِّنَٰتِ...﴾ [سورة الحديد، الآية:٢٥].

Ma'ana: ((Haƙiƙa mun aiko manzanninmu da hujjoji mabayyana ..)). (Hadid: 25)

Manzon Allah (s.a.w) kuma ya ce:

"ما من نبي من الأنبياء إلا وقد أوتي من الآيات ما آمن على مثله البشر، وإنما كان الذي أوتيته وحياً أوحاه إلي، فأرجو أن أكون أكثرهم تابعاً القيامة." [متفق يوم عليه].

Ma'ana: "Babu wani annabi face an ba shi wata sheda (mu'ujiza) da za ta sa mutane su yi imani da shi, ni kuwa irin ta wa mu'ujizar wahayi ne da Allah ya aiko mini shi; don haka ina fatan in zamo mafificinsu a yawan mabiya ranar alƙiyama". Bukhari da Muslimu ne suka ruwaito shi.

**(10) Imani da annabtar Annabinmu Muhammad (s.a.w):**

Imani da annabtarsa wani ginshiƙi ne mai girma daga cikin turaku ko ginshiƙai na imani, kuma babu wani imani in babu shi. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَمَن لَّمْ يُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ فَإِنَّآ أَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ سَعِيرًا

﴾ ﴿ [سورة الفتح، الآية:١٣]

Ma'ana: ((Duk wanda bai yi imani da Allah da manzonSa ba to haƙiƙa (kafiri ne), mun kuwa tanadarwa kafirai azabar wutar "Sa'ira" (mai tsananin ƙuna) )). (Fath: 13)

Manzon Allah (s.a.w) kuma ya ce:

"أمرت أن أقاتل الناس حتى يشهدوا أن لا إله إلا الله وأني رسول الله." [رواه مسلم].

Ma'ana: "An ba ni umarnin yaƙar mutane (dukkaninsu) har sai dai idan sun yi imani da cewa babu abin bauta na gaskiya sai Allah, sun kuma shaida cewa ni Manzon Allah ne ..". Muslimu ne ya ruwaito shi.

Imani da Manzon Allah (s.a.w) ba ya ingantuwa sai an haɗa abubuwa masu zuwa:

**- Na farko:** Sanin Annabinmu (s.a.w). Shi ne Muhammadu ɗan AbdulLahi ɗan Abdul Muɗɗalib, ɗan Hashimu, shi kuwa Hashimu daga ƙuraishawa yake, su kuma ƙuraishawa larabawa ne, larabawa kuma jikokin Isma'ila ne ɗan Ibrahim badaɗin Allah, salati da salamin Allah su ƙara tabbata a gare su. Ya rayu shekara sittin da uku (63), arba'in (40) daga cikinsu kafin ya zama annabi, ishirin da uku (23) kuma bayan ya zama annabi kuma manzo.

**- Abu na biyu:** Gaskata shi cikin abin da ya labarta, da bin umarninsa, da kuma nisantar abin da ya hana ko ya tsawatar a kai, haka nan kar a bauta wa Allah sai da abin da ya shar'anta.

**- Na uku:** Kudurce cewa shi Manzon Allah ne zuwa dukkanin "Nauyaya" guda biyu; mutane da aljanu, saboda haka ba su da wata hanya ko wata dama sai cikin binsa (s.a.w). Allah ta'ala ya ce:

﴿ قُلۡ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيۡكُمۡ جَمِيعًا ...﴾ [سورة الأعراف، الآية:١٥٨].

Ma'ana: ((Ka ce (ya kai wannan Manzo): Ya ku mutane! Haƙiƙa ni ne manzon Allah zuwa gare ku baki ɗaya..)). (A'raf: 158)

**- Na huɗu:** Imani da manzancinsa, da kasancewarsa mafificin annabawa kuma cikamakinsu (na ƙarshensu). Allah ta'ala ya ce:

﴿ ...وَلَـٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَۗ ...﴾ [سورة الأحزاب، الآية:٤٠].

Ma'ana: ((..Sai dai shi Manzon Allah ne, kuma cikamakin annabawa..)). (Ahzab: 40)

Da kuma ƙudurce cewa shi badaɗin Allah ne, kuma shugaban 'yan Adam, ma'abocin babban ceto, wanda aka keɓanta da matsayin "wasila" wanda shi ne matsayi mafi ɗaukaka a gidan aljanna, a ƙudurce cewa Annabi shi ne ma'abocin tafkin da za a sha, kuma al'ummarsa su ne mafi alherin al'ummu. Allah ta'ala ya ce:

﴿ كُنتُمۡ خَيۡرَ أُمَّةٍ أُخۡرِجَتۡ لِلنَّاسِ ...﴾ [سورة آل عمران، الآية:١١٠].

Ma'ana: ((Kun kasance al'umma mafi alheri da aka fitar wa mutane..)). (Ali Imran: 110).

Kuma su ne mafi yawancin 'yan aljanna, kuma saƙon da aka ba wa Annabinmu ya shafe dukkanin saƙonnin da suka gabace shi.

**- Na biyar:** Allah ta'ala ya ƙarfafe shi da mafi girman mu'ujiza, kuma mafi bayyanar alama, wacce ita ce (mu'ujizar) Alƙur'ani mai girma, zancen Allah katangagge daga canji ko gurɓatawa. Allah ta'ala ya ce:

﴿ قُل لَّئِنِ ٱجْتَمَعَتِ ٱلْإِنسُ وَٱلْجِنُّ عَلَىٰٓ أَن يَأْتُوا۟ بِمِثْلِ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ لَا يَأْتُونَ بِمِثْلِهِۦ وَلَوْ كَانَ بَعْضُهُمْ لِبَعْضٍ ظَهِيرًا ﴿٨٨﴾ ﴾ [سورة الإسراء، الآية:٨٨].

Ma'ana: ((Ka ce (da su): "Wallahi idan da mutane da aljanu sun haɗa kansu don kawo irin wannan Alƙur'ani, to ba za su zo da irinsa ba, ko da kuwa sashinsu sun zamanto suna taimakawa sashi" )). (Isra': 88).

Allah ya ƙara cewa:

﴿ إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا ٱلذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ﴿٩﴾ ﴾ [سورة الحجر، الآية:٩].

Ma'ana: ((Haƙiƙa Mu Muka saukar da Al'ƙur'ani, haƙiƙa kuma lallai Mu za Mu kiyaye shi)). (Hijir: 9)

**- Na shida**: Imani da cewa Manzon Allah (s.a.w) ya isar da saƙo, ya ba da amana, ya kuma yi wa al'umma nasiha, babu wani alkhairi face ya nuna musu shi, ya kuma kwaɗaitar da su gare shi, babu kuma wani sharri sai da ya hana al'umma afka masa tare da tsoratar da su shi.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ لَقَدْ جَآءَكُمْ رَسُولٌ مِّنْ أَنفُسِكُمْ عَزِيزٌ عَلَيْهِ مَا عَنِتُّمْ حَرِيصٌ عَلَيْكُم بِٱلْمُؤْمِنِينَ رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿١٢٨﴾ ﴾ [سورة التوبة:الآية ١٢٨].

Ma'ana: ((Haƙiƙa Manzo daga cikinku ya zo muku; abin da duk zai cuce ku yana damunsa, mai kwaɗayi ne (ga dukkani wani alheri) a gare ku, mai tausaya wa kuma mai jin ƙai ga muminai)). (Tauba: 128)

Manzon Allah (s.a.w) kuma ya ce:

"ما من نبي بعثه الله في أمة قبلي إلا كان حقاً عليه أن يدل أمته على

خير ما يعلمه لهم، ويحذر أمته من شر ما يعلمه لهم." [رواه مسلم].

"Babu wani Annabi da aka aiko wa wata al'umma kafin al'ummata, sai an wajabta masa nuna wa al'ummar tasa duk wani alheri da ya san zai amfane su, ya kuma tsoratar da su duk wani sharri da zai iya samunsu". Muslim ne ya ruwaito shi.

**- Na bakwai**: Son Annabi (s.a.w), tare da gabatar da son nasa kan son kai da ma son dukkanin sauran halittu, hakanan girmama shi, mutunta shi, ɗaukaka shi, karrama shi, da kuma biyayya a gare shi; waɗannan duka haƙƙoƙinsa ne da Allah ya wajabta miƙa su a gare shi cikin littafinSa; domin son shi yana cikin son Allah, haka yi masa biyayya ma yanki ne na biyayya ga Allah;

﴿ قُلْ إِن كُنتُمْ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِى يُحْبِبْكُمُ ٱللَّهُ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ذُنُوبَكُمْ ۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٣١﴾ ﴾ [سورة آل عمران:الآية ٣١].

Ma'ana: ((Ka ce musu (ya kai wannan Manzo) in dai kun kasance kuna son Allah to sai ku biyo ni, Allah zai so ku, zai kuma gafarta muku zunubanku, Allah shi ne Mai yawan gafara, Mai matuƙar jin ƙai)) (Ali-Imran: 31)

Manzon Allah (s.a.w) kuma ya ce:

"لا يؤمن أحدكم حتى أكون أحب إليه من ولده ووالده والناس أجمعين" [متفق عليه].

Ma'ana: "Ɗayanku ba zai zama mai imani ba har sai na zamanto abin ƙauna a gare shi sama da ɗansa da mahaifinsa da ma dukkanin mutane". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

**- Na Takwas:** Yin salati da salami a gare shi tare da yawaitawa yinsu; domin kuwa marowaci na haƙiƙa shi ne wanda aka ambaci Annabi a gabansa amma ya ƙi yi masa

salati. Allah ta'ala cewa ya yi:

ا إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَـٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ عَلَى ٱلنَّبِيِّ ۚ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ صَلُّوا۟ عَلَيْهِ وَسَلِّمُوا۟ تَسْلِيمًا ﴿٥٦﴾ ﴾ [سورة الأحزاب:الآية ٥٦] .

Ma'ana: ((Haƙiƙa Allah da Mala'ikunSa suna yi wa Annabi salati, Ya ku waɗanda suka yi imani kuma ku yi salati tare da yin salami a gare shi sosai)). (Al –Ahzab: 56)

Annabi (s.a.w) kuma ya ce:

"من صلى عليّ واحدة، صلّى الله عليه بها عشراً." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Wanda ya yi mini salati sau ɗaya, Allah zai yi masa salati goma sakamakonsa" Muslim ne ya ruwaito shi.

Muhimmancin yin salati yana ƙara ƙarfafa a wasu lokuta, kamar lokacin tashahhud (tahiya), cikin al-ƙunutu, cikin sallar gawa, cikin huɗubar juma'a, bayan kiran sallah, lokacin shiga masallaci da lokacin fita daga cikinsa, cikin addu'a, idan an ambaci Annabi (s.a.w) da ma dai wasu guraren daban.

**- Na tara:** (Sanin) cewa Annabi (s.a.w) shi da sauran annabawa dukkaninsu suna nan da ransu a wajen Ubangijinsu, suna rayuwa irin ta "Barzakhu" (wato rayuwar da ke bayan rayuwar duniya kafin kuma tashin ƙiyama), wacce ta ma fi rayuwar shahidai kamala da ɗaukaka, amma kuma ba irin rayuwar da suka yi ba ce a filin duniya, ba mu dai san yadda yanayinta yake ba, kuma kasancewarsu a cikinta bai fitar da su daga kasancewarsu matattu ba. Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"إن الله حرم على الأرض أن تأكل أجساد الأنبياء." [رواه أبو داود والنسائي].

Ma'ana: "Allah ya haramta wa ƙasa cin naman jikkunan annabawa". Abu Dawuda da Nasa'i ne suka ruwaito shi.

Kuma Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"ما من مسلم يسلم عليّ إلا رد الله علي روحي كي أرد عليه السلام". [ رواه أبو داود ].

Ma'ana: "Babu wanda zai yi sallama a gare ni face Allah ya dawo min da raina domin in amsa masa sallamar". Abu Dawuda ne ya ruwaito shi.

**- Na goma:** Yana daga girmama Annabi (s.a.w) kada a ɗaga murya a gabansa a lokacin da yake da ransa, haka nan yayin sallama a gare shi a gaban kabarinsa.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَرْفَعُوٓاْ أَصْوَٰتَكُمْ فَوْقَ صَوْتِ ٱلنَّبِيِّ وَلَا تَجْهَرُواْ لَهُۥ بِٱلْقَوْلِ كَجَهْرِ بَعْضِكُمْ لِبَعْضٍ أَن تَحْبَطَ أَعْمَـٰلُكُمْ وَأَنتُمْ لَا تَشْعُرُونَ ﴿٢﴾ ﴾ [سورة الحجرات:الآية ٢].

Ma'ana: ((Ya ku waɗanda suka yi imani kada ku ɗaga muryoyinku sama da muryar Annabi, kada kuma ku bayyanar da Magana gare shi kamar yadda kuke yi wa junanku, don kada ayyukanku su lalace, alhali ku ba kwa jin hakan (ba ku sani ba) )). (Hujurat: 2)

Kasancewar darajar Annabi (s.a.w) bayan an binne shi kamar darajarsa ne a lokacin da yake da rai; ya wajaba mu girmama shi, kamar yadda magabatanmu na farko suka yi, Allah ya ƙara yadda a gare su, yadda suka zamanto mafi tsananin biyayya a gare shi, kuma mafiya nisa daga saɓa masa ko ƙirƙirar abin da ba ya cikin addinin da ya zo da shi daga Allah.

**- Na goma sha ɗaya:** Son sahabbansa da mutanen gidansa da matansa, tare da jiɓintar su dukkaninsu, da gudun tawayarsu ko zaginsu ko sukansu da wani abin suka; domin kuwa Allah ya yarda da su ya zaɓe su su zamanto

abokan rayuwa ga Annabinsa, ya kuma wajabta wa wannan al'ummar sonsu da jiɓintarsu.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلۡأَوَّلُونَ مِنَ ٱلۡمُهَٰجِرِينَ وَٱلۡأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُم بِإِحۡسَٰنٖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُ ﴾ [سورة التوبة:الآية ١٠٠].

Ma'ana: ((Magabata na farko, waɗanda suka yi hijira, haka mutan Madina, da kuma waɗanda sukai musu biyayya tare da kyautatawa (duka) Allah ya yarda da su, su ma sun yarda da shi ..)). (Tauba: 100)

Kuma Annabi (s.a.w) ya ce:

"لا تسبوا أصحابي، فوالذي نفسي بيده لو أنفق أحدكم مثل أحد ذهباً ما بلغ مد أحدهم ولا نصيفه." [رواه البخاري].

Ma'ana: "Ka da ku zagi sahabbaina, na rantse da wanda raina yake hannunSa, da ɗaya daga cikinku zai bayar da zinare kwatankwacin dutsen Uhudu da bai kai ladan mudu ɗaya ko ma rabin mudu da ɗayansu ya bayar ba". Bukhari ne ya ruwaito shi

Haka nan Allah Ya kuma kwaɗaitar da waɗanda suka zo bayansu da su dinga nema musu gafara tare da roƙon kada Allah ya sanya wani gillu da ƙiyayya a cikin zukantansu ga magabatan. Inda ya ke cewa:

﴿ وَٱلَّذِينَ جَآءُو مِنۢ بَعۡدِهِمۡ يَقُولُونَ رَبَّنَا ٱغۡفِرۡ لَنَا وَلِإِخۡوَٰنِنَا ٱلَّذِينَ سَبَقُونَا بِٱلۡإِيمَٰنِ وَلَا تَجۡعَلۡ فِي قُلُوبِنَا غِلّٗا لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ رَبَّنَآ إِنَّكَ رَءُوفٞ رَّحِيمٌ ١٠ ﴾ [سورة الحشر:الآية ١٠].

Ma'ana: ((Waɗanda kuma suka zo daga bayansu, suna

cewa: "Ya Ubangijinmu! Ka gafarta mana da kuma 'yan uwanmu waɗanda suka rigaye mu da imani, kada kuma ka sanya wata gaba a zukatanmu ga waɗanda suka ba da gaskiya, ya Ubangijinmu kai mai yawan tausasawa ne kuma mai tsananin jin ƙai)). (Hashri: 10)

**- Na goma sha biyu:** Nisantar zurfafawa cikin lamarinsa; domin kuwa yin hakan yana cikin mafi tsananin cutarwa a gare shi; domin kuwa ya tsoratar da al'ummarsa zurfafawar da wuce-iyaka cikin koɗa shi da yabonsa, da kuma kai shi sama da matsayin da Allah Ubangiji ya ajiye shi a cikinsa, irin matsayin da Allah Mabuwayi Maɗaukaki shi kaɗai ya keɓantu da shi. Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"إنما أنا عبد فقولوا عبد الله ورسوله، لا أحب أن ترفعوني فوق منزلتي."

Ma'ana: "Ni ba komai ba ne face bawa (ga Allah); saboda haka ku ce (mini): "Bawan Allah, Manzon Allah", ba na so ku ɗaga ni har ku kai ni sama da matsayina".

Ya kuma ƙara da cewa:

"لا تطروني كما أطرت النصارى ابن مريم." [ رواه البخاري ].

Ma'ana: "Kar ku koɗa ni (wato zurfafawa ga yabo) kamar yadda Nasarawa (kiristoci) suka koɗa Ɗan Maryamu" Bukhari ne ya ruwaito shi

Kuma ba ya halatta a roƙe shi, ko a nemi ɗauki daga wajensa, ko a yi ɗawafi ga kabarinsa (a kewaya shi kamar Ka'aba), ko a kai masa bakance, ko a yi masa yanka; domin yin haka dukkaninsa shirka ne da Allah, Allah dai ya hana a miƙa wata ibada ga waninsa.

To haka nan shi ma kishiyar zurfafawar ba abin yi ba ne; domin kuwa rashin girmama Annabi (s.a.w) wanda yake nuna rena matsayinsa, haka nan sukansa ko wulaƙanci gare shi ko yi masa isgili ridda ce wato fita daga musulunci kuma kafirci ne ga Allah. Allah ya ce:

﴿قُلۡ أَبِٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ وَرَسُولِهِۦ كُنتُمۡ تَسۡتَهۡزِءُونَ ٦٥ لَا تَعۡتَذِرُواْ قَدۡ كَفَرۡتُم بَعۡدَ إِيمَٰنِكُمۡۚ﴾ [سورة التوبة:الآية ٦٦] .

Ma'ana: ((Ka ce da su: "Yanzu Allah ne da ayoyinSa da ManzonSa kuke yi wa izgili? Ka da ku kawo wani hanzari; haƙiƙa kun dai kafirta bayan imaninku .." (Tauba: 65-66)

Amma soyayya ta gaske ga Manzon Allah (s.a.w) ita ce wacce take kora ma'abocinta zuwa kwaikwayon ayyukansa, da bibiyar sunnarsa, da barin duk wani abin da ya saɓa wa hanyarsa, Allah ya ƙara masa salati da salami. Allah ta'ala ya ce:

﴿قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۗ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣١﴾ [سورة آل عمران:الآية ٣١]

Ma'ana: ((Ka ce (da su): "Idan kun kasance kuna son Allah to ku bi ni, sai Allah ya so ku, ya kuma gafarta muku zunubanku, Allah kuwa Mai yawan gafara ne Mai matuƙar jin ƙai". (Ali Imran: 31)

Saboda haka abin da ya wajaba shi ne kada a zurfafa kada kuma a yi ƙwauro wajen girmama Manzon Allah (s.a.w), kada a kai shi matsayin Allantaka, kada kuma a tauye masa alƙadarinsa da haƙƙinsa na girmamawa da soyayya waɗanda suka fi bayyanuwa a fagen biyayya ga shari'arsa, da tafiya kan turbar karantarwarsa, da kuma kwaikwayon ayyukansa, salatin Allah da salaminSa su ƙara tabbata a gare shi.

**- Na goma sha uku**: Imani da Annabi (s.a.w) ba ya tabbatuwa sai da gaskata shi da aiki da abin da ya zo da shi, wannan kuma shi ne ma'anar miƙa ragama zuwa gare shi, shi ya sa binsa shi ne bin Allah, saɓa masa kuma shi ne saɓawa Allah. Imani da shi yana cika ne kawai bayan

tabbatuwar gaskata shi da kammalar biyayya a gare shi, sallal Lahu alaihi wa sallam.

………………………………………………………

# RUKUNI NA BIYAR : IMANI DA RANAR LAHIRA

(1) Imani da ranar lahira: Shi ne ƙudurce cewa rayuwar duniya za ta ƙare, bayanta kuma sai a shiga wata rayuwar ta daban, wacce take farawa daga mutuwa da kuma rayuwar "barzakhu" sannan tashin ƙiyama, sannan a tashi mutane, a tattara su, sannan a yi musu sakamako har dai kowa ya shiga masaukinsa; Aljanna ko Wuta.

Wannan ƙuduri game da ranar lahira ɗaya ne daga cikin rukunan Imani wanda ba ya kammaluwa sai da su, wanda kuma ya yi inkarinsa to ya kafirta. Allah Ta'ala ya ce:

﴿ وَلَٰكِنَّ ٱلۡبِرَّ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ ﴾ [سورة البقرة:الآية ١٧٧].

Ma'ana: ((Sai dai haƙiƙanin bin Allah (yana tare da) da wanda ya yi imani da Allah da ranar Lahira..)). (Baƙara: 177)

Annabi (s.a.w) kuma ya faɗa a cikin hadisin nan na zuwan Jibrila (a.s) inda ya ce masa: "Ba ni labarin mene ne imani? Sai ya ce:

" أن تؤمن بالله، وملائكته، وكتبه، ورسله، واليوم الآخر، وأن تؤمن بالقدر خيره وشره." [رواه مسلم].

Ma'ana: (shi ne) Ka yi imani da Allah da Mala'ikunSa da littattafanSa da ManzanninSa da ranar lahira, ka kuma yi imani da ƙaddara, alherinta da sharrinta". Muslim ne ya ruwaito shi 1/157

Yana daga abubuwan da ya wajaba a yi imani da su: Abubuwan da za su gabaci ranar lahira waɗanda Manzon Allah ya ba da labarinsu a matsayin alamomin tashin ƙiyama.

Malamai sun kasa waɗannan alamomi zuwa kashi biyu:

A – Kananan alamomi: Su ne waɗanda suke nuna kusancin tashin ƙiyama, waɗannan alamomin suna da yawa sosai, wasu da yawa daga cikinsu ko ma galibinsu sun rigaya sun faru.

Daga cikinsu da akwai: Aiko Annabi Muhammadu (s.a.w), tozarta amana, ƙawata masallatai da alfahari da su, gogoriyon makiwata cikin tsawaita gine-gine, yaƙi da Yahudawa tare da karkashe su, kusantuwar lokuta, ƙarancin aiki (na gari), bayyanar fitintinu, yawan kashe-kashe da yawan zinace-zinace da fasiƙanci. Allah ta'ala ya ce:

ﭐﱡﭐ ٱقۡتَرَبَتِ ٱلسَّاعَةُ وَٱنشَقَّ ٱلۡقَمَرُ ١ ﱠ [سورة القمر:الآية ١].

Ma'ana: ((Alƙiyama ta kusanto, wata ya tsage)). (Ƙamar: 1)

B- Manyan alamomin tashin ƙiyama: Su ne waɗanda za su zo daf da tashin ƙiyama ɗin, suna nufin gargaɗi da isowar farko-farkonta. Waɗannan alamomi guda goma ne, har yanzu babu wacce ta faru daga cikinsu.

Daga cikinsu akwai: fitowar Mahadi, fitowar Dujal, saukowar Annabi Isa (as) daga sama yana mai hukunci da adalci, zai karya gicciye (kuros), ya kuma kashe Dujal da aladu, zai kuma soke "Jiziya" (harajin da kafirai suke bayarwa domin a kula da su cikin ƙasar musuluci), zai yi hukunci da shari'ar Musulunci, Yajuju da Majuju kuma za su fito, sai ya yi musu addu'a su mutu. Daga alamomin dai har ila yau akwai Daddarewar ƙasa sau uku; ɗaya a gabas, ɗaya a yamma, ɗaya kuma a tsibirin larabawa, wani Hayaƙi da zai turnuƙe sararin samaniya ya lulluɓe mutane ya game su dukkaninsu, za kuma a ɗauke Al-Kur'ani daga duniya baki ɗaya zuwa sama, rana za ta fito daga mafaɗarta. Yana daga cikin alamomin dai fitowar dabba, da fitowar wata wuta mai girma daga "Adan" (a ƙasar Yaman) za ta dinga kora mutane zuwa ƙasar "Sham", wannan ita ce alama ta

ƙarshe cikin manyan alamun tashin ƙiyama.

روى مسلم عن حذيفة بن أسيد الغفاري –رضي الله عنه– قال: اطلع النبي صلى الله عليه وسلم، ونحن نتذاكر فقال: " ما تذكرون؟" قالوا: نذكر الساعة. قال: "إنها لن تقوم حتى تروا قبلها عشر آيات. فذكر: الدخان، والدجال، والدابة، وطلوع الشمس من مغربها، ونزول عيسى بن مريم، ويأجوج، وثلاثة خسوف: خسف بالمشرق، وخسف بالمغرب، وخسف بجزيرة العرب، وآخر ذلك نار تخرج من اليمن تطرد الناس إلى محشرهم." [رواه مسلم].

Muslim ya ruwaito daga Huzaifa ɗan Asid Algifari, Allah ya ƙara yarda a gare shi, ya ce: Annabi (s.a.w) ya leƙo ya same mu muna bita, sai ya ce: "Me kuke tattaunawa? Sai muka ce: Muna tattaunawa ne game da Tashin ƙiyama, sai Annabi (s.a.w) ya ce: "Ai lallai alƙiyama ba za ta tashi ba har sai kun ga abubuwa goma gabaninta, sai Annabi ya faɗi: hayaƙi, da Dujal, da dabba, da fitowar rana daga mafaɗarta, da saukowar Annabi Isa ɗan Maryamu, da Yajuju, da darewar ƙasa sau uku; ɗaya a gabas, ɗaya a yamma, ɗaya kuma a tsibirin larabawa, ƙarshensu kuma sai wata wuta da za ta fito daga Yaman, tana kora mutane zuwa matattararsu (inda za a yi musu hisabi)". Muslimu ne ya ruwaito shi.

Kuma Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"يخرج في آخر أمتي المهدي، يسقيه الله الغيث، وتخرج الأرض نباتها، ويعطي المال صحاحاً، وتكثر الماشية، وتعظم الأمة، يعيش سبعاً، أو ثمانياً، يعني حججاً". [ رواه الحاكم في المستدرك ].

Ma'ana: "A ƙarshen zamani Mahadi zai fito, Allah zai shayar da shi ruwan sama, ƙasa kuma ta fito da tsirranta, za

a raba dukiya yadda ya kamata, dabbobin gida kuma za su yawaita, al'umma kuma za ta ɗaukaka ta bunƙasa, zai rayu bakwai ko takwas, yana nufin shekaru (wato a cikin wannan halin). Hakim ne ya ruwaito shi a littafinsa: "Al-Mustadrak".

Ya kuma zo a cikin wani hadisi cewa waɗannan alamomi suna bibiyar junansu ne kamar yadda ƙwayar carbi take bin 'yar uwarta a cikin zubinsu, saboda haka kowacce ta bayyana daga cikinsu sai 'yar uwatta ta biyo ta, da zarar sun ƙare kuma sai alƙiyama ta tashi da ikon Allah Maɗaukaki.

Abin da ake nufi da "As-Sa'a" (tashin alƙiyama): wato ranar da mutane za su fito daga cikin kaburburansu da umarnin Ubangijinsu; domin a yi musu hisabi, daga nan kuma sai a ni'imta wanda ya kyautata daga cikinsu, a kuma azabtar da wanda ya munana. Allah ta'ala y ace:

﴿ يَوْمَ يَخْرُجُونَ مِنَ ٱلْأَجْدَاثِ سِرَاعًا كَأَنَّهُمْ إِلَىٰ نُصُبٍ يُوفِضُونَ ﴿٤٣﴾ ﴾ [سورة المعارج:الآية ٤٣].

Ma'ana: ((Ranar da za su fito daga cikin kaburburansu suna ta gaggawa, kai ka ce suna gaggawa ne zuwa kafaffun tutotoci (wato matattararsu) )). (Ma'arij: 43)

Wannan rana Alƙur'ani ya ba ta sunaye daban-daban, daga cikinsu akwai:

- Al-Ƙiyama (Ranar tashi), Al-Ƙari'a (Mai ƙwanƙwasa), Ranar hisabi, Ranar sakamako, Aɗ-Ɗamma (uwar masifu), Al-waƙi'a (Mai aukuwa), Al-Haƙƙa (Mai tabbatarwa), As-Sakkha (mai tsawa), Al-gashiya (Mai lulluɓe mutane), da sauransu.

- Ranar ƙiyama: Allah ya ce:

﴿ لَآ أُقْسِمُ بِيَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ ﴿١﴾ ﴾ [سورة القيامة:الآية ١].

Ma'ana: ((Ba sai na yi rantsuwa da ranar al-ƙiyama ba))

(Al-ƙiyama: 1)

- Rana Mai ƙwanƙwasa: Allah ta'ala ya ce:

﴿ ٱلۡقَارِعَةُ ۝١ مَا ٱلۡقَارِعَةُ ۝٢ ﴾ [سورة القارعة:الآيتان ١-٢].

Ma'ana: ((Mai ƙwanƙwasar (zukata da tsoro), Mene ne Mai ƙwanƙwasa?!)).

- Ranar Hisabi : Allah ya ce :

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَضِلُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ لَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدُۢ بِمَا نَسُواْ يَوۡمَ ٱلۡحِسَابِ ﴾ [سورة ص:الآية ٢٦].

Ma'ana: ((Haƙiƙa waɗanda suke ɓace wa hanyar Allah, azaba mai tsanani ta tabbata a gare su; domin mantawa da suka yi da ranar hisabi)). (Sad: 26)

- Ranar sakamako: Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَإِنَّ ٱلۡفُجَّارَ لَفِي جَحِيمٖ ۝١٤ يَصۡلَوۡنَهَا يَوۡمَ ٱلدِّينِ ۝١٥ ﴾ [سورة الانفطار:الآيتان ١٤-١٥].

Ma'ana: ((Haƙiƙa lallai fajirai suna cikin wutar Jahimu. Za su shige ta ne a ranar sakamako)). (Infiɗar: 14 – 15)

- Aɗ-Ɗamma: Allah ta'ala ya ce:

﴿ فَإِذَا جَآءَتِ ٱلطَّآمَّةُ ٱلۡكُبۡرَىٰ ۝٣٤ ﴾ [سورة النازعات : الآية ٣٤] .

Ma'ana: ((To, idan uwar masifu mafi girma ta zo)). (Nazi'at: 34)

- Al-Waƙi'a: Allah ta'ala ya ce:

﴿ إِذَا وَقَعَتِ ٱلۡوَاقِعَةُ ۝١ ﴾ [سورة الواقعة:الآية ١].

Ma'ana: ((Idan Mai aukuwa ta uku)) (Al-waƙi''a: 1)

- Al- Haƙƙa: Allah ta'ala ya ce:

﴿ ٱلۡحَآقَّةُ ۝١ مَا ٱلۡحَآقَّةُ ۝٢ ﴾ [سورة الحاقة:الآيتان ١-٢].

Ma'ana: ((Mai tabbatarwa! Mamakin girman Mai tabbatarwa!)) (Al-Haƙƙa: 1-2)

- As-Sakkha: Allah ta'ala ya ce:

﴿فَإِذَا جَآءَتِ ٱلصَّآخَّةُ ۝٣٣﴾ [سورة عبس:الآية ٣٣].

Ma'ana: ((To, idan (ranar nan) Mai tsawa (wacce take kurumtarwa saboda tsawarta) ta zo)). (Abasa: 33)

- Al-Gashiya: Allah ta'ala ya ce:

﴿هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلۡغَٰشِيَةِ ۝١﴾ [سورة الغاشية:الآية ١].

Ma'ana: ((Shin labarin (ranar nan) mai lulluɓe mutane (da tsoronta) ya zo maka?)) (Gashiya: 1)

**(2) Siffar yadda ake imani da ranar lahira:**

Imani da ranar lahira akwai na dunƙule, akwai kuma na rarrabe.

- Dunƙulallen shi ne: Mu yi imani da cewa akwai wata rana da Allah zai haɗa halittun farko da na ƙarshe, domin ya yi musu hisabi, kowa gwargwadon aikinsa, wasu a sa su a aljanna, wasu kuma a sa su a wuta mai ruruwa. Allah ta'ala ya ce:

﴿قُلۡ إِنَّ ٱلۡأَوَّلِينَ وَٱلۡأٓخِرِينَ ۝٤٩ لَمَجۡمُوعُونَ إِلَىٰ مِيقَٰتِ يَوۡمٖ مَّعۡلُومٖ ۝٥٠﴾ [سورة الواقعة:الآيتان ٤٩-٥٠].

Ma'ana: ((Ka ce (da su) haƙiƙa halittun farko da na ƙarshe, lallai za a tattara su a wani yini sananne)). (Waƙi'a: 49-50)

- Shi kuwa imanin dalla-dalla da ranar lahira; yana nufin mutum ya yi imani da abubuwan da suke faruwa bayan mutuwa dalla-dalla, wannan ɗin ya ƙunshi abubuwa daban-daban, daga cikinsu akwai:

- **Na farko:** Fitinar Kabari: Ana nufin tambayar da ake

yi wa mamaci bayan an binne shi game da Ubangijinsa, addininsa, da kuma annabinsa Muhammadu (s.a.w), a nan ne Allah zai tabbatar da harshen muminai su faɗi tabbatacciya kuma ingatacciyar Magana, kamar yadda ya zo a cikin hadisi, cewa idan an tambayi mumini zai ce:

"ربي الله ، وديني الإسلام، ونبي محمد ﷺ." [متفق عليه].

Ma'ana: "Ubangijina shi ne Allah, addinina shi ne musulunci, annabina kuma Muhammadu (s.a.w)". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

To ya wajaba a yi imani da abubuwan da hadisai suka nuna na batun tambayar Mala'iku guda biyu da yadda tambayar za ta kasance, da amsar da mumini zai bayar, da kuma wacce munafiki zai bayar.

**- Abu na biyu:** Azaba da Ni'imar Kabari: Wajibi ne mutum ya yi imani da azaba da kuma ni'imar da ke kasancewa a cikin kabari, da kasancewar kabari ko dai ya zamanto rami ne daga ramukan wuta, ko ya zamanto dausayi daga dausayan aljanna. Haka nan ya wajaba a yi imani da cewa kabari shi ne masauki na farko daga masaukan lahira; saboda haka duk wanda ya samu tsira a cikin kabari, to albishara ce da cewa abin da yake bayansa zai zamanto mai sauƙi ne sama da shi. Wanda kuwa bai ci nasara ba a kabarinsa to abin da zai biyo bayansa zai zamanto masa mafi tsanani. Kuma duk wanda ya mutu to kamar an yi masa tashin ƙiyama ne.

Ni'imar kabari da kuma azabarsa suna faruwa kan jiki da rai gabaɗaya, wani zubin kuma kan rai kaɗai abin ke afkawa banda gangar jiki.

Azaba dai ta waɗanda suka afka cikin zalunci ne (ga kansu ko waninsu), ita kuwa ni'ima rabon muminan gaske ce.

Matacce dai ana yi masa azaba kuma ana ni'imtar da shi a rayuwar "barzakhu" (tsakanin duniya da lahira) ko an

binne shi ko ba a binne shi ba; saboda haka ko da ƙona mutum aka yi ko aka nitsar da shi cikin ruwa ko namun dawa ko tsuntsaye suka cinye shi, to wannan duka ba ya hana ya sadu da azabar ko ni'imar.

Allah ta'ala ya ce:

ا ٱلنَّارُ يُعۡرَضُونَ عَلَيۡهَا غُدُوّٗا وَعَشِيّٗاۖ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ أَدۡخِلُوٓاْ ءَالَ فِرۡعَوۡنَ أَشَدَّ ٱلۡعَذَابِ ﴿٤٦﴾ ﴾ [سورة غافر:الآية ٤٦].

Ma'ana: ((Wuta ce za a riƙa bijirar da su gareta safe da yamma, ranar da alƙiyama kuma ta tashi(sai a ce): "Ku shigar da jama'ar Fir'auna (tare da shi) a cikin mafi tsananin azaba")). (Gafir: 46)

Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"فلولا أن لا تدافنوا لدعوت الله أن يسمعكم من عذاب القبر." [رواه مسلم].

Ma'ana "Da ba don kada ku dena binne junanku ba da na roƙi Allah ya jiyar da ku wani abu daga azabar kabari". Muslim ne ya ruwaito shi.

- **Abu na Uku:** Busa Kaho: Wani Kaho ne da Israfilu (alaihis salam) zai busa (sau biyu); busawa ta farko kowa da komai zai mutu in banda wasu 'yan abubuwa da Allah ya so togace su, sai kuma ya yi busa ta biyu, wacce za ta tasar da dukkanin halittun Allah tun daga farkon duniya har ran da ta ƙare.

Allah ta'ala ya ce:

ا وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِ فَصَعِقَ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا مَن شَآءَ ٱللَّهُۖ ثُمَّ نُفِخَ فِيهِ أُخۡرَىٰ فَإِذَا هُمۡ قِيَامٞ يَنظُرُونَ ﴿٦٨﴾ ﴾ [سورة

الزمر:الآية ٦٨].

Ma'ana: ((Kuma aka busa ƙaho, take sai duk waɗanda ke sama da ƙasa suka mutu, in banda wanda Allah ya so (rayuwarsu), sannan sai aka ƙara wata busar, take kuma sai ga su a tsaitsaye suna kallo)). (Zumar: 68)

Manzon Allah (s.a.w) ya ce (a cikin wani hadisi):

"ثم ينفخ في الصور فلا يسمعه أحد إلا أصغى لِيتاً ورفع لِيتاً، ثم لا يبقى أحد إلا صعق، ثم ينزل الله مطراً كأنه الطَّلّ، فتنبت منه أجساد الناس، ثم ينفخ فيه أخرى فإذا هم قيام ينظرون." [رواه مسلم].

Ma'ana: ".. Sannan za a busa ƙaho, babu wanda zai ji shi sai ya yi layi, to daga nan babu wani mai rai sai ya mutu, sai waɗanda Allah ya so (ya togace) sannan sai Allah ya saukar da ruwa kamar yayyafi, sai jikkunan mutane su tsiro, sai kuma a ƙara busa ƙaho take, kuma sai mutane su tashi tsaye suna kallo". Muslim ne ya ruwaito shi.

**- Abu Na huɗu:** Tashi (bayan mutuwa): Wannan yana nufin cewa Allah zai raya matattu a lokacin da aka busa ƙaho busa ta biyu, sai kowa ya tashi gaba ga Ubangijin halittu. Idan Allah ya yi izini da busa ƙaho, ya kuma ba wa rayuka izinin su koma cikin jikkunansu, lokacin ne mutane za su tashi daga cikin kaburburansu sai kuma su kama hanya da sauri zuwa ga matsaya (ko dandalin alƙiyama), za su yi wannan tafiya ƙafafunsu tsirara babu takalma, jikkunansu ma tsirara babu sitira, suna masu loɓa wato ba mai sha (kaciya), mawofinta; babu komai na duniya tare da su, nan za su tsaya lokaci mai tsawo, rana kuma ta kusance su a kuma ƙara mata zafi, gumi kuma zai takurawa kowa saboda tsananin wannan matsaya; wani guminsa zai kai masa idon sawunsa, wani kuma guiwarsa, wani zuwa ƙugunsa, wani zuwa ƙirjinsa wajen nonuwansa, wani kuma zuwa kafaɗunsa, kai wani ma zufar tasa har sai ta kai bakinsa ta yi masa linzami, kowa dai gwargwadon aikinsa.

Tashi bayan mutuwa dai gaskiya ne ya tabbata cikin shari'a, kuma abu ne da kowa ke iya gane shi da idonsa da hankalinsa.

- A shar'ance dai: Ayoyi masu yawa cikin Alƙur'ani da ingatattun nassoshin hadisai duka sun tabbatar da wannan al'amari.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ قُلْ بَلَىٰ وَرَبِّى لَتُبْعَثُنَّ ﴾ [سورة التغابن:الآية ].

Ma'ana: ((Ka ce (musu): tabbas ne, na kuma rantse da Ubangijina, tabbas lallai za a tashe ku (bayan mutuwa) )). (Tagabun: 7)

Haka nan Allah ta'ala ya ce:

﴿ كَمَا بَدَأْنَآ أَوَّلَ خَلْقٍ نُّعِيدُهُۥ ﴾ [سورة الأنبياء:الآية ١٠٤].

Ma'ana: ((Kamar yadda muka ƙagi halittu (haka) za mu maido da su)). (Anbiya: 104)

Haka nan Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"ثم ينفخ في الصور فلا يسمعه أحد إلا أصغى ليتاً ورفع ليتاً، ثم لا يبقى أحد إلا صعق، ثم يترل الله مطراً كأنه الطل، أو الظل ــ شك الراوي ــ فتنبت أجساد الناس، ثم ينفخ فيه أخرى فإذا هم قيام ينظرون." [رواه مسلم].

Ma'ana: ".. Sannan za a busa ƙaho, to babu wanda zai ji shi har sai ya yi layi, daga nan kuma duk wanda ya rage a duniya zai mutu, face wanda Allah ya so (togacewa), sai kuma Allah ya saukar da ruwa kamar yayyafi, ko ya ce ne kamar inuwa –mai riwaya ne ya yi kokwanto-, sai jikkunan mutane su tsiro, sai kuma a ƙara busa ƙaho, take kuma sai mutane su tashi tsaye suna kallo". Muslim ne ya ruwaito shi 4/2259.

Haka nan Allah ya ce:

ا قَالَ مَن يُحۡيِ ٱلۡعِظَٰمَ وَهِيَ رَمِيمٞ ﴿٧٨﴾ قُلۡ يُحۡيِيهَا ٱلَّذِيٓ أَنشَأَهَآ أَوَّلَ مَرَّةٖۖ وَهُوَ بِكُلِّ خَلۡقٍ عَلِيمٌ ﴿٧٩﴾ ﴾ [سورة يس:الآيتان ٧٨-٧٩].

Ma'ana: ((.. Ya ce wa (ya isa) ya raya ƙasusuwa alhali suna rududdugaggu? Ka ce (da su): Wanda ya ƙirƙire su tun farkon fari shi ne wanda zai rayar da su, kuma shi mai cikakken sani ne game da duk wani abun halitta)). (Yasin: 78 – 79)

- Abin da kuma ya shafi tabbatuwar tashin matattu ta fuskar abin da ido ke iya gani: shi ne kamar abin da Allah ya nuna wa bayinsa suka gani ganin idonsu yadda yake tashin matattu. A cikin suratul Baƙara akwai misalai guda biyar da suke nuna hakan. Misalan su ne: Mutanen Annabi Musa waɗanda Allah ya raya su bayan ya kashe su, da kuma wanda Banu Isra'ila suka kashe shi, sai kuma mutanen da suka fita daga gidajensu domin gudun mutuwa, da kuma wanda ya wuce ta wajen wata alƙaryar da ta rushe ta zama kango, sai kuma tsuntsayen Annabi Ibrahim (alaihis salam).

- Tabbatarwar hankali ga wannan aƙida ta tashin matattu bayan mutuwa; zai iya bayyanuwa ta fuska biyu:

a- Kasancewar Allah ta'ala shi ne wanda ya fari sammai da ƙassai da abin da ke cikinsu, Allah ne ya halicce su tun farko; wanda kuwa ya fari abu bayan babu shi, ba zai gagare shi ba ya dawo da shi.

b- Cewa ƙasa tana kasancewa a mace a ƙeƙashe babu wata rayuwa a cikinta sai Allah ya saukar da ruwa daga sama sai ta girgije ta rayu ta zama koriya shar, ta cika da duk wani nau'i na tsirrai masu ban sha'awa. To wanda yake da ikon raya ƙasa kamar haka bayan ta gama mutuwa, a fili yake cewa zai iya raya matattu.

- **Abu Na biyar** cikin imani da ranar lahira: Tattara

mutane a waje guda da yi musu hisabi da kuma sakamako: Ya wajaba mu yi imani da cewa za a tattara halittu a tattambaye su (kan ayyukansu) a kuma tsaida adalci a tsakaninsu a kuma ba su sakamakon ayyukansu. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَحَشَرۡنَٰهُمۡ فَلَمۡ نُغَادِرۡ مِنۡهُمۡ أَحَدٗا ﴾ [سورة الكهف:الآية ٤٧].

Ma'ana: ((Kuma (za) mu tara su ba (tare da) mun bar kowa ba daga cikinsu)). (Kahfi: 47)

Ya ƙara da cewa:

﴿ فَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ فَيَقُولُ هَآؤُمُ ٱقۡرَءُواْ كِتَٰبِيَهۡ ١٩ إِنِّي ظَنَنتُ أَنِّي مُلَٰقٍ حِسَابِيَهۡ ٢٠ فَهُوَ فِي عِيشَةٖ رَّاضِيَةٖ ٢١ ﴾ [سورة الحاقة:الآيات ١٩-٢١].

Ma'ana: ((Amma duk wanda aka ba wa littafinsa a hannunsa na dama, zai ce (da na kusa da shi): "Ku karɓa ku karanta littafina, haƙiƙa ni na tabbata cewa (haka) zan haɗu da sakamakona", to (haka) zai zama cikin rayuwa yardajjiya)). (Al-haƙƙa: 19-21)

Ya kuma ce:

﴿ وَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِمَالِهِۦ فَيَقُولُ يَٰلَيۡتَنِي لَمۡ أُوتَ كِتَٰبِيَهۡ ٢٥ وَلَمۡ أَدۡرِ مَا حِسَابِيَهۡ ٢٦ ﴾ [سورة الحاقة:الآيتان ٢٥-٢٦].

Ma'ana: ((Amma kuwa wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na hagu, sai ya ce: "Kaitona ina ma da ba a ba ni littafina ba! Kuma ban san menene sakamakona ba!)).

Shi dai "Hashru" shi ne kora mutane da kuma tattara su a matsaya (dandalin hisabi) domin yi musu hisabi. Banbanci tsakanin "Ba'as" (tashin matattu) da kuma "Hashru" (tattara halittu) cewa na farko ma'anarsa mayar da rayuka zuwa ga jukkunansu, ita kuwa kalmar ta biyu "Hashru" tana nufin

kora waɗanda aka dawo musu da rayukansu da kuma tattarasu waje guda shi ne dandalin hisabi.

Shi kuwa hisabi da sakamako: shi ne tsayarwar da Allah ke wa bayinSa a gaba gare shi ya sanar da su ayyukansu da suka aikata. To su muminai masu kiyaye dokokin Allah hisabinsu shi ne a nuna musu ayyukansu har su gane irin ni'imar da Allah ya yi musu da ya suturce musu su a duniya, da kuma yafe musu su da ya yi a lahira, kuma za a tashe su kowa gwargwadon imaninsa, mala'iku za su tarbe su suna masu yi musu albishir da aljanna, suna kuma kwantar musu da hankulansu dangane da firgici da tashin hankalin da ke cike da wannan rana mai tsanani, sai fuskokinsu su haskaka, haka za su kasance masu haske da murmushi da nuna albushara.

Amma masu ƙaryatawa da bijire wa (Allah) za a yi musu hisabi mai tsanani tare da bin diddigin duk wata ƙwaya ƙarama da babba, za kuma a dinga jansu a bisa fuskokinsu ranar alƙiyama domin wulaƙantawa gare su da kuma ba su sakamakon abin da suka gabatar, da kuma ƙaryatawar da suka yi (ga Allah).

Mutane na farko da za a yi wa hisabi su ne wannan al'umma ta Annabin mu Muhammad (s.a.w), a cikinsu kuma da akwai mutum dubu saba'in da za su shiga aljanna ba tare da hisabi ko azaba ba; saboda kamalar tauhidinsu, kamar yadda Annabi (s.a.w) ya siffanta su da cewa:

"لا يسترقون، ولا يكتوون، ولا يتطيرون، وعلى ربـــهم يتوكلون."

Ma'ana: ".. Su ne waɗanda ba sa neman a yi musu tofi, ba sa yin lalas, ba sa camfi, kuma ga Allah kaɗai suke dogaro". Daga cikin waɗannan mutanen da akwai sahabin nan mai daraja: "Ukkashatu ɗan Mihsan" Allah ya ƙara masa yarda.

Abu na farko da za a yi hisabi a kansa, cikin abubuwan da suka shafi haƙƙoƙin Allah shi ne: Sallah, abin da ya

shafi haƙƙoƙin mutane kuma za a fara ne da: abin da ya shafi jini.

**- Abu Na shida** cikin imanin dalla-dalla da ranar lahira shi ne: Tafki.

Muna imani da tafkin Annabi (s.a.w), shi kuwa tafki ne mai girma, kuma mashaya ce mai daraja, da ake kwararo wa daga ruwan aljanna, daga kogin "Al-Kausara" zuwa dandalin tashin alƙiyama, muminan al'ummar Annabi Muhammadu (s.a.w) kuma su ne za su sha daga gare shi.

Yana daga cikin siffofinsa cewa ya fi nono fari, ya fi ƙanƙara sanyi, ya fi zuma zaƙi, kuma ya fi al-miski ƙanshi, yana da girma matuƙa da gaske; faɗinsa da tsawonsa duka ɗaya ne, tsakanin kowace kusurwarsa da mai binta ya kai tafiyar wata guda, akwai indararai guda biyu, suna kawo masa madadi (ƙarin ruwa) daga aljanna, kofinansa kuwa sun fi yawan taurarin sararin samaniya, duk wanda ya sha shi sau ɗaya ba zai ƙara jin ƙishi ba har abada.

Annabi (s.a.w) ya ce:

"حوضي مسيرة شهر، ماؤه أبيض من اللبن، وريحه أطيب من المسك، وكيزانه كنجوم السماء، من شرب منه فلا يظمأ أبداً." [رواه البخاري].

Ma'ana: "Tafkina (girmansa) ya kai tafiyar wata, ruwansa ya fi nono fari, ƙanshinsa kuma ya fi na al-miski, kofinansa kuma kamar yawan taurarin sama, wanda duk ya sha daga cikinsu ba zai ƙara jin ƙishi ba". (Bukhari ne ya ruwaito shi)

**- Abu na Bakwai cikin imani da lahira** shi ne: Ceto:

A lokacin da bala'i ya tsananta ga mutane a dandalin nan mai girma (na tashin alƙiyama), kuma zamansu ya tsawaita a cikinsa, sai su shiga ƙoƙarin neman wanda zai cece su a wajen Ubangijinsu domin ya tseratar da su daga baƙƙan

cikin wannan guri da kuma tsananinsa. A nan ne dukkanin manya-manyan annabawan nan masu azama za su ba wa mutane uzuri, har sai sun tuƙe zuwa wajen cikamakin Manzanni Annabinmu Muhammadu (s.a.w), wanda shi da ma Allah ya gafarta masa dukkanin zunubansa na farko da na ƙarshe, nan take sai ya ɗauki matakin da dukkanin halittun farko da na ƙarshe za su yaba masa a kan sa, kuma a nan girman matsayinsa da maɗaukakiyar darajarsa za su bayyana; zai tafi ƙarƙashin al'arshin Allah ya faɗi ya yi gaisuwa (sajada), a nan gurin Allah zai kimsa masa wasu kalmomi na yabo ga Allah da zai yabe shi da su ya yi masa kirari da girmama shi, sannan ya nemi izini sai a ba shi damar ceton dukkanin halittun Allah kan cewa a yi musu hukunci (kowa ya san matsayinsa), bayan sun sha damuwa da baƙin cikin da ya fi ƙarfinsu.

Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"إن الشمس تدنو يوم القيامة حتى يبلغ العرق نصف الأذن، فبينما هم كذلك، استغاثوا بآدم ثم بإبراهيم ثم بموسى ثم بعيسى ثم بمحمد صلى الله عليه وسلم، فيشفع ليقضى بين الخلق، فيمشي حتى يأخذ بحلقة الباب، فيومئذ يبعثه الله مقاماً محموداً يحمده أهل الجمع كلهم." [رواه البخاري].

Ma'ana: "Haƙiƙa rana za ta sauko kurkusa da mutane ranar alƙiyama, har zufa ta kai (wa wasu) rabin kunne, suna cikin wannan hali sai su je su nemi ɗaukin Adamu sannan Ibrahim, sannan Musa, sannan Isa, sannan Muhammadu (Allah ya ƙara salati da salami a gare su baki ɗaya), sai ya cece su kan a yi musu hisabi, zai tafi har sai ya je ya riƙe ƙofa. To a wannan ranar ce Allah zai tashe shi a matsayin nan abin yabo, wanda duk halittun da ke wannan taron za su yaba masa". Bukhari ne ya ruwaito shi.

Wannan babban ceto Allah ya keɓance shi ga ManzonSa (s.a.w) shi shi kaɗai. Ya kuma tabbata cewa yana da wasu damammakin na ceto su ne:

1- Ceton da zai yi wa 'yan aljanna kan a ba su izinin shiga cikinta. Dalilin wannan nau'in ceto shi ne faɗin Manzon Allah (s.a.w) inda ya ce:

"آتي باب الجنة يوم القيامة فأستفتح، فيقول الخازن من أنت؟ قال فأقول محمد، فيقول بك أمرت لا أفتح لأحد قبلك." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Zan je ƙofar aljanna ranar alƙiyama, sai in nemi a buɗe mini, sai mai tsaronta ya ce: wanene kai? Sai in ce "Muhammadu ne", sai ya ce: "Kai da ma aka ce kar in buɗe wa wani aljanna ya shige ta gabaninka". Muslim ne ya ruwaito shi.

2- Ceton da zai yi wa mutanen da kyawawa da munanan ayyukansu suka yi daidai, sai Annabi (s.a.w) ya cece su a shigar da su aljanna. Wasu malamai ne suka faɗi wannan nau'in na ceto, amma babu wani hadisi ingatacce a kansa daga Annabi (s.a.w) ko ma waninsa.

3- Cetonsa ga mutanen da suka cancanci shiga wuta a kan kada a shigar da su ita. Dalilinta shi ne gamemmen lafazin hadisin nan da Annabi ya ce a cikinsa:

"شفاعتي لأهل الكبائر من أمتي." [رواه أبو داود].

Ma'ana: "Cetona (ya tabbata) ga ma'abota manyan zunubai daga cikin al'ummata". Abu Dawuda ne ya ruwaito shi.

4- Ceton da zai yi kan ɗaga darajar 'yan aljanna a cikin aljanna. Dalilinta shi ne faɗin Manzon Allah (s.a.w) da ya ce:

"اللهم اغفر لأبي سلمة وأرفع درجته في المهديين." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Allah ka gafarta wa Abu salamata, ka kuma ɗaga darajarsa a cikin waɗanda ka shiryar". Muslim ne ya

ruwaito shi.

5- Cetonsa ga mutanen da za su shiga aljanna ba tare da an yi musu hisabi ko azaba ba. Dalilinsa shi ne hadisin nan na Ukashatu ɗan Mihsan, wanda ya ba da labarin mutum dubu saba'in da za su shiga aljanna ba tare da an yi musu hisabi ko azaba ba, inda Annabi (s.a.w) ya yi masa addu'a da cewa:

"اللهم اجعله منهم" (متفق عليه).

"Ya Allah ka sa shi a cikinsu". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

6- Ceton da zai yi wa ma'abota manyan zunubai bayan sun shiga cikin wuta kan cewa a fitar da su. Dalilinsa shi ne faɗin Manzon Allah (s.a.w):

"شفاعتي لأهل الكبائر من أمتي." [رواه أبو دواد].

"Cetona (ya tabbata) ga ma'abota manyan zunubai daga cikin al'ummata". Abu Dawuda ne ya ruwaito shi.

Da kuma faɗinsa (s.a.w):

"يخرج قوم من النار بشفاعة محمد ﷺ فيدخلون الجنة يسمون الجهنميين." [رواه البخاري].

Ma'ana: "Wasu mutane za su fito daga wuta a dalilin ceton Muhammadu (s.a.w) sai su shiga aljanna, ana kiransu: "Jahannamawa". Bukhari ne ya ruwaito shi.

7- Cetonsa (s.a.w) ga wanda ya cancanci azaba kan cewa a rage masa tsananinta, kamar cetonsa ga baffansa: Abu ɗalib. Dalilinsa faɗinsa (s.a.w):

"لعله تنفعه شفاعتي يوم القيامة فيجعل في ضحضاح من النار يبلغ كعبيه يغلي منه دماغه." [متفق عليه].

Ma'ana: "Ina fatan cetona a ranar alƙiyama ya amfane shi, a sa shi a cikin wani kwazazzabo na wuta wanda bai wuce idon sawunsa ba, amma kwanyarsa tana tafarfasa".

Ceto ba ya yiyuwa sai da cikar sharaɗai guda biyu:

a- Yardar Allah da mai ceton da wanda za a ceta.

b- Izinin Allah ga shi mai ceton da ya yi ceton.

Allah ta'ala Ya ce:

﴿ وَلَا يَشْفَعُونَ إِلَّا لِمَنِ ٱرْتَضَىٰ ﴾ [سورة الأنبياء:الآية ٢٨]

Ma'ana: ((.. Kuma (su Mala'iku) ba sa ceto sai ga wanda Allah ya yarda (da su) )) (Al-anbiya: 28)

Kuma ya ce:

﴿ مَن ذَا ٱلَّذِى يَشْفَعُ عِندَهُۥٓ إِلَّا بِإِذْنِهِۦ ﴾ [سورة البقرة:الآية ٢٥٥].

Ma'ana: ((Wa ye zai yi ceto a gurinSa (Allah) in ba tare da izininSa ba?)). (Baƙara: 255)

**- Abu na takwas** daga cikin imani da lahira shi ne: Ma'auni:

Ma'auni tabbatacce abu ne da ya wajaba a yi imani da shi. Shi ne abin da Allah zai kafa shi ranar alƙiyama domin auna ayyukan bayi; domin ba su sakamakon ayyukansu, kuma abun ma'uani ne na haƙiƙa, wanda yana da tafuka guda biyu da kuma harshe, ana auna ayyuka da shi, ko kuma takardun ayyukan, ko kuma shi kansa mai ayyukan, wato dukkaninsu akan sa su a ma'auni, duk da yake dai abin da ake izina da nauyinsa ko rashin nauyinsa kawai shi ne aikin, banda zatin me aikin ko takardarsa.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَنَضَعُ ٱلْمَوَٰزِينَ ٱلْقِسْطَ لِيَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ فَلَا تُظْلَمُ نَفْسٌ شَيْـًٔا ۖ وَإِن كَانَ مِثْقَالَ حَبَّةٍ مِّنْ خَرْدَلٍ أَتَيْنَا بِهَا ۗ وَكَفَىٰ بِنَا حَٰسِبِينَ ﴿٤٧﴾ ﴾ [سورة الأنبياء:الآية ٤].

Ma'ana: ((Za mu kuma sanya ma'aunai na gaskiya a ranar

alƙiyama; saboda haka babu wanda za a zalunta a komai, ko da kuwa ya kasance gwargwadon ƙwayar komayya ne za mu zo da shi, kuma mun isa masu hisabi!)). (Anbiya: 47)

Haka nan Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَٱلْوَزْنُ يَوْمَئِذٍ ٱلْحَقُّ ۚ فَمَن ثَقُلَتْ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُو۟لَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ۝٨ وَمَنْ خَفَّتْ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُو۟لَـٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُم بِمَا كَانُوا۟ بِـَٔايَـٰتِنَا يَظْلِمُونَ ۝٩ ﴾ [سورة الأعراف:الآيتان ٨-٩]

Ma'ana: ((Awo a wannan ranar daidai ne dukkaninsa; saboda haka waɗanda duk ma'aunansu suka nauyaya to sun zama masu babban rabo. Wanda kuma ma'aunansu suka yi sakayau to waɗannan su ne suka yi asarar kawunansu (rayuwarsu) saboda kasancewarsu masu zalunci (jayayya) da ayoyinmu)). (A'raf: 8-9)

Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"الطهور شطر الإيمان، والحمد لله تملأ الميزان." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Tsarki shi ne rabin imani, "Alhamdu lil lahi" kuma tana cika ma'auni". Muslim ne ya ruwaito shi.

Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"يوضع الميزان يوم القيامة فلو وزن فيه السماوات والأرض لوسعت." [رواه الحاكم].

Ma'ana: "Za a sanya ma'auni ranar alƙiyama, to da za a auna sama da ƙasa a cikinsa da ya ishe su". Hakim ne ya ruwaito shi.

**- Abu na tara a cikin imani da lahira:** shi ne: Siraɗi.

Muna imani da siraɗi, shi kuwa wata gada ce da aka kafa ta a bisa doron bayan wutar Jahannama, kuma hanya ce mai ban tsoro da razani, mutane duka za su bi ta kansa zuwa

aljanna, a cikinsu akwai wanda zai shuɗe kamar ƙyaftawa, wani kuma kamar walƙiya, wani kamar iska, wani kamar tsuntsu, wani kamar ingarmar doki, wani kamar gudun maza, yana sassarfa sosai, ƙarshen masu wucewa kuwa jan gindi yake da ƙyar, kowa zai wuce ne gwargwadon aikinsa, har a zo kan wanda zai wuce haskensa gwargwadon babban yatsan ƙafarsa ne kawai, akwai ma wanda za a wafce shi a jefa shi cikin wuta, wanda kuwa duk ya tsallake siraɗi to zai shiga aljanna.

Mutum na farko da zai tsallake siraɗi shi ne Annabinmu (s.a.w) sannan sauran al'ummarsa. A wannan ranar kuma babu mai iya magana sai annabawa, su ma kuma addu'a kaɗai suke yi, suna cewa: "Allah kare, Allah kare", a cikin Jahannama kuma da akwai wasu tarkuna suna kafe a gefukan siraɗi, babu wanda ya san yawansu sai Allah sai su yi ta waftar wanda duk Allah ya so (zai halakar) daga cikin halittunSa.

Daga cikin siffofinsa: kasancewarsa ya fi takobi kaifi, ya kuma fi gashi siranta, ga shi da santsi, babu wata ƙafa da za ta iya dogewa a kansa sai dai wanda Allah ya tabbatar da shi, kuma za a kafa shi ne a cikin duhu, za a turo amana da zumunci su tsaya a kuiɓunan siraɗi don su yi sheda ga wanda ya kula da su ko ya tozarta su.

Allah ta'ala ya ce:

ا وَإِن مِّنكُمۡ إِلَّا وَارِدُهَاۚ كَانَ عَلَىٰ رَبِّكَ حَتۡمٗا مَّقۡضِيّٗا ﴿٧١﴾

ثُمَّ نُنَجِّي ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّنَذَرُ ٱلظَّٰلِمِينَ فِيهَا جِثِيّٗا ﴿٧٢﴾ ﴾ [سورة مريم:الآيتان ٧١-٧٢].

Ma'ana: ((Babu kuma wanda a cikinku ba zai gangara ta wajenta ba (wato Jahannama). (Wannan) ya zamanto wajibi ne (kuma) zartaccen hukunci ne a wurin Ubangijinka. Sannan kuma za Mu tseratar da waɗanda suka ji tsoron

(Allah) Mu kuma bar kafirai a duddurƙushe cikinta (wato Jahannama) )). (Maryam: 71-72)

Manzon Allah (s.a.w) kuma ya ce:

"ويضرب الصراط بين ظهراني جهنم فأكون أنا وأمتي أول من يجيزه." [رواه مسلم].

Ma'ana: ".. Za a aje siraɗi a tsakiyar wuta, sai in zamanto ni da al'ummata mu ne na farkon tsallakawa".

Haka nan ya ce:

"ويضرب جسر جهنم .. فأكون أول من يجيز، ودعاء الرسل يومئذ: اللهم سلّم سلّم." [متفق عليه].

Ma'ana: ".. Za a sanya gadar jahannama .. sai in zamanto mutum na farko da zai tsallake ta, addu'ar manzanni a wannan rana ita ce: "Allah kare, Allah kare". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Abu Sa'idil khuduri (r.a) ya ce:

"بلغني أن الجسر أدق من الشعر وأحد من السيف." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Labari ya iske ni cewa gadar nan (ta siraɗi) ta fi gashi siranta, kuma ta fi takobi kaifi". Muslim ne ya ruwaito shi.

A wani hadisin kuma Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"وترسل الأمانة والرحم، فتقومان على جنبي الصراط يميناً وشمالاً، فيمر أولكم كالبرق... ثم كمرّ الريح، ثم كمرّ الطير وشد الرجال، تجري بهم أعمالهم، ونبيكم قائم على الصراط يقول: رب سلم سلم، حتى تعجز أعمال العباد، حتى يجئ الرجل فلا يستطيع السير إلا زحفاً. قال: وعلى حافتي الصراط كلاليب معلقة مأمورة بأخذ من أمرت به، فمخدوش ناجٍ، ومكدوس في النار." [رواه مسلم].

Ma'ana: ".. Kuma za a turo "amana" da "zumunci" su zo su tsaya a kan gefukan siraɗin; damansa da hagunsa, sai na farkonku su shuɗe kamar walƙiya .. wasu kuma kamar iska .. wasu kamar tsuntsu da kuma wasu kamar gudun mazaje, kowa aikinsa ne zai gudanar da shi, shi kuwa Annabinku yana tsaye bisa siraɗin yana ta addu'a: Allah ka kare, Allah ka kiyaye, har dai ayyukan bayi su gaza, har a kai matsayin da mutum zai zo ya kasa tafiya sai dai da jan ciki", ya ce: "A geffan siraɗin akwai wasu tarkuna a rataye, an sa su su kama duk wanda aka sa su kama shi, wani za a yakuso shi ya sha da kyar, wani kuwa za a yi kif da shi a cikin wuta". Muslim ne ya ruwaito shi.

**- Abu na goma cikin imani da ranar lahira** shi ne: Gada.

Muna imani da cewa muminai idan suka tsallake siraɗi za kuma su tsaya a kan gada, wani guri da ke tsakanin aljanna da wuta, za a tsaida muminan da suka tsallake siraɗi suka kuɓuta daga azabar wuta a cikinsa; domin a gudanar da ƙisasi a junansu kafin a shiga aljanna, idan aka tsaftace su aka kuma tsarkake su to a sannan sai a ba su izinin shigewa aljanna.

Annabi (s.a.w) ya ce:

"يخلص المؤمنون من النار، فيحبسون على قنطرة بين الجنة والنار، فيقتص لبعضهم من بعض مظالم كانت بينهم في الدنيا، حتى إذا هذبوا ونقوا أذن لهم في دخول الجنة، فوالذي نفس محمد بيده لأحدهم أهدى بمنـــزله في الجنة منه بمنـــزله كان في الدنيا." [رواه البخاري].

Ma'ana: "Muminai za su kuɓuta daga wuta, sai kuma a tsare su a kan wata gada da ke tsakanin aljanna da wuta, sai a yi fanshesheniya a tsakaninsu na duk wani zalunci da ke tsakaninsu a duniya, har sai an tsaftace kuma an tsarkake su sai a yi musu izinin shiga aljanna. Na rantse da wanda raina

ke hannunSa, tabbas kowanne ɗaya daga cikinsu zai gane gidansa na aljanna sama da yadda yake gane gidansa na duniya". Bukhari ne ya ruwaito shi.

**- Abu na goma sha-ɗaya a cikin imani da ranar lahira shi ne: Aljanna da Wuta.**

Muna imani da cewa aljanna gaskiya ce, haka wuta ma gaskiya ce, haka nan da kasancewar suna nan yanzu a same, ba kuma za su ƙare ba, ba za su lalace ba, za su ci gaba da wanzuwa, ni'imar da ke cikin aljanna ba za ta ƙare ba, ba kuma za ta gushe ba, azabar 'yan wuta irin waɗanda Allah ya hukunta musu dawwama a cikinta suma azabarsu ba za ta ƙare ba kuma ba za ta yanke ba.

Su kuwa masu kaɗaita Allah; za su fita daga wuta da ceton masu ceto da kuma rahamar sarkin masu rahama.

Aljanna dai gida ne na karamci, wanda Allah ya tanade shi ga masu bin tsarinSa ranar alƙiyama, a cikinta da akwai ƙoramai masu gudana, da benaye masu tsawo, da mata kyawawa, a cikinta akwai abin da rayuka suke sha'awa, idanu kuma suke daɗaɗa da ganinsu na daga abubuwan da idanu ba su taɓa gani ba, idanu ba su taɓa ji ba, bai kuma taɓa ɗarsuwa a cikin zuciyar wani ɗan Adam ba, ni'imar aljanna ba ta ƙarewa, ba kuma ta yankewa, suna cikinta a dawwame babu tsinkewa. Kai! Gwargwadon gurin aje bulala (ta dukan dabba) ya fi duniya da abin da yake cikinta. Ana kuma jin ƙanshinta tun ana nisan shekara arba'in da ita. Mafi girman ni'imar da ke cikin aljanna ita ce ni'imar ganin Allah da muminai za su yi da ƙwayoyin idanunsu.

Amma kafirai: ana kange su ga barin ganin Ubangijinsu, saboda haka wanda ya kore ganin muminai ga Ubangijinsu to ya daidaita su ke nan da kafirai a wannan haramtawar da za a yi wa kafiran.

A aljanna da akwai darajoji guda ɗari, tsakanin kowacce daraja da mai binta ya kai abin da ke tsakanin sama da ƙasa.

Kololuwar aljanna ita ce aljannar "Firdausi", al'arshin Sarkin rahama kuma shi ne rufin soronta. Kuma tana da ƙofofi takwas, abin da ke tsakanin ƙyamaran ƙofar ya kai nisan da ke tsakanin Makka da Hajar, amma akwai lokacin da zai zo ya zamanto ya cushe don yawan masu shiga. Ɗan autan 'yan aljanna a irin darajojinsu shi ne wanda aka ba shi kwatankwacin duniya da ninkinta goma.

A game da aljanna Allah ta'ala ya ce:

﴿ أُعِدَّتْ لِلْمُتَّقِينَ ﴾ [سورة آل عمران:الآية ١٣٣] .

Ma'ana: ((An shirya ta ne domin masu taƙawa)). (Ali Imran: 133)

A kan dawwamar 'yan aljanna da kuma dawwamar ita aljannar ya ce:

﴿ جَزَآؤُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّـٰتُ عَدْنٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَـٰرُ خَـٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۖ رَّضِىَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ ۚ ذَٰلِكَ لِمَنْ خَشِىَ رَبَّهُۥ ﴿٨﴾ ﴾ [سورة البينة:الآية ٨]

Ma'ana: ((Sakamakonsu a wajen Ubangijinsu shi ne aljannatan zama waɗanda ƙoramai suke gudu a ƙarƙashinsu a cikinta za su yi ta dawwama har abada, Allah ya yarda da su suma kuma sun yarda da shi, wannan (sakamakon) yana tabbata ne ga duk wanda ya tsoraci Ubangijinsa)). (Bayyina: 8)

Ita kuwa wuta gida ne na azaba wanda Allah ya tanadarwa kafirai da masu saɓo, a cikinta da akwai mafi tsananin azaba da dukkanin dangoginta, masu tsaronta kuma wasu mala'iku ne kaurara ƙarfafa. Kafiran da duk suka shiga wuta to a cikinta za su dawwama, abincinsu wata bishiya ce da ake ce mata "Zaƙƙum", tafasasshen ruwan zafi kuma shi ne ruwansu. Zafin wutar duniya kashi

ɗaya ne daga saba'in ɗin zafin ta lahira, wato ke nan an fifita ta a kan ta duniya da kashi saba'in ba ɗaya, kowanne kaso kamar zafin wannan kashi ɗayan na duniya yake ko ma ya fi shi zafi.

Ita wannan wuta dai ba ta ƙosawa da wanda duk aka sa mata a cikinta, a ka jefa shi a cikin zurfinta, sai ma dai ta ce: "Ko da akwai ƙari?!" Ita ma kuma tana da ƙofofi bakwai, kowace ƙofa tana da daidai kasonta (daga bayi).

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce -a lokacin da yake magana game da wuta-:

ا أُعِدَّتْ لِلْكَٰفِرِينَ ﴾ [سورة آل عمران:الآية ١٣١].

Ma'ana: ((An tanaje ta ne domin kafirai)). (Ali – Imran: 131)

Allah ta'ala ya ce –yayin da yake magana game da dawwamar wuta da kuma bayanin cewa ba za ta ƙare ba-:

ا إِنَّ ٱللَّهَ لَعَنَ ٱلْكَٰفِرِينَ وَأَعَدَّ لَهُمْ سَعِيرًا ﴿٦٤﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ﴾ [سورة الأحزاب:الآيتان ٦٤-٦٥]

Ma'ana: ((Haƙiƙa Allah ya tsine wa kafirai ya kuma tanadar musu wutar Sa'ira. A cikinta za su dawwama har abada)). (Ahzab: 64 – 65)

**(3) Fa'idojin Imani da ranar lahira:**

Imani da ranar lahira yana da fa'idoji masu girma, daga cikinsu:

1- Yana haifar da son ayyukan biyayya, da kwaɗayinsu domin ƙaunar ladar Allah.

2- Tsoron aikata ayyukan da suka saɓa wa Allah ko yarda da su; domin tsoron uƙubar wannan rana.

3- Ɗebe kewar mumini daga duk wani abu da ya rasa na duniya saboda ƙaunar ni'imar lahira da kyakkyawan

sakamakonta.

4- Imani da tashin matattu bayan mutuwa shi ne tushen rabautar ɗaiɗaiku da jama'u; domin kuwa mutum idan ya yi imani da cewa Allah zai tashi halittu bayan mutuwarsu kuma zai yi musu hisabi sannan ya saka wa kowa gwargwadon ayyukansa, ya kuma ɗaukar wa wanda aka zalunta fansa daga wanda ya ci zalinsa ko da kuwa tsakanin dabbobi ne, wannan ƙudurin zai sa mutum ya tsaya kan biyayya ga Allah, zai kuma tunɓuke tushen sharri ya yawaita alheri, ya kuma sa nutsuwa da mutunci su game a cikin zamantakewar mutane.

# RUKUNI NA SHIDA: IMANI DA ƘADDARA

**(1) Ma'anar ƙaddara da kuma muhimmancin imani da ita:**

Kaddara tana nufin: tsarin da Allah ya tsara halittu a kansa, gwargwadon yadda iliminSa ya gabata kuma hikimarSa ta hukunta. Wannan tsari na "ƙaddara" ya samo asali ne daga siffar Allah ta "ƙudura" wato ikonSa da kasancewarSa mai cikakken iko ne kan komai da komai, kuma mai cikakkiyar damar aikata duk abin da ya ga damar aikatawa ne.

Imani da ƙaddara yana daga cikin imani da rububiyar Allah (wato: "UbangijintakarSa") Tsarkakakken Sarki Maɗaukaki, kuma ɗaya ne daga rukunan imani da imanin wani ba zai cika ba sai da su. Allah ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّا كُلَّ شَيْءٍ خَلَقْنَاهُ بِقَدَرٍ ﴾ [سورة القمر:الآية ٤٩] .

Ma'ana: ((Haƙiƙa Mu, kowanne abu mun halicce shi ne da wani tsari (ƙaddara) )). (Kamar: 49)

Annabi (s.a.w) kuma ya ce:

"كل شيء بقدر حتى العجز والكيس، أو الكيس والعجز." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Komai (da Allah ya yi) da wani tsari yake, hatta gazawa (kasala) da kuma ƙoƙari". Muslim ne ya ruwaito shi.

**(2) Matakan Kaddara:**

Imanin mutum da ƙaddara ba ya kammala sai ya tabbatar da wasu matakai guda huɗu:

- **Na farko** dai ya yi imani da cewa Allah yana da ilimi

tun fil azal wanda ya haɗe ya kewaye komai da komai. Allah ta'ala ya ce:

﴿ أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِى ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ ۗ إِنَّ ذَٰلِكَ فِى كِتَٰبٍ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ﴿٧٠﴾ ﴾ [سورة الحج:الآية ٧٠]

Ma'ana: ((Ba ka san cewa Allah ya san duk wani abin da ke cikin sama da ƙasa ba, haƙiƙa wancan (ilimin) yana cikin wani littafi (wato Lauhul Mahfuz), haƙiƙa wancan (ilimin) abu ne mai sauƙi a wajen Allah)). (Haj: 70)

- **Na biyu**: Imani da cewa Allah ya rubuta dukkanin iliminSa na tsare-tsaren halittunSa a cikin "Lauhul Mahfuz". Allah ta'ala ya ce:

﴿ مَّا فَرَّطْنَا فِى ٱلْكِتَٰبِ مِن شَىْءٍ ۚ ﴾ [سورة الأنعام:الآية ٣٨].

Ma'ana: ((Ba mu yi sakacin barin komai ba a cikin littafin nan)). (An'am: 38)

Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"كتب الله مقادير الخلائق قبل أن يخلق السموات والأرض بخمسين ألف سنة." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Allah ya rubuta tsare-tsaren halittu tun kafin ya halicci sama da ƙasa da shekara dubu hamsin". Muslim ne ya ruwaito shi.

- **Na uku:** Imani da cewa abin da Allah ya ga dama shi ne yake zartuwa, kuma shi mai iko ne kan zartar da duk wani abin da yake so. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٩﴾ ﴾ [سورة التكوير:الآية ٢٩].

Ma'ana: ((Ba za ku so (faruwar wani abu) ba sai Allah Ubangijin bayi ya ga damar (faruwarsa) )). (Takwir: 29)

Manzon Allah (s.a.w) kuma da wani ya ce da shi: "Abin da Allah ya so, kai ma ka so (shi za a yi), sai ya ce masa:

"أجعلتني لله نداً ، بل ما شاء الله وحده." [رواه أحمد].

Ma'ana: "Shin yanzu ka mai da ni kini ga Allah ke nan?! Bari wannan zance! Sai dai abin da Allah shi shi kaɗai ya so (shi ne zai faru)". Imam Ahmad ne ya ruwaito shi.

**- Abu Na huɗu:** Imani da cewa Allah shi ne mahaliccin komai, Allah ta'ala ya ce:

﴿ ٱللَّهُ خَـٰلِقُ كُلِّ شَىْءٍ ۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ وَكِيلٌ ﴿٦٢﴾ ﴾

[سورة الزمر:الآية ٦٢].

Ma'ana: ((Allah shi ne Mahaliccin komai, kuma shi ne Mai kula da komai)). (Zumar: 62)

Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَٱللَّهُ خَلَقَكُمْ وَمَا تَعْمَلُونَ ﴿٩٦﴾ ﴾ [سورة الصافات:الآية ٩٦].

Ma'ana: ((Allah ne ya halicce ku da ma duk abin da ku ke aikatawa)). (Saffat: 96)

Manzon Allah (s.a.w) kuma ya ce:

"إن الله يصنع كل صانع وصنعته." [رواه البخاري].

"Haƙiƙa Allah shi ne yake yin kowanne ma'aikaci tare da aikinsa". Bukhari ne ya ruwaito shi.

**(3) Kashe – kashen tsara ƙaddara:**

a- Gamammen tsarin ƙaddara ga dukkanin halittu; wanda aka rubuta a cikin "Lauhul Mahfuz" tun kafin a halicci sammai da ƙassai da shekara dubu hamsin.

b- Tsarin rayuwa; wato tsara abin da zai samu bawa daga ranar da aka busa masa rai har ranar ƙarshe ta rayuwarsa.

c- Tsarin ƙaddarar shekara–shekara, wato tsarin abin da yake gudana a kowace shekara, hakan yana faruwa ne a lailatul ƙadarin kowace shekara. Allah ta'ala ya ce:

﴿ فِيهَا يُفْرَقُ كُلُّ أَمْرٍ حَكِيمٍ ﴾ [سورة الدخان:الآية ٤] .

Ma'ana: ((A cikinta ne (wato daren lailatul ƙadari) ake rarraba duk wani al'amari mai hikima)). (Dukhan: 4)

d- Tsarin yau da kullum, wato tsara abin da ke faruwa kowace rana na ɗaukaka da ƙasƙanta, baiwa da hani, rayawa da kashewa da sauransu. Allah ta'ala ya ce:

﴿ يَسْأَلُهُ مَن فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ كُلَّ يَوْمٍ هُوَ فِي شَأْنٍ ﴾

[سورة الرحمن:الآية ٢٩].

Ma'ana: ((Duk abin da yake cikin sammai da ƙassai bara yake a wurinsa, shi kullum a cikin shu'unai yake)). (Al-Rahman: 29)

### (4) Aƙidar Magabata dangane da ƙaddara:

Sun ƙudurce cewa Allah shi ne Mahaliccin komai da komai, Ubangijinsa kuma Mamallakinsa, Ya tsara duk wasu tsare-tsare na ababan halitta tun kafin ya halicce su, ya ƙaddara musu ajalillikansu, arzukansu da ma ayyukansu, ya kuma rubuta abin da za su tuƙe zuwa gare shi na rabauta ko tsiyata, kai komai Allah ya ƙididdige shi a cikin littafin nan mai bayanin komai (wato Lauhul Mahfuz). Saboda haka abin da Allah ya so shi ne zai faru, wanda kuma bai so ba ba zai taɓa faruwa ba, Ya san abin da ya faru, da abin da yake faruwa, da abin da bai faru ba in da ya faru yaya zai faru. Allah Mai iko ne kan komai, Yana shiriyar wanda Ya so kuma ya ɓatar da wanda Ya so, amma tare da haka su ma bayi suna da tasu damar da ikon aikata abin da Allah ya ba su ikon aikatawa, amma (su magabatanmu na ƙwarai) suna ƙudurce da cewa bayi ba su da wani nufi sai abin da Allah ya nufa. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَالَّذِينَ جَاهَدُوا فِينَا لَنَهْدِيَنَّهُمْ سُبُلَنَا ﴾ [سورة العنكبوت:الآية ٦٩]

Ma'ana: ((Waɗanda duk suka yi ƙoƙari a neman yardarMu, lallai za Mu shiryar da su hanyoyinMu ..)) (Ankabut: 69)

Har ila yau suna ƙudurce cewa: Allah ta'ala shi ne mahaliccin bayi da ayyukansu, tare da cewa su ne suke aikata ayyukan nasu a haƙiƙa, saboda haka babu hujja ga wani mutum kan Allah idan ya bar wani wajibi, ko kuma ya aikata wani haramtaccen aiki, sai dai shi ne ma yake da cikakkiyar hujja a kan bayi, ya dai halatta a kafa hujja da ƙaddara kan masifu, amma ba a kan aibobin (da mu muka sabauta) ko laifuffuka ba. Kamar yadda Manzon Allah (s.a.w) ya faɗa game da jayayyar da Musa da Adamu suka yi:

"تحاج آدم وموسى، فقال موسى: أنت آدم الذي أخرجتك خطيئتك من الجنة؟ فقال له آدم: أنت موسى الذي اصطفاك الله برسالاته وبكلامه، ثم تلومني على أمر قد قُدّر عليّ قبل أن أخلق، فحج آدمُ موسى." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Adamu da Musa sun yi ja-in-ja, sai Musa ya ce: "Kai ne Adamun nan da zunubinka ya fitar da kai daga aljanna[1]?!", sai Adamu ya ce: "Kai ne Musan nan da Allah ya keɓe ka da saƙonSa da maganarSa, sannan kuma ka zo

---

[1] Annabi Musa yana zarginsa ne kan wannan masifa da ta afka masa shi da 'ya'yansa, kasancewar shi ya sabauta ta, wato kamar ya ce ne: me ya sa ka jawo mana wannan bala'i?! Jawabin Annabi Adamu kuma yana nuna cewa ai ita wannan masifa wani abu ne ƙaddararre, shi kuma laifi an riga an tuba daga gare shi kuma an yafe shi, ya za ka zo kana zargina a kan ƙaddararriyar masifa da yafaffen laifi duk saninka da Allah?! Duba: Shifa'ul alil na Ibnul ƙayyim, da Sharhin Ɗahawiyya.

kana zargina a kan abin da aka riga aka ƙaddara shi a kaina tun kafin a halicce ni?" Saboda haka sai Adamu ya rinjayi Musa". Muslimu ne ya ruwaito shi.

### (5) Ayyukan bayi:

Ayyukan da Allah yake halitta a duniya nau'i biyu ne:

1- Na farko dai: shi ne abin da Allah ya ke gudanar da shi na ayyukanSa cikin halittunSa, saboda haka babu wanda yake da zaɓi ko wani ganin dama a cikin irin wannan ayyukan nasa. Nufi a nan na Allah ne shi shi kaɗai. Misalin waɗannan ayyukan; rayawa da kashewa, lafiya da rashinta da makamantansu.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَٱللَّهُ خَلَقَكُمۡ وَمَا تَعۡمَلُونَ ﴾ [سورة الصافات:الآية ٩٦] .

Ma'ana: ((Allah shi ne ya halicce ku, ku da abin da kuke aikatawa)). (Saffat: 96)

Kuma ya ce:

﴿ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلۡمَوۡتَ وَٱلۡحَيَوٰةَ لِيَبۡلُوَكُمۡ أَيُّكُمۡ أَحۡسَنُ عَمَلٗاۚ ﴾

[سورة الملك:الآية ٢].

Ma'anarSa: (( (Shi ne) wanda ya halicci mutuwa da rayuwa domin ya jarrabe ku (ya ga) waye a cikinku ya fi kyakkyawan aiki)). (Mulk: 2)

2- Nau'i na biyu daga ayyukan Allah a duniya: shi ne abin da dukkanin halittu masu nufi (wato masu hankali) su ke aikatawa, irin waɗannan ayyukan suna faruwa ne da zaɓi da kuma nufin waɗanda suke aikata su ɗin; saboda Allah ya halitta musu wannan damar. Allah ta'ala ya ce:

﴿ لِمَن شَآءَ مِنكُمۡ أَن يَسۡتَقِيمَ ﴾ [سورة التكوير:الآية ٢٨].

Ma'ana: ((.. Ga wanda duk ya so ya shiryu daga cikinku)) (Takwir: 28).

Haka nan Allah ya ce:

ا فَمَن شَآءَ فَلۡيُؤۡمِن وَمَن شَآءَ فَلۡيَكۡفُرۡۚ ﴾ [سورة الكهف:الآية ٢٩].

Ma'ana: ((To, duk wanda ya so ya yi imani sai ya yi, wanda kuma yake son aikata kafirci shi ma sai ya yi) (Kahfi: 29)

Saboda haka suna samun yabo kan abin da suka yi na yabo, ana kuma zarginsu in sun yi aikin zargi. Allah dai ba ya uƙuba sai a kan aikin da aka yi shi da nufi da ganin dama. Kamar yadda Allah ya ce:

ا وَمَآ أَنَا۠ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ﴾ [سورة ق:الآية ٢٩].

Ma'ana: ((Kuma Ni ba azzalumi ba ne ga bayi)) (Kaf: 29).

Kowanne mutum dai ya san banbanci tsakanin yin aiki tare da nufi, da kuma yinsa a dole, misali mutum in zai sauko daga kan soro zai bi tsani ne idan da zaɓinsa, mai yiyuwa ne kuma a jefo shi daga kan soron ya faɗo ba shiri, ka ga sauka ta farko shi ne: aiki mai nufi da kuma zaɓi, ta biyun kuma shi ne dole.

**(6) Ya ya za a siffanta abu ɗaya da cewa: halittar Allah ne kuma aikin bawa ne?**

Allah shi ya halicci bawa kuma ya halicci ayyukansa, ya kuma ba shi nufi da iko, saboda haka bawa shi ne yake aikinsa a haƙiƙa, shi ne yake aikata shi da gaɓɓansa; saboda yana da nufi da kuma iko, idan ya yi imani to da ganin damarsa ya yi shi da kuma nufinsa, haka nan idan ya kafirce ya kafirce ne da ganin damarsa da nufinsa cikakke, kamar idan an ce: wannan ɗan itacen daga wannan bishiyar yake, ko kuma: wannan shukar daga wannan ƙasar take, ana nufin sun fito ne daga cikinsu, idan kuma aka ce: daga Allah suke, ana nufin shi ne ya halicce su, babu kuma cin karo tsakanin maganganun guda biyu, irin wannan shi ne

alaƙa tsakanin shari'ar Allah da ƙaddararSa.

Allah ta'ala ya ce:

ﵟوَٱللَّهُ خَلَقَكُمۡ وَمَا تَعۡمَلُونَ ٩٦ﵞ [سورة الصافات:الآية ٩٦] .

Ma'ana: ((Allah shi ne ya halicce ku, ku da abin da kuke aikatawa)). (Saffat: 96)

Haka nan ya ce:

ﵟفَأَمَّا مَنۡ أَعۡطَىٰ وَٱتَّقَىٰ ٥ وَصَدَّقَ بِٱلۡحُسۡنَىٰ ٦ فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلۡيُسۡرَىٰ ٧ وَأَمَّا مَنۢ بَخِلَ وَٱسۡتَغۡنَىٰ ٨ وَكَذَّبَ بِٱلۡحُسۡنَىٰ ٩ فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلۡعُسۡرَىٰ ١٠ﵞ [سورة الليل:الآيات ٥-١٠]

Ma'ana: ((To amma wanda ya yi kyauta ya kuma yi taƙawa. Ya kuma gaskata mafi kyawun kalma (wato: La ilaha illal Lahu), to za mu hore masa (hanya) mai sauƙi. Amma kuma wanda ya yi rowa, ya kuma wadatu, kuma ya ƙaryata mafi kyawun kalma, to da sannu za mu hore masa (hanya) mai wahala)). (Al-Laili: 5-10)

**(7) Abin da ya wajaba bawa ya yi dangane da ƙaddara:**

Abubuwa biyu ne:

- Na farko: Mutum ya nemi taimakon Allah wajen aikata abin da aka ƙadarta masa aikata shi da kuma nisantar abin da aka tsoratar da shi aikata shi, ya kuma roƙi Allah ya hore masa hanya mai sauƙi, ya kuma nisantar da shi mai tsauri, ya dogara da Allah ya nemi tsarinSa, sai ya zamanto mabuƙaci ga Allah wajen janyo alheri da kuma barin sharri. Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

"احرص على ما ينفعك، واستعن بالله ولا تعجز، وإن أصابك شيء فلا تقل: لو أني فعلت كذا لكان كذا، ولكن قل: قدر الله وما شاء فعل،

فإن لو تفتح عمل الشيطان."

Ma'ana: "Ka kiyaye duk abin da zai amfane ka, ka nemi taimakon Allah, kada kuma ka gajiya, idan wani abu ya same ka (na masifa) to kada ka ce: "Da dai kaza na yi da kaza ne ya faru", sai dai ka ce: "Wannan ƙaddarar Allah ce, abin da kuma duk ya so shi ne zai faru"; domin kalmar "Lau" (wato"Dama") tana buɗe aikin Shaiɗan ne".

- Abu na biyu shi ne: ya haƙura da abin da aka ƙaddara masa, kada ya yi raki, ya san cewa wannan wani abu ne daga Allah sai ya yarda ya miƙa wuya. Ya kuma sani cewa duk abin da ya same shi dama can ba zai taɓa kuskure shi ba, abin da kuma ya kuskure masa ba zai taɓa samunsa ba dama. Manzon Allah (s.a.w) ya ce :

"وأعلم أن ما أصابك لم يكن ليخطئك، وأن ما أخطأك لم يكن ليصيبك."

Ma'ana: "Ka sani cewa duk abin da ya same ka dama can ba zai taɓa kuskure ka ba, abin da kuma ya kuskure maka ba zai taɓa samunka ba dama".

(8) **Yarda da hukunci da ƙaddarar Allah**:

Ya kamata a yarda da ƙaddarar Allah; domin yana cikin kamalar yarda da Ubangijintakar Allah (Rububiyya); saboda haka ya kamata duk wani mumini ya yarda da hukuncin Allah; domin aikin Allah da hukuncinSa alheri ne dukkaninsa, adalci ne kuma hikima ne. Wanda ransa ya nutsu da cewa duk abin da ya same shi ba zai kuskure masa ba, kuma abin da ya kuskure masa ba zai taɓa samunsa ba, za ka ga ransa ya tsira daga ruɗani da kaikawo, damuwa da kaɗuwa za su fita daga rayuwarsa, sai ya zamanto ba ya damuwa da abin da ya kufce masa, ba kuma ya tsoron rayuwar da take fuskantarsa, saboda haka zai zamanto yafi kowa morewa, jin daɗI da kwanciyar hankali a rayuwarsa.

Wanda ya san cewa ajalinsa a ƙayyade yake, arzikinsa ma a ƙirge yake, saboda haka ya san tsoro ba zai ƙara masa kwanaki a duniya ba, ƙwauro ma ba zai ƙara masa arzikinsa ba, tun da dai komai a rubuce yake, wanda ya san haka to zai zamanto mai haƙuri kan duk abin da ya same shi daga masifu, ya zamanto kuma mai neman gafara kan abin da ya aikata daga zunubai da aibuka, zai kuma yarda da abin da Allah ya ƙaddara masa, sai ya zamanto ya haɗa tsakanin bin umarni da kuma haƙuri da masifu.

Allah ta'ala ya ce:

﴿ مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ وَمَن يُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ يَهۡدِ قَلۡبَهُۥۚ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١١ ﴾ [سورة التغابن:الآية ١١]

Ma'ana: ((Ba wani abu da zai same (ka) na masifa sai da izinin Allah, duk kuwa wanda ya ba da gaskiya da Allah zai shiryi zuciyarsa. Allah kuma shi ne mai cikakken sanin komai da komai)). (Tagabun: 11)

Haka nan Allah ya ce:

﴿ فَٱصۡبِرۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ ﴾ [سورة غافر:الآية ٥٥].

Ma'ana: ((Ka yi haƙuri, haƙiƙa alƙawarin Allah gaskiya ne, ka kuma nemi gafarar zunubanka)) (Gafir: 55)

(9) Shiriya iri biyu ce:

- **Ta farko**: shiriya mai ma'anar nuna gaskiya da jangora zuwa gare ta, shiriya mai wannan ma'anar dukkanin halittu suna da rabo a cikinta, kuma ita ce abin da manzanni da mabiyansu suke da iko a kansa. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَإِنَّكَ لَتَهۡدِيٓ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ﴾ [سورة الشورى:الآية ٥٢]

Ma'ana: ((Haƙiƙa kai kana shiryarwa zuwa hanya

madaidaiciya)). (Shura: 52)

- **Shiriya ta biyu**: ita ce shiriyar datarwa da tabbatarwa a kan gaskiya; baiwa da falala daga Allah ga bayinSa masu taƙawa. Irin wannan shiriyar babu wani mai iko a kanta sai Allah. Allah ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّكَ لَا تَهْدِى مَنْ أَحْبَبْتَ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَهْدِى مَن يَشَآءُ ۚ ﴾

[سورة القصص:الآية ٥٦].

Ma'ana: ((Haƙiƙa kai ba ka da ikon shiriyar duk wanda kake so, sai dai Allah shi ne mai shiryar da duk wanda ya nufi (shiryarwa) )). (Kasas: 56)

**(10) Iradar Allah (wato NufinSa) a cikin Alƙur'ani iri biyu ne:**

- Na farko: Nufi mai ma'anar halittawa da tsarawa (Kauniya Kadariyya), shi ne nufin Allah da ya game duk wani samammen abu, saboda haka sai abin da Allah ya so zai faru, abin da kuma duk bai so ba ba zai faru ba. Shi irin wannan nufin dole ne ya zamanto tare da afkuwar abin da (Allah) ya nufi afkuwarsa, amma ba dole ne ya zamanto Allah yana son abin ko Yana ƙaunarsa ba, sai dai idan abin ya haɗa irin wannan nufin da kuma nufi iri na biyu (bayaninsa yana zuwa kusa). Allah ta'ala ya ce:

﴿ فَمَن يُرِدِ ٱللَّهُ أَن يَهْدِيَهُۥ يَشْرَحْ صَدْرَهُۥ لِلْإِسْلَٰمِ ۖ ﴾ [سورة الأنعام:الآية ١٢٥].

Ma'ana: ((To, duk wanda Allah ya nufi shiriyarsa sai ya buɗe ƙirjinsa ga (karɓar) musulunci)). (An'am: 125)

1- Ma'ana ta biyu ta "Irada" ita ce: mai nuna cewa abin nufin addini ne kuma shari'a ne, irin wannan iradar tana nufin Allah yana son abin nufin nasa tare da masu aikata shi kuma Ya yarda da su. Irin wannan iradar ba dole ne ta zamanto tare da abin da aka nufa ɗin ba, sai dai idan ya

haɗu da "irada kauniyya". Allah ta'ala ya ce:

ﵟيُرِيدُ ٱللَّهُ بِكُمُ ٱلۡيُسۡرَ وَلَا يُرِيدُ بِكُمُ ٱلۡعُسۡرَﵞ [سورة البقرة:الآية ١٨٥].

Ma'ana: ((Allah yana so muku sauƙi ne, ba kuma ya son tsanani a gare ku)) (Baƙara: 185)

Irada kauniyya (nufi mai ma'anar halittawa) yafi ɗayan nau'in faɗi ta kowace fuska; domin kuwa duk abin nufin shari'a idan ya faru to ya zama abin nufin halitta da tsari, amma ba duk abin da aka nufe shi nufin halitta da tsari ne yake zama abin nufin shari'a ba. Misali: Imanin Abubakar Allah ya ƙara yarda a gare shi, shi duka nau'o'i biyu na nufin Allah sun haɗu a kansa. Misalin kuma abin da nufin halitta ne kurum ya samu a kansa shi ne: kafircin Abu Jahal. Misalin abin da kuma nufin halittawa da tsarawa bai samu a kansa ba -duk da cewa an nufe shi nufin addini da shari'a- shi ne: imanin Abu Jahal. To duk da kasancewar Allah ta'ala ya nufi afkuwar zunubai a cikin tsarinSa, ya kuma ga damar samar da su, sai dai ba ya yarda da su a addinance, ba kuma ya sonsu ba ya umarni da su, ƙinsu ma yake yi da ƙyamarsu, yana kuma hani ga barinsu yana narkon azaba ga mai aikata su, amma duka wannan ba ya fita daga tsarin ƙaddararSa.

Su kuwa ayyukan ɗa'a da imani, Allah yana sonsu yana umarni da su yana kuma yi wa ma'abotansu alƙawarin lada da kyakkyawan sakamako. Saboda haka shi Allah ta'ala ba a saɓa masa ba tare da ganin damarsa ba. Babu abin da ke faruwa sai abin da ya so faruwarSa. Allah ta'ala ya ce:

ﵟوَلَا يَرۡضَىٰ لِعِبَادِهِ ٱلۡكُفۡرَۖﵞ [سورة الزمر:الآية ٧].

Ma'ana: ((Ba kuma Ya yarda da kafirci daga bayinSa)) (Zumar: 7)

Haka nan ya ce:

ا ﴿ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلْفَسَادَ ﴾ [سورة البقرة:الآية ٢٠٥].

Ma'ana: ((Kuma Allah ba Ya son ɓanna)). (Baƙara: 205)

**(11) Abubuwan da suke maganin ƙaddara:**

Allah Maɗaukaki ya sanya wasu abubuwa da suke angije ƙaddara (kafin ta faru) kuma suke gusar da ita (bayan ta afku), kamar addu'a, sadaka, magunguna, taka-tsantsan da kuma ɗaukan ƙwaƙƙwaran mataki; domin dukkaninsu daga hukuncin Allah da ƙaddararSa ne, har ma gazawa da ƙoƙari duka suna cikin ƙaddara.

**(12) Mas'ala: Me ake nufi da cewa: Kaddara sirrin Allah ne a cikin halittunSa?**

Wannan magana tana aiki ne kawai a ɓangaren da aka ɓoye wa bayi daga cikin ɓangarorin ƙaddara; domin haƙiƙanin baɗinin abubuwa babu wanda ya san su sai Allah, ɗan Adam ba shi da damar saninsu, kamar sanin cewa Allah ya ɓatar ko ya shiryar, ko ya kashe ko ya raya, ko ya hana ko ya bayar (kafin faruwar abu). Kamar yadda Annabi (s.a.w) ya ce:

"إذا ذكر القدر فأمسكوا." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Idan aka ambaci ƙaddara to ku kame". Muslim ne ya ruwaito shi.

Amma sauran ɓangarorin ƙaddara da hikimominta masu girma da martabobinta da kuma abubuwan da ke haifuwa daga gare ta, to waɗannan abubuwan duka ya halatta a bayyana su ga mutane kuma ya halatta a san su; domin ƙaddara ɗaya ce daga cikin rukunan imani waɗanda ya kamata a koye su a kuma san su, kamar yadda Manzon Allah (s.a.w) ya faɗa a lokacin da ya ambaci rukunan imani ga Jibrilu (hadda ƙaddara) sai ya ce:

"هذا جبريل أتاكم يعلمكم دينكم" (رواه مسلم).

"Wannan Jibrilu ne ya zo muku domin ya sanar da ku addininku". Muslim ne ya ruwaito shi.

(13) Kafa hujja da ƙaddara:

Kasancewar Allah yana sane da abin da zai kasance tun kafin kasancewar tasa abu ne na gaibu, babu wanda ya san shi sai shi, bayinSa da ya ɗora wa bauta a gare shi ba su san shi ba; saboda haka ba zai zama hujja ba ga wani daga cikinsu, kuma ba ya halatta a bar aiki domin dogaro da abin da ƙaddara ta rigaya ta hukunta. Kaddara ba hujja ba ce da mutum zai kafa wa Allah ko bayinSa, in da ya halatta ga wani ya kafa hujja da ƙaddara kan wani aiki nasa mummuna to da ba za a kama wani azzalumi da laifi ba, kuma da ba za a kashe wani mushiriki ba, da kuma ba a tsaida wani haddi ba, ko a hana wani zaluntar wani ba, wannan kuwa ɓanna ce a addini da kuma duniya wacce kowa ya san cutarwar da za ta yi ba kaɗan ba ce.

Sai mu ce da wanda yake kafa hujja da ƙaddara: Ba ka da wani tabbataccen ilimi kan cewa kai ɗan wuta ne ko ɗan aljanna ne, in da kana da irin wannan ilimin da sai mu ƙyaleka ba cas ba as, (tun da kuwa ba haka ba ne) sai dai mu ce da kai: Ka yi aiki, muna fatan Allah ya datar da kai ka zama cikin 'yan aljanna.

Wani daga cikin sahabbai da ya ji hadisan ƙaddara sai ya ce: "Ban taɓa jin ƙoƙarin ibada ba kamar yanzu". Manzon Allah (s.a.w) kuma da aka tambaye shi game da kafa hujja da ƙaddara, sai ya ce:

"اعملوا فكل ميسر لما خلق له، فمن كان من أهل السعادة فسييسر لعمل أهل السعادة، ومن كان من أهل الشقاوة فسييسر لعمل أهل الشقاوة."

Ma'ana: "Ku yi aiki, kowa za a sauƙaƙe masa (aikin irin gidan) da aka halicce shi dominsa, wanda yake daga cikin

masu rabauta ('yan aljanna) sai a sauƙaƙe masa aikin masu rabauta, wanda kuma yake cikin masu tsiyata ('yan wuta) sai a sauƙaƙa masa aikin matsiyata, sai kuma ya karanta faɗin Allah ta'ala:

﴿ فَأَمَّا مَنْ أَعْطَىٰ وَٱتَّقَىٰ ۝٥ وَصَدَّقَ بِٱلْحُسْنَىٰ ۝٦ فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلْيُسْرَىٰ ۝٧ وَأَمَّا مَنۢ بَخِلَ وَٱسْتَغْنَىٰ ۝٨ وَكَذَّبَ بِٱلْحُسْنَىٰ ۝٩ فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلْعُسْرَىٰ ۝١٠ ﴾ [سورة الليل:الآيات ٥-١٠].

Ma'ana: ((To amma wanda ya yi kyauta ya kuma yi taƙawa. Ya kuma gaskata mafi kyawun kalma (wato: La ilaha illal Lahu), to za mu hore masa (hanya) mai sauƙi. Amma kuma wanda ya yi rowa, ya kuma wadatu (ga barin Allah), kuma ya ƙaryata mafi kyawun kalma, to da sannu za mu hore masa (hanya) mai wahala)). (Al-Laili: 5-10)

**(14) Ɗaukan mataki:**

Abin da ke samun bawa (daga musibu) nau'i biyu ne: akwai abin da zai iya yin wata hikima ya fitar da kansa, to bai kamata ya kasa hakan ba, akwai kuma abin da ba shi da wata damar fitar da kan nasa, to bai kamata ya yi raki ba; domin Matsarkaki kuma Maɗaukakin Sarki ya san da masifun kafin su faru, amma ba ilimanSa ne ya jefa ma'abocin wannan bala'i a cikinsa ba, sai dai ta afku ne a dalilin wasu sababai waɗanda su ne suka kai ga faruwar abun, to idan faruwar masifar a dalilin wani sakaci ne daga mutum ta fuskar barin wasu matakai da wasu hanyoyin da su ne za su iya kare shi daga afkawa cikin wannan masifa, kuma ya zamanto addininsa ya umarce shi da aiwatar da su, to haƙiƙa wannan abun zargi ne saboda wannan sakacin da ya nuna wajen kare kansa da rashin ɗaukan matakan da za su ba shi dama.

Amma idan ba shi da damar yin hakan to haƙiƙa wannan za a yi masa uzuri.

Saboda haka ɗaukar mataki ba wai cin karo yake yi ba da ƙaddara, bai kuma saɓa wa dogaro da Allah ba, sai dai shi ma wani yanki ne daga cikinsu, sai dai idan ƙaddara ta rigaya ta afku to ya wajaba a yarda a kuma miƙa wuya ga yin Allah, a fake da faɗin (kalmar nan da Annabi ya koyar): "Wannan ƙaddara ce daga Allah, abin da ya so kuma shi ne zai faru". Amma kafin abin ya riga ya faru aikin mukallafi shi ne ɗaukar matakan da shari'a ta ba da damar ɗaukansu, da kuma yaƙar ƙaddara da ƙaddara. Za mu ga annabawa - tare da ƙarfafarsu da ake yi da wahayi da kuma kiyayewar Allah- su ma suna ɗaukan mataki da hanyoyin kare kansu daga maƙiyansu. Hatta Manzon Allah (s.a.w) shugaban masu tawakkali yana riƙo da duk wani sababi duk da ƙarfin tawakkalinsa bisa ga Ubangijinsa.

Allah ta'ala ya ce:

﴿وَأَعِدُّوا۟ لَهُم مَّا ٱسْتَطَعْتُم مِّن قُوَّةٍ وَمِن رِّبَاطِ ٱلْخَيْلِ تُرْهِبُونَ بِهِۦ عَدُوَّ ٱللَّهِ وَعَدُوَّكُمْ﴾ [سورة الأنفال:الآية ٦٠].

Ma'ana: ((Ku yi musu tanadi iyakar iyawarku na duka dangogin ƙarfi da tanadaddun dawakai, ku riƙa tsorata maƙiyan Allah kuma maƙiyanku da shi (tanadin) )). (Anfal: 60)

Har ila yau Allah ta'ala ya ce:

﴿هُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ ذَلُولًا فَٱمْشُوا۟ فِى مَنَاكِبِهَا وَكُلُوا۟ مِن رِّزْقِهِۦ ۖ وَإِلَيْهِ ٱلنُّشُورُ ﴿١٥﴾﴾ [سورة الملك:الآية ١٥] .

Ma'ana: ((Shi ne wanda ya sanya ƙasa ta zama horarriya a gare ku, saboda haka ku yi tafiya a cikin sassanta kuma ku ci daga arzikinSa, makoma kuma zuwa gare Shi ne (take

kawai) )). (Mulk: 15)

Manzon Allah (s.a.w) kuma ya ce:

"المؤمن القوي خير وأحب إلى الله من المؤمن الضعيف، وفي كل خير، احرص على ما ينفعك، واستعن بالله ولا تعجز، وإن أصابك شيء فلا تقل: لو أني فعلت كذا لكان كذا وكذا، ولكن قل: قدّر الله ما شاء فعل، فإن لو تفتح عمل الشيطان." [رواه مسلم].

Ma'ana: "Mumini mai ƙarfi ya fi mumini mai rauni alheri da kuma dacewa da soyayyar Allah, ka kiyaye duk wani abin da zai amfane ka, ka kuma nemi taimakon Allah, kada ka gajiya, idan kuma wani abu (na masifa) ya same ka to kada ka ce: "Da na yi kaza da kaza da kaza ya faru", sai dai ka ce: "Wannan ƙaddara ce ta Allah, duk abin da kuma Allah ya so shi zai aikata; domin kalmar: "Lau" (wato: dama) tana buɗe aikin Shaiɗan ne". Muslim ne ya ruwaito shi.

## (15) Hukuncin wanda ya yi inkarin ƙaddara:

Duk wanda ya yi inkarin ƙaddara to ya yi inkarin wani ginshiƙi ne daga ginshiƙan Shari'a, ya kuma kafirta saboda hakan. Wani daga cikin magabata –Allah ya ji ƙansa- ya ce: "In za ku yi jayayya da 'yan ƙadariyya (masu inkarin ƙaddara) to ku tambaye su game da ilimin Allah (shin ya san komai tun kafin faruwarsa?), to idan suka yi inkarin hakan to sun zama kafirai, idan kuma suka tabbatar da ilimin Allah to an ƙure su ke nan".

## (16) Fa'idojin Imani da ƙaddara:

Imani da hukuncin Allah da ƙaddararSa yana haifar da wasu 'ya'yan itatuwa masu daɗi, yana kuma barin wasu gurabu masu kyau, waɗanda su kuma suke haifar da gyaruwar al'umma a dunƙule da ma ɗaiɗaikunta, daga

cikinsu:

1- Yana haifar da (aikata) dangogi daban-daban na nagartattun ibadoji da siffofi ababan yabawa; ikhlasi ga Allah, dogaro da shi, tsoronSa, kwaɗayi da kyakkyawan zato a gare Shi, haƙuri da tsananin juriya, gamawa da halin ɗebe haso, yarda da Allah, kaɗaita Shi da godiya, farin ciki da falalarSa da rahamarSa, ƙanƙantar da kai ga Allah Mabuwayi Maɗaukaki, barin girman kai da alfahari, kamar yadda yake haifar da ciyarwa a ɓangarorin aikin alheri domin amincewa da Allah, jaruntaka da kutsawa, wadatar zuci da ɗaukaka rai ga barin wuraren wulaƙanci, himma tuƙuru, ɗaukan mataki, dagewa a cikin al'amura, saiti a lokacin farin ciki ko masifa, kuɓuta daga hassada da yi wa Allah fito na fito (cikin rabon arziki ga bayinSa), 'yantuwar hankula daga soki burutsu da almara, haka nan yana haifar da kwanciyar hankali da nutsuwar zuciya.

2- Wanda ya yi imani da ƙaddara zai zamanto a cikin dukkanin rayuwarsa yana tafiya a miƙaƙƙiyar turba, in ya samu wata ni'ima ba za ta sa shi wuce wuri ba, haka nan wata masifa ba za ta fitar masa da rai daga cin nasara ba, zai tabbatar da cewa duk wani abin da ya same shi na masifa daga Allah ne, shi ya ƙaddara shi, saboda haka ba raki sai haƙuri da neman ladan Allah.

3- Imani da ƙaddara yana kare mutum daga hanyoyin ɓata da mummunar makoma, domin wannan imanin nasa zai sa shi ya dinga ƙoƙari ko da yaushe don ya ci gaba da tafiya a kan hanya madaidaiciya da kuma yawaita ayyuka na gari, haka nan zai dinga nisantar zunubai ƙanana da kuma masu halakarwa.

4- Imani da ƙaddara zai haifar wa mumini ikon fuskantar duk wata wahala da duk wani firgici da ƙaƙƙarfar zuciya, da cikakken imani tare da ɗaukan mataki.

Manzon Allah (s.a.w) ya ce:

" عجباً لأمر المؤمن إن أمره كله له خير، وليس ذلك إلا للمؤمن، إن أصابته سراء شكر فكان خيراً له، وإن أصابته ضراء صبر فكان خيراً له."

[رواه مسلم].

Ma'ana: "Abin Mamaki ne lamarin mumini! Lamarinsa duka shi alheri ne a gare shi! Babu wanda yake da wannan baiwar sai shi; shi idan abin alheri ya same shi sai ya yi godiya, sai wannan ya zamar masa alheri, idan kuma wata masifa ta same shi, sai ya yi haƙuri, sai hakan ya zamar masa alheri". Muslim ne ya ruwaito shi.

ABUBUWAN DA KE CIKI:


| | |
|---|---|
| GABATARWA | 1 |
| RUKUNAN IMANI | 3 |
| RUKUNI NA ƊAYA: IMANI DA ALLAH | 8 |
| GINSHIKAN TABBATUWAR IMANI | 8 |
| Muhimmancin Tauhidi | 19 |
| Kammaluwar Tauhidi | 19 |
| Ma'anar Ibada | 22 |
| Dalilai da Hujjojin Kaɗaita Allah: | 25 |
| RUKUNI NA BIYU: IMANI DA MALA'IKU | 30 |
| Matsayin Imani da Mala'iku a cikin addini da kuma hukuncinsa | 31 |
| Yadda ake imani da Mala'iku | 31 |
| Imani da mala'iku na dalla-dalla | 33 |
| Adadin Mala'iku | 33 |
| Sunayen Mala'iku | 35 |
| Siffofin Mala'iku | 35 |
| Ayyukan Mala'iku | 37 |
| Haƙƙoƙin Mala'iku a kan 'yan Adam | 39 |
| Fa'idojin imani da Mala'iku: | 39 |
| RUKUNI NA UKU: IMANI DA LITTATTAFAI | 41 |
| Haƙiƙanin imani da littattafan Allah | 41 |
| Buƙatuwar mutane ga saukar da littattafai da bayanin hikimar saukar da su | 42 |
| Yadda imani da Littattafan Allah ya ke | 43 |
| Karɓar labaran tsofaffin littattafan Allah | 45 |
| Littattafan da aka ambata cikin Al-ƙur'ani da Sunnah | 47 |
| RUKUNI NA HUƊU: IMANI DA MANZANNI | 53 |
| Haƙiƙanin Ma'anar Annabta | 53 |
| Hikimar aiko manzanni | 54 |
| Ayyukan Manzannin Allah ya ƙara yi musu sala | 56 |
| Manzanni Mutane ne ba su san gaibu ba | 58 |
| Kare Manzanni (daga zunubai) (Isma) | 59 |
| Adadin annabawa da manzanni da kuma ambaton | |

| | |
|---|---|
| mafificin daraja daga cikinsu | 61 |
| Alamomin annabawa (a.s) (Mu'ujizoji) | 65 |
| Imani da annabtar Annabinmu Muhammad (s.a.w) | 65 |
| RUKUNI NA BIYAR: IMANI DA RANAR LAHIRA | 77 |
| Siffar yadda ake imani da ranar lahira | 81 |
| Fa'idojin Imani da ranar lahira | 100 |
| RUKUNI NA SHIDA: IMANI DA KADDARA | 102 |
| Ma'anar ƙaddara da kuma muhimmancin imani da ita: | 102 |
| Matakan Kaddara | 102 |
| Kashe – kashen tsara ƙaddara | 104 |
| Aƙidar Magabata dangane da ƙaddara | 105 |
| Ayyukan bayi | 107 |
| Ya ya za a siffanta abu ɗaya da cewa: halittar Allah ne kuma aikin bawa ne? | 108 |
| Abin da ya wajaba bawa ya yi dangane da ƙaddara | 109 |
| Yarda da hukunci da ƙaddarar Allah | 110 |
| Abubuwan da suke maganin ƙaddara | 114 |
| Kafa hujja da ƙaddara | 115 |
| Ɗaukan mataki | 116 |
| Hukuncin wanda ya yi inkarin ƙaddara | 118 |
| Fa'idojin Imani da ƙaddara | 118 |